NASSI

DAGA LITTATAFAN

SHUGABA

MAO TSETUNG

TALAKAWAN DUKAN KASASHEN
DUNIYA KU GAMA KAI!

NASSI
DAGA LITTATTAFAN
SHUGABA
MAO TSETUNG

★

MADABA'AR HARSUNAN WAJE
PEKING 1972

Asn Buga a Jamhuriyar Jama'ar Sin.

FIHIRISA

1. Jam'iyyar Kwaminis 1
2. Azuzuwa da Famar Aji 10
3. Gurguzu da Kwaminisanci 26
4. Daidaita Saɓani Sosai tsakanin Jama'a 51
5. Yaƙi da Zaman Lafiya 66
6. Daulantaka da Duk Azzalumai Damisoshin Takarda Ne 82
7. A Iya Fama, A Iya Nasara 93
8. Yaƙin Jama'a 100
9. Rundunar Soja ta Jama'a 114
10. Shugabancin Kwamitocin Jam'iyya 119
11. Hanyar Jama'a 135
12. Aikin Siyasa 153
13. Dangantaka tsakanin Hafsoshi da Sojoji 169
14. Dangantaka tsakanin Rundunar Soja da Jama'a 174

15. Dimakuradiyya a Manyan Fannoni Uku 178
16. Tarbiyya da Horon Sojoji 186
17. Bautawa Jama'a 191
18. Kishin Kasa da Zumuntar Duniya 196
19. Jarumtakar Tawaye 203
20. Mu Gina Kasarmu cikin Kwazo da Tsimi 208
21. Dogara bisa Karfin Kai da Jurewa Madaciyar Fama 216
22. Hanyoyin Tunani da Hanyoyin Aiki 225
23. Bincike da Nazari 254
24. Daidaita Tunanin Kuskure 262
25. Hadin Kai 278
26. Biyayya 281
27. Kushe da Kushewa Kai 285
28. 'Yan Kwaminis 296
29. Ma'aikatan Hukuma 306
30. Samari 320
31. Mata 326
32. Al'ada da Fasaha 331
33. Nazari 337

1. JAM'IYYAR KWAMINIS

Kwayar karfin da ke jan sha'animmu gaba ita ce Jam'iyyar Kwaminis ta Sin.

Tushen tsarin sanin-ka (theory) wanda tunanimmu ke bi shi ne Marksanci-Leninanci (Marxism-Leninism).

> Jawabin Bude Taro a Zama na Farko na Majalisar Wakilan Jama'ar Kasa ta Farko ta Jamhuriyar Jama'ar Sin (15 ga Satumba, 1954).

Idan za a yi tawayen turu, tilas sai da jam'iyyar tawaye. Idan babu jam'iyyar tawayen turu, idan babu jam'iyya wadda aka kafa ta bisa tsarin sanin-ka na tawayen turun Marksanci-Leninanci da kuma cikin

haliyar tawayen turu ta Marksanci-Leninanci, to, lalle kuwa ba zai yiwu ba a shiga jan ragamar ajin ma'aikata da dimbin jama'a zuwa ga cin daulantaka da karnukanta.

"Rundunonin Tawayen Duniya Ku Hada Kai, Ku Yaki Harin Madaulanta!" (Nuwamba 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Idan ba game da kokarin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin ba, kuma ba tare da Sinnawa 'yan Kwaminis wadanda suke ginshikan jama'ar Sin ba, to kuwa, ba zai yiwu Sin ta samu 'yancinta kuma ta sunce kai ba, haka zalika ba mai yiwuwa ba ne Sin ta ce za ta masana'antar da kasa kuma ta maida harkar noma ta hanyar zamani.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945); *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Jam'iyyar Kwaminis ta Sin ita ce kwaya mai ja gora ga jama'ar Sin duka baki daya.

Da a ce ba irin wannan kwaya, da sha'anin gurguzu ba zai iya nasara ba.

Saduwa Da Dukan Wakilan Da Suka Halarci Taron Kasa na Uku na Kungiyar Samari ta Sabuwar Dimakuradiyya ta Sin (25 ga Mayu, 1957).

Jam'iyya kintsattsiya mai damara da tsarin sanin-ka na Marksanci-Leninanci, mai amfani da hanyar kushewa kai kuma mai cudanya da jama'a, da rundunar soja wadda irin wannan Jam'iyya ke yi wa ja gora, kuma da hadaddun goshin fama na dukan azuzuwan tawayen turu da rukunan tawayen turu a karkashin shugabancin irin wannan Jam'iyya—wadannan su ne muhimman makamai guda uku da muka ci makiya da su.

"Kan Mulkin Shibtar Dimakuradiyyar Jama'a" (30 ga Yuni, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ya kamata mu amince wa jama'a, kuma ya kamata mu amince wa Jam'iyya, wadannan su ne muhimman ka'idodi biyu. Idan mun yi shakkar ka'idodin nan biyu, to, ba abin da za mu iya yi.

"Kan Al'amarin Gama Gwiwa wajen Noma" (31 ga Yuli, 1955).

Da yin damara da tsarin sanin-ka da tunani na Marksanci-Leninanci ne, Jam'iyyar Kwaminis ta Sin ta kawo wa jama'ar Sin wata sabuwar haliya ta yin aiki, sabuwar haliya wadda musamman ta kunshe cewa a hada tsarin sanin-ka da aikatawa (practice) wuri guda, kuma da cudanya da jama'a sosai da kushewa kai.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Jam'iyyar siyasa da ke shugabantar babbar harkar tawayen turu, idan ba ta da tsarin sanin-ka na tawayen turu, ba ta da

sanin tarihi kuma ba ta fahimci harkar aikatawa sosai ba, to, ba ya yiwuwa ta ci nasara.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Kamar yadda muka taba fadi cewa, harkar gyara (rectification movement) "harkar tarbiyya ce babba ta Marksanci". Da gyara ana nufin dukan Jam'iyya ce ta koyi Marksanci ta kan suka da kushewa kai. Tabbat ne za mu kara zurfin sanin Marksanci cikin wannan harkar gyara.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

Babbar dawainiya ce a tabbatar da zama mai kyau ga mutanen Sin miliyan darurruka, da kuma gina kasarmu wadda ke baya a arziki da ilmi ta zama kasa mai wa-

data, mai ƙarfi kuma da zurfin ilmi. Kuma domin mu samu mu ɗauki wannan nauyi kuma mu yi aiki sosai ne tare da dukan waɗanda suke ba 'yan Jam'iyya ba ne da suke da nufi mai kyau kuma masu kishin zuci da niyyar gyara, ya zama ɗole mu yi wannan harkar gyara yanzu da kuma gobe, kuma mu ci gaba da cire wa kammu duk abin da ba shi da kyau.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

Tsarin manufar siyasa shi ne mafarin ko wane aiki na jam'iyyar siyasar tawaye, kuma ya kan bayyanu a lokacin aikatawa da kuma ƙarshen aikin jam'iyyar. Ko wane aiki na jam'iyyar siyasar tawaye gudanarwa ne na tsarin manufar siyasarta. Im ba ta gudanar da tsarin manufar siyasar gaskiya, tana gudanar da maras gaskiya, im ba ta gudanar da tsarin manufar siyasa

cikin lamiri, tana yi a makance. Abar da muke kira fasaha, ita ce gudanarwar tsarin manufar siyasa da abin da ya bayyanu a ƙarshenta. Sai tare da aikin jama'a kawai, watau sai cikin fasaha, za mu iya sanin ko tsarin manufar siyasa na da kyau ko babu, kuma mu san iyakacin kyau da rashin kyau. Amma aikin mutane, musamman aikin jam'iyyar tawayen turu da jama'ar tawayen turu, babu wanda bai haɗu da wani tsarin manufar siyasa ba. Sabili da haka, kafin a yi wani aiki, ɗole mu bayyana tsarin manufar siyasa da muka ɗauka bisa halin da muke ciki ga 'yan Jam'iyya da jama'a. Im ba haka ba, 'yan Jam'iyya da jama'a za su goce wa ja gorar tsarin manufar siyasa, su yi aiki a makance kuma su tafiyar da tsarin manufar siyasa maras kyau.

"Kan Tsarin Manufar Siyasa game da Masana'antu da Ciniki" (27 ga Fabrairu, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

Jam'iyyarmu ta tsara babbar hanyar bi da babbar manufar siyasa na tawayen turun kasar Sin har da wadansu hanyoyin aiki musamman da manufofi musamman. Ko da ya ke wani gami, abokai da yawa suna tuna hanyoyin aiki musamman da manufofi musamman na Jam'iyyarmu, su kan manta da babbar hanya da babbar manufa na Jam'iyyarmu. Idan har dai mun manta da su, to, za mu zama makafin 'yan tawaye, guntayen 'yan tawaye masu kai a rude, kuma im mun tafiyar da wata hanyar aiki musamman da wata manufa musamman, ba shakka hanya za ta bace mana, sai ka ga mu rika rausayawa ta hagu, mu rausaya ta dama, kuma aiki zai wahalu.

"Jawabi a Taron Ma'aikatan Hukuma a 'Yantacciyar Jihar Shansi-Suiyuan" (1 ga Afril, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Tsarin manufar siyasa da dabarar tafiyad da abuba su ne rayin Jam'iyya, tilas abokai masu ja gaba na ko wane mataki su maida hankali sosai, kada su yi sake ko da sunan wasa.

"Sanarwa bisa Halin Da Ake ciki" (20 ga Maris, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

2. AZUZUWA DA FAMAR AJI

A famar aji, wasu azuzuwa su yi nasara, wasu ko su hallaka. Wannan shi ne tarihi, watau haka tarihin wayewar kai na shekaru dubbai ya ke. A bayyana tarihi da wannan ra'ayi shi ne materiyalisanci na tarihi, kuma akasin wannan ra'ayi shi ne idiyalisanci na tarihi.

"A Bar Zaton Iska, A Shirya domin Fama" (14 ga Agusta, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

A halin zama na aji, ko wane mutum wakili ne na wani aji musamman, kuma babu tunanin da ba tambarin aji hade da shi.

"Kan Aikatawa" (Yuli 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Sauye-sauye cikin halin zaman al'umma suna aukuwa musamman domin yalwatar saßani cikin gida na zaman al'umma, watau saßani tsakanin ƙarfin ba da albarka da dangantakar kawo albarka, watau saßani tsakanin aji da aji, saßani tsakanin sabo da tsoho, domin ci gaban waɗannan saßani shi ke kai zaman al'umma gaba, kuma shi ke ba sabon zama ƙarfin cin gurbin tsoho.

"Kan Saßani" (Agusta 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Mummunan zalunci wajen arziki da danniyar siyasa na ajin ma'abutan ƙasa (landlord) bisa manoma suka tilasta su rika yin boren ƙin mulkin wannan aji. ... A halin zaman mulkin gargajiya (feudal society) a ƙasar Sin, famar aji ta manoma, da boren manoma da yake-yaken manoma su ne kawai suka zama ƙarfin gaske wajen yalwatar tarihi.

"Tawayen Sin da Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (Disamba 1939), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

A karshen magana, famar al'umma fama ce ta aji. A kasar Amirka, wadanda ke danne bakar fata su ne da'irorin mahukunta azzalumai na farar fata kawai. Su kuwa ko kusa ba su da hujjar wakiltar ma'aikata, manoma, 'yan ilmi na tawayen turu da sauran wayayyun mutane wadanda su ne suka fi yawa a cikin farar fata.

> "Sanarwar Goyon Bayan Bakaken Fata na Amirka a Gaskantacciyar Famarsu ta Kin Nuna Bambancin Kabila Da Daulantakar Amirka Ke Yi" (8 ga Agusta, 1963).

Aikimmu ne mu shirya jama'a. Ga azzaluman Sin, aikimmu ne mu shirya jama'a domin mu nakasa su. Kome na zalunci daya ne, im ba a zungure shi ba, ba ya faduwa. Kamar dai sharan dabe,

duk inda tsintsiya ba ta kai ba, dauda ba ta kaura da kanta.

> "Halin Da Ake ciki da Manufar Siyasarmu bayan Nasara a Yakin Kare Harin Japan" (13 ga Agusta, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Makiyi ba zai hallaka kansa ba. Ko azzalumai Sinnawa ko rundunonin hari na madaulanta Amirkawa a kasar Sin, da kansu ba za su janye jikinsu daga fagen tarihi ba.

> "A Ci Gaba da Tawaye har Karshe" (30 ga Disamba, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Tawayen turu ba liyafa ba ne, ba rubutun labari ko zanen hoto ko yi wa tufafi ado ba ne, kuma ba abin kwalisa ba ne, ko fadanci, ko kyaliya, ko karimtaka. Tawayen turu bore ne, aikin karfi da yaji ne da wani

aji ke amfani da shi wajen hamßurad da wani aji.

"Rahoto kan Binciken Harkar Manoma a Lardin Hunan" (Maris 1927), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Chiang Kai-shek kullum yana ƙwace ko wace ƙwayar mulki da ko wace ƙwayar amfani daga jama'a. To, mu fa? Manufar siyasarmu ita ce mu rama gayya, mu yi fada domin ko wane inci na ƙasa. Muna aiki bisa misalinsa. Kullum yana ƙoƙarin aza yaƙi kan jama'a, hannunsa na hagu da takobi, na dama ma da takobi. Mu ma sai mu ɗauki takobi bisa misalinsa. ... A yanzu Chiang Kai-shek yana wasa takubbansa, mu ma sai mu wasa namu.

"Halin Da Ake ciki da Manufar Siyasarmu bayan Nasara a Yaƙin Kare Harin Japan" (13 ga Agusta, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Su wane ne maƙiyammu? Su wane ne aminammu? Wannan ita ce muhimmiyar tambaya ta farko ga tawayen turu. Tahaƙikin dalilin da ya sa duk tawaye-tawayen Sin na da ba su samu nasara sosai ba shi ne don rashin haɗa kai da aminai na gaske a far wa maƙiya na gaske. Jam'iyyar tawayen turu ita ce ja gora ta jama'a, kuma ba tawayen turu da ya taßa nasara in jam'iyyar tawayen turu ta ßad da jama'a. Domin mu tabbata lalle ne za mu sami nasara a tawayen turummu kuma ba za mu ßad da jama'a ba, dole ne mu mai da hankali kan haɗa kai da aminammu na gaske domin mu far wa maƙiyammu na gaske. Domin mu bambanta aminammu na gaske da maƙiyammu na gaske, dole mu shiga babbar ƙiddigar matsayin arziki na ko wane aji a halin zaman al'ummar Sin da kuma irin taketakensu ga tawayen turu.

"Binciken Azuzuwa a Zaman Al'ummar Sin" (Maris 1926), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Duk azzalumai jarababbun yaƙi (warlords), manyan munafukai hakimai (bureaucrats), ajin munafukai masu tsare mutuncin arzikin bakin dole (comprador class), da ajin manyan ma'abutan ƙasa waɗanda ke ƙawance da daulantaka, kai har da sashen tsirarrun 'yan ilmi azzalumai da ke haɗe da su, dukansu makiyammu ne. Ajin talakawan masana'antu shi ne ƙarfi na shugabantar tawayen turummu. Aminai mafiya kusa da mu su ne duk makamantan talakawa da kuma 'yan ƙananan tajirai. Cikin madaidaitan tajirai masu shakka, mai yiwuwa ne 'yan damarsu su zama makiyammu kuma 'yan hagunsu su zama aminammu—amma ko wane lokaci ya kamata mu sa hankali bisansu don kar mu bari su shuka rikici a tsakanimmu.

"Binciken Azuzuwa a Zaman Al'ummar Sin" (Maris 1926), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Ko wane ne yake tare da jama'a 'yan tawayen turu, shi ma ɗan tawaye ne. Ko wane ne yake tare da daulantaka, mulkin gargajiya da manyan tajirai-hakimai, shi makiyin tawaye ne. Ko wane ne yake tare da jama'a 'yan tawaye a baka kawai, amma yana aikata wani abu dabam, shi ma ɗan tawaye ne kawai a baka. Kuma ko wane ne yake tare da jama'a 'yan tawaye a baka da kuma a aikace, shi ɗan tawaye ne na gaske.

Jawabin Rufe Taro a Zama na Biyu na Kwamitin Kasa na Farko na Taron Shawarar Siyasar Jama'ar Sin (23 ga Yuni, 1950).

Na gani bai kyautatu a gare mu ba a ce makiyi bai zargi mutum, ko jam'iyya, ko rundunar soja ko makaranta ba, domin haka tabbat zai nuna mun tashi daidai da makiyi. Abu ne mai kyau im makiyi ya zarge mu, domin haka zai tabbatar, mun zana iyaka tsakanimmu da makiyi. Zai

ma fi kyau im maƙiyi ya zarge mu sosai, kuma ya shafa mana kashin kaji, ya ce ba mu da kirki ko kaɗan, domin haka zai nuna ba iyaka kaɗai muka zana tsakanimmu da maƙiyi ba har ma mun sami babbar nasara a aikimmu.

"Abu Mai Kyau Ne Ba Mugu Ba Ne ga Maƙiyi Ya Zarge Ka" (26 ga Mayu, 1939).

Duk abin da maƙiya ke ƙi, ya kamata mu goyi bayansa, duk abin da maƙiya ke goyon bayansa, mu ƙi shi.

"Hira da 'yan Jaridu Uku na Kamfanin Watsa Labarai na Tsakiya, *Sao Tang Pao* da *Hsin Min Pao*" (16 ga Satumba, 1939), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Mun tsaya a matsayin ajin talakawa da jama'a. Ga 'yan Jam'iyyar Kwaminis, wannan yana nufin tsayewa Jam'iyya,

tsayewa halin Jam'iyya da tsarin manufar siyasar Jam'iyya.

"Jawabi a Taron Yenan kan Wallafa da Fasaha" (Mayu 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Bayan an hallaka maƙiya masu bindiga, da akwai sauran maƙiya marasa bindiga, lalle ne za su shiga famar ko rai ko mutuwa da mu, ko kusa kada mu ƙankanta waɗannan maƙiya. Idan yanzu ba mu gabatar da batun nan ba kuma ba mu fahimci wannan batu haka nan ba, za mu aikata manyamanyan kuskure.

"Rahoto ga Cikakken Zama na Biyu na Taro na Bakwai na Kwamitin Tsakiya na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (5 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Madaulanta da azzalumai na gida ko kusa ba za su haƙura da hasararsu ba, za su dinga shure-shuren mutuwarsu. Bayan

an kafa zaman lafiya a duk ƙasa, mai yiwuwa ne har ila yau su ci gaba da shuka ɓarna da ta da tarzoma ta ko wace hanya, kuma a ko wace rana a ko wane sa'i za su bidi sake rayad da mulkinsu a ƙasar Sin. Tabbat ne kuma babu wata shakka game da wannan, ko kusa bai kamata ba mu dan saki ragamar hankalimmu.

Jawabin Budɛ Taro a Cikakken Zama na Farko na Taron Shawarar Siyasar Jama'ar Sin (21 ga Satumba, 1949).

An kusa ida gurguzantad da tsarin mallakar dukiya a ƙasar Sin, babbar bugayya ta azuzuwa da jama'a suka yi ta yi a lokacin tawayen turu, yanzu dai kusan ba ta kuma, amma duk da haka akwai sauran ƙurar hamɓurarrun azuzuwan ma'abutan ƙasa da na munafukai masu tsare mutumcin bakin dole, kuma har yanzu da akwai ajin tajirai, 'yan ƙananan tajirai ma sai yanzu aka fara sauya ra'ayinsu. Har yanzu ba

a ƙare famar aji ba tukuna. Famar aji tsakanin talakawa da attajirai, tsakanin rukunonin siyasa dabam daban, kuma da ta tsakanin ajin talakawa da na attajirai a fagen hankali da tunani har kullum fama ce ta dogon lokaci, tana da kalwaɗe-kalwaɗe, wani lokaci ma ta kan tsananta ƙwarai da gaske. Talakawa nema su ke su sauya duniya bisa ra'ayinsu, haka zalika tajirai ma. Game da wannan, al'amari na tsakanin gurguzu da tajirtaka (capitalism) wa zai ci nasara wa zai faɗi, wannan al'amari har yanzu ba a daidaita shi ba sosai.

"Game da Hanyar Daidaita Sa-ɓani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Zai bukaci lokaci mai tsawo kafin a daidaita maganar famar tunani tsakanin gurguzu da tajirtaka a ƙasarmu. Dalili shi ne tasirin ajin tajirai da 'yan ilmi waɗanda suka taso daga tsohon zaman al'umma zai jima a ƙasarmu, haka kuma irin tunanin

ajinsu. Im ba a fahimci wannan sosai ko kuma ba a fahimta ba sam, lalle za a yi manyan kuskure, kuma za a kasa kula da amfanin yin fama wadda ta wajaba ta fagen tunani.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

A kasarmu, tunanin attajirai da kananan attajirai da tunanin kin Marksanci za su jima. An dai kafa tushen tsarin mulkin gurguzu a kasarmu. Mun ci nasara wajen canjin tsarin mallakar hanyoyin kawo albarka, amma har yanzu ba mu ci nasara sosai ba a fannin siyasa da tunani. A fagen tunani, maganar wa zai ci a fama tsakanin talakawa da tajirai ba a daidaita sosai ba tukuna. Har yanzu dole mu ci gaba da doguwar fama bisa tunanin attajirai da kananan attajirai. Kuskure ne rashin fahimtar haka, kuma a bar famar tunani. Dukan mummunan tunani, dukan haki mai guba da dukan

miyagun shaidanu dole ne a kushe musu, ko da sunan wasa kada a bari su yadu. Amma irin sukar da za a yi musu sai ta zamana mai cikakken dalili, mai kididdiga, mai jawo hankali, kada ta zama ta halin keta da nuna halin hakimci ko metafisik ko dogamatisanci.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

Da dogamatisanci da munafuntar Marksanci-Leninanci (revisionism) dukansu biyu adawa su ke da Marksanci. Dole ne Marksanci ya ci gaba, dole ya yalwata tare da ci gaban aikatawa, ba zai tsaya haka nan ba. Zai tsumbure in ya kafe wuri guda. Amma duk da haka, tushen ka'idodin Marksanci ba za a take su ba, in an taka za a yi kuskure. Haka dogamatisanci ne a warware Marksanci ta ra'ayin ·metafisik kuma a dauke shi kamar abu ne mai tsanani da tauri. Yi wa tushen ka'idodin Marksanci

da gaskiyarsa ta kullum musu, wannan shi ne munafuntar Marksanci. Munafuntar Marksanci tunani ne na attajirai. Masu munafuntar Marksanci sun ki yarda da bambanci tsakanin gurguzu da tajirci da bambanci tsakanin mulkin shibta na talakawa da na tajirai. Abin da su ke gabatarwa a hakika ba hanyar gurguzu ba ce, hanyar tajirci ce. A halin yanzu, munafuntar Marksanci ta fi dogamatisanci muni. Daya daga cikin muhimman ayyukammu yanzu a fannin tunani shi ne a ci gaba da sukar munafuntar Marksanci.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

Munafuntar Marksanci ko zarafintaka ta Dama (Right opportunism) gudanar tunani ce ta attajirai (bourgeois trend), kuma ta fi dogamatisanci kawo kasada. Masu munafuntar Marksanci da 'yan zarafintakar Dama su ma sun dau Marksanci a baka, su ma wai suna la'antar "dogamatisanci." Amma abin da su ke zargi sosai shi ne ainihin gaskiyar Marksanci. Suna ki kuma suna jirkitar da materiyalisanci da diyalektik, suna ki ko suna nema su rage karfin mulkin shibta na dimakuradiyyar jama'a da kuma hidimar shugabanci na Jam'iyyar Kwaminis, haka zalika suna ki ko suna raunana aikin rikidarwa da ginegine na gurguzu. Bayan samun nasarar farko a tawayen gurguzu a kasarmu, har ila yau da akwai wadanda ke mafarkin banza na neman sake rayad da tsarin zaman tajirci, kuma suna da niyyar fama da ajin ma'aikata a dukan fannoni har ta fuskar tunani. Kuma mutanen hannun damarsu a wannan fama su ne 'yam munafuntar Marksanci.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

3. GURGUZU DA KWAMINISANCI

Kwaminisanci wani cikakken tsarin tunani ne na ajin talakawa, kuma sabon tsarin halin zama ne. Ya bambanta da duk wani tsarin tunani kuma da duk wani tsarin halin zama, shi ne mafi cika, mafi ci gaba, mafi nuna tawayen turu, mafi ma'ana a tarihin dan Adam. Tsarin tunani da tsarin halin zama na mulkin gargajiya, yanzu dai an tura su gidan nunin tarihi. Haka tsarin tunani da tsarin halin zama na jarinci sun zama abubuwan gidan nunin tarihi a wani gefen duniya (watau a Rasha), kuma a sauran kasashe, sun yi kama da "mutumin da ke bakin mutuwa, kamar rana ta zo faduwa", su ma dai ba da jimawa ba za su shiga gidan

nunin tarihi. Sai dai tsarin tunani da tsarin halin zama na kwaminisanci ne kawai ke da kuruciya na share duniya da karfin aradu da kuma irin karfi mai kau da tuddai za su tofu kamar lingaɓun jan yaro a duk duniya.

"Kan Sabuwar Dimakuradiyya" (Janairu 1940), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Biyu.

A karshe dai tsarin gurguzu zai karɓi gurbin tsarin jarinci, wannan halitacciyar doka ce wadda za ta auku ba sai tare da yardar dan Adam ba. Kome kokarin da azzalumai ke yi wajen tsai da ci gaban tarihi, zai zama na banza domin kul ba dade kul ba jima tawayen turu zai auku kuma tilas ya yi nasara.

"Jawabi a Majalisar Rasha don Bikin Cikon Shekaru 40 da Babban Tawayen Gurguzu na Oktoba" (6 ga Nuwamba, 1957).

Mu 'yan Kwaminis har abada ba mu ɓoye manufar siyasarmu. Ba shakka balle musu cewa, babban shirimmu na gobe ko babbar manufarmu ta ƙoli ne kai Sin zuwa ga zaman gurguzu da zaman kwaminisanci. Sunan Jam'iyyarmu da ra'ayimmu na Marksanci game da duniya suna bayyana wannan kishin zuci mai haske a fili da za mu tabbatar gobe.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Duk ɗawainiyar tawayen turun Sin wadda Jam'iyyar Kwaminis ta Sin ke shugabanta, ana iya kasa ta gida biyu, watau mataki na tawayen dimaƙuraɗiyya da na tawayen gurguzu, waɗanda su ke matakai ne dabam a halin tawaye, kuma na biyu ba ya samuwa sai bayan an ida na farko. Tawayen dimaƙuraɗiyya shi ne bukatacce shiri zuwa ga tawayen gurguzu, kuma shi tawayen gurguzu abu ne da ɗole ya

bayyana bayan tawayen dimaƙuraɗiyya. Burin ƙarshe ga ko wane ɗan kwaminis shi ne ya ƙoƙarta domin kawo zaman gurguzu da na kwaminisanci.

"Tawayen Sin da Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (Disamba 1939), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Burin tawayen gurguzu shi ne suntad da ƙarfin ba da albarka. Sauyin mallakar dukiya daga hannun mutum ɗaya zuwa ga na tarayyar gurguzu wajen noma da sana'ar hannu, kuma daga mallakar jarinci zuwa ga mallakar gurguzu wajen mahasusin masana'antu da ciniki, lalle zai kawo 'yanci sosai ga ƙarfin ba da albarka. Kuma ta haka, za a kawo halayen zaman al'umma da za su daɗa yalwata albarkar sana'a da noma.

Jawabi a Taron Koli game da Harkokin Kasa (25 ga Janairu, 1956).

Yanzu muna tawaye ba wai kawai na sauyin tsarin halin zama ba, watau sauyi daga mallakar dukiya a hannun mutum ɗaya zuwa ga hannun al'umma duka, amma har da tawaye a fasahar sana'a watau sauyi daga aikin kawo albarka da hannu zuwa ga aikin kawo albarka da manyan na'urori na zamani, kuma wadannan tawaye biyu a hade suke. A sha'anin noma, bisa yadda hali ya ke a ƙasarmu sai an fara ɗa gama gwiwa kafin a shiga amfani da manyan na'urori (a ƙasashen jarinci ana ci gaba da noma bisa hanyar jarinci). Sabo da haka ko da sunan wasa kada mu ɗauki sana'a da noma, gurguzantar da sana'a da noma kamar abubuwa biyu ne a ware, kuma bai kamata a darajantad da ɗaya a bar ɗaya ba.

"Kan Al'amarin Gama Gwiwa wajen Noma" (31 ga Yuli, 1955).

Sabon tsarin zaman nan da aka kafa ba da ɗadewa ba, zai bukaci lokaci kafin a

zaunad da shi sosai. Kada a yi zato cewa ko da kafa shi zai zama abu mai ƙwari, haka ba ya yiwuwa. Sai da kaɗan kaɗan zai ƙarfafa. Domin a zaunad da shi sosai, ba tilas ne kawai a gurguzantad da sana'ar ƙasa, a nace da ci gaba da tawayen gurguzu wajen tattalin arziki ba, kuma dole ne a ci gaba da jar fama ta tawayen gurguzu da tarbiyyar gurguzu a fannin siyasa da tunani. Kuma bayan haka, ana bukatar sharuɗa iri iri cikin duniya su taimaka.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

A ƙasarmu, famar zaunad da tsarin gurguzu, fama mai nuna ko gurguzu ko jarinci ne zai yi nasara, za ta ɗauki wani dogon lokaci na tarihi. Amma ya kamata mu fahimci cewa wannan sabon tsarin gurguzu zai zaunu ba tare da shakka ba. Tabbat

ne za mu iya kafa kasar gurguzu mai sana'a, mai noma, mai kimiyya da ilmi iri na zamani.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

'Yan ilmi wadanda suke gaba da kasarmu ba su da yawa ko kadan. Wadannan mutane ba su kaunar kasarmu mai mulkin shibta na talakawa, suna begen tsohon halin zama. Da sun samu dan zarafi, sai su ta da fitinar neman hamburad da Jam'iyyar Kwaminis domin sake kafa tsohuwar Sin. Tsakanin hanyar ajin talakawa da ta ajin attajirai, tsakanin hanyar gurguzu da ta jarinci, wadannan mutane suna nuna taurin kai ga bin hanya ta biyu. A gaskiya dai wannan hanya ba ta biyuwa, sabo da haka a shirye suke wajen ba da kansu ga daulantaka, mulkin gargajiya da mulkin tajirai-hakimai. Irin wadannan mutane ana iya tsintarsu a da'irorin siyasa, masana'antu da ciniki, kungiyoyin al'ada da ilmi,

haka zalika ana ganinsu a da'irorin kimiyya da fasahar sana'a da addini, kuma mutanen nan azzalumai ne na gaske.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

Muhimmin al'amari shi ne tarbiyyar manoma. Tattalin arzikin manoma a barbaje yake, kuma bisa fasahar Rasha, abin zai bukaci lokaci mai tsawo kuma da aiki mai wahala kafin mu ce za mu mai da noma bisa hanyar gurguzu. Idan ba a gurguzantad da noma ba, to kuwa, ba za a iya kafa cikakken gurguzu mai kwari ba.

"Kan Mulkin Shibtar Dimakuradiyyar Jama'a" (30 ga Yuni, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ya kamata mu yi imani cewa, na farko, dimbin manoma na son da kadan kadan a karkashin shugabancin Jam'iyya su bi

hanyar gurguzu, na biyu, shi ne lalle Jam'iyya tana iya shugabantar manoma bisa wannan hanyar gurguzu. Wadannan abubuwa biyu su ne tushen al'amarin kuma suna nuna babban abin da ake nufi.

"Kan Al'amarin Gama Gwiwa wajen Noma" (31 ga Yuli, 1955).

Ya kamata ofisoshin dà ke shugabantar kungiyoyin gama gwiwar noma su kafa tsayayyen iko na matalautan manoman da ke akwai yanzu da sababbin madaidaitan manoma masu karamin karfi a cikin ofisoshin shugabanci, karfi wanda zai taimaka musu shi ne karfin tsofaffin madaidaitan manoma masu karamin karfi da tsofaffi ko sababbin madaidaitan manoma masu tsayayyen karfi. To, ta haka kawai ne za a iya bin tsarin manufar Jam'iyya domin tabbata hadin kai tsakanin matalautan manoma da madaidaitan manoma, a karfafa kungiyoyin gama gwiwar noma, a yalwata

kawo albarka, kuma a yadda ya kamata a ida rikidad da duk kauyuka bisa hanyar gurguzu. Idan ba haka ba, hadin kai tsakanin madaidaitan manoma da matalautan manoma, karfafa kungiyoyin gama gwiwar noma, yalwatad da kawo albarka da rikidad da kauyuka baki daya bisa hanyar gurguzu ba za su yiwu ba.

Gabatarwa ga "Yadda Iko na Kungiyar Hadin Kan Manoma na Wutang, Garin Kaoshan a Gundumar Changsha, Ya Koma Hannun Matalautan Manoma daga Hannun Madaidaitan Manoma" (1955).

Dole ne a hada kai da madaidaitan manoma, idan ba a yi haka ba zai zama kuskure. Amma a cikin kauyuka, bisa wa ajin ma'aikata da Jam'iyyar Kwaminis ya kamata su dogara domin su hadu da madaidaitan manoma su rikidad da kauyuka baki daya ta hanyar gurguzu? Lalle sai bisa matalautan manoma kawai. Haka ma a da lokacin da muke famar kin ma'abutan kasa, kuma

da tafiyar da aikin raba gonaki (land reform), yanzu ma haka ne wajen famarmu bisa mawadatan manoma da sauran abubuwan jarinci, domin rikidad da noma ta hanyar gurguzu. A lokatan nan biyu na tawayen turu, da farko su madaidaitan manoma sun nuna shakka. Amma sai kawai yayin da suka gane babban nufin matsala da kuma gabatowar nasara a fili sai suka kawo jiki ga tawayen turu. Ya kamata matalautan manoma su yi aikin shawo kan madaidaitan manoma, su ja su a jiki domin tawayen turu a kwana a tashi ya kara girma har nasarar karshe.

Gabatarwa ga "Darasunan Da Aka Samu daga Bullowar 'Kungiyar Madaidaitan Manoma' da 'Kungiyar Matalautan Manoma' a Gundumar Fuan" (1955).

Akwai babban nufi na nuna son jarinci mai tsanani a tsakanin kosassun manoma. Idan mun ce za mu yi dan sake cikin aikin

siyasarmu game da manoma a cikin harkar gama gwiwa da kuma cikin dogon zamani na gaba, wannan nufi zai yadu.

Gabatarwa ga "Dole Ne A Dage ga Famar Kin Halin Nuna Son Jarinci" (1955).

Harkar gama gwiwa a sha'anin noma fama ce ta siyasa da ta tunani mai tsanani tun farko. Babu kungiyar gama gwiwa da za a kafa ba tare da irin wannan fama ba. Kafin a kafa sabon tsarin zama a gurbin tsoho, dole ne sai an share tsohon. Kullum a zukatan mutane da ringin tsohon tunani mai nuna tsohon tsari, kuma ba a iya kau da shi da sauki. Bayan an kafa kungiyar gama gwiwa, dole ta yi wasu fama da yawa kana ta karfafu. Ko da haka ma, in ta rage kokarinta, mai yiwuwa ne ta rushe.

Gabatarwa ga "Darasi Mai Tsanani" (1955).

A 'yan shekarun nan da suka shige, nufin nuna son jarinci sai yaduwa yake ko wace rana a kauyuka, kuma a ko ina sai ganin sababbin mawadatan manoma ake, da yawa daga cikin kosassun madaidaitan manoma sai kokarin zama mawadatan manoma suke. Dimbin matalautan manoma domin ba su da isassun hanyoyin ba da albarka, har yanzu suna cikin talauci, wadansu sun shiga bashi, wadansu sun sai da gandu, ko sun ba da sufurinsa. Idan an kyale al'amarin nan ya yadu, halin bambanci tsakanin talauci da wadata ba makawa zai ci gaba da lalacewa a kauyuka. Manoman da suka yi asarar gandunansu da wadanda har yanzu suke cikin talauci za su yi ta yi mana gunaguni cewa ba mu cece su daga bakin mutuwa ba, kuma ba mu taimake su wajen haye wahalolinsu ba. Kosassun madaidaitan manoma masu nufin bin hanyar jarinci su ma za su yi fushi da mu, lalle har abada ba za mu iya shafe hawayensu ba sai dai im muna da burin bin

hanyar jarinci. A cikin irin wannan hali, ana kuwa iya karfafa kawance tsakanin ma'aikata da manoma? Abu ne a fili cewa ba ya yiwuwa. Wannan matsala sai da wani sabon digi za a iya daidaita ta. Watau da kadan kadan a gurguzantad da sana'o'i da kuma a rikidad da sana'ar hannu bisa hanyar gurguzu, haka zalika da sana'o'i da ciniki iri na jarinci har ila yau kuma da kadan kadan a tabbatad da rikidar noma ta bi hanyar gurguzu, watau gama gwiwar manoma, a soke tsarin tattalin arziki na mawadatan manoma da kuma tsarin tattalin arziki na mallakar mutum daya a kauyuka domin wannan zai sa mutanen kauyuka su wadata gaba daya. A ganimmu fa, ta haka ne kawai kawancen ma'aikata da manoma zai iya karfafa.

"Kan Al'amarin Gama Gwiwa wajen Noma" (31 ga Yuli, 1955).

Wajen yin babban shiri, muna nufin shirin da zai ɗauki ɗukan bukatun mutanen ƙasarmu miliyan 600. Im mun zo yin wani shiri ko daidaita wani sha'ani ko yin tunani bisa wani al'amari, dole ne mu fara da cewa Sin tana da jimlar mutane miliyan 600, ko kaɗan kada mu manta da wannan.

"Game da Hanyar Daidaita Sa6ani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Ban da shugabanci na Jam'iyya, wata muhimmiyar aba ita ce jimlar mutanemmu miliyan 600. Yawan mutane na nufin yawan ɗabaru da sha'awa da himma. Ba a taɓa ganin mutane sun tashi da himma da ƙwazo da fara'a irin yanzu ba.

"Gabatar Da Wata Kungiyar Haɗin Kan Manoma" (15 ga Afril, 1958).

Ban da sauran halaye, wani abu mai tsone ido game da mutanen Sin miliyan 600 shi ne talauci da rashi. A sama sama wannan ba abu ba ne mai kyau, amma cikin halin gaskiya abu ne mai kyau. Talauci na kawo son a yi sauyi, son aiki da son tawaye. A kan warkar farar takarda da ba ko zane a kai, za a iya sabon rubutu mafi kyau kuma za a iya zana sabon hoto mafi kyau.

"Gabatar Da Wata Kungiyar Haɗin Kan Manoma" (15 ga Afril, 1958).

Bayan nasarar tawayen turun Sin a duk ƙasa baki ɗaya da kuma warware matsalar ganduna, da akwai sa6ani iri biyu masu digi a Sin. Na farko na cikin gida ne, watau sa6ani tsakanin ajin ma'aikata da na tajirai. Na biyu na waje ne, watau sa6ani tsakanin Sin da ƙasashen daulantaka. Sabo da haka, bayan nasarar tawayen dimaƙuraɗiyya ta jama'a, ikon mulkin ƙasar jamhuriyar jama'a a ƙarƙashin shugabancin

ajin ma'aikata, ba za a rage masa ƙarfi ba sai dai a ƙara ƙarfafa shi.

> "Rahoto ga Cikakken Zama na Biyu na Taro na Bakwai na Kwamitin Tsakiya na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (5 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

"Ba ku son wargaza ikon mulkin ƙasa ne?" I, muna so, amma ba yanzu ba, yanzu dai ba za mu iya yinsa ba. Don me? Domin da akwai daulantaka har yanzu, da akwai azzalumai kuma da akwai azuzuwa har yanzu a ƙasarmu. Aikimmu yanzu shi ne mu ƙarfafa makaman mulkin ƙasa na jama'a, watau musamman ma rundunar sojojin jama'a, 'yan sandan jama'a da kotun jama'a, domin mu ƙarfafa tsaron ƙasa kuma mu kiyaye bukatun jama'a.

> "Kan Mulkin Shibtar Dimakuradiyyar Jama'a" (30 ga Yuni, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ƙasarmu ƙasa ce mai mulkin shibta na dimakuradiyyar jama'a wadda ajin ma'aikata ke ja wa ragama, kuma an kafa ta bisa ƙawancen ma'aikata da manoma. Wadanne ne ayyukan shi wannan mulkin shibta? Aikinsa na farko shi ne danne ajin azzalumai da daularsu har da mazambata masu ƙin tawayen gurguzu na gida, da wadanda suke yi wa gine-ginen gurguzu ɓarna, watau shi ne domin daidaita saɓani tsakanimmu da makiyammu na gida. Ga misalai, a kama wasu 'yan ƙin tawaye a yi musu hukunci kuma a haramta wa ma'abutan ƙasa da tajirai-hakimai hujjar ƙuri'a da ta 'yancin yin magana har na wani lokaci, duk wadannan abubuwa na cikin iznuwar mulkin shibta. Domin a kiyaye dokar zaman al'umma kuma a tsare abin moriya na dimbin jama'a, tilas ne a nuna ikon mulkin shibta ga ɓarayi, maciya amana, 'yan kisan kai, masu ta da gobara, ayarin shakiyai da sauran mutane marasa halin kirki masu kawo babbar

fitina ga jama'a. Aiki na biyu na mulkin shibta shi ne tsare ƙasa daga maƙarƙashiya da hari waɗanda maƙiya za su iya kawo mana daga waje. A wannan hali, ya kamata mulkin shibta ya ɗauki aikin ɗaidaita saɓani tsakanimmu da maƙiyammu na waje. Burin mulkin shibta shi ne kare jama'a don su yi aiki cikin lafiya, su gina ƙasar Sin ta zama ƙasar gurguzu mai sana'a, noma, kimiyya da al'ada na zamani.

"Game da Hanyar Daidaita Saɓani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Mulkin shibta na dimaƙuraɗiyyar jama'a yana bukatar shugabancin ajin ma'aikata. Domin wannan aji shi ne aji mafi la'akari, maras son kai, ga shi kuma mafi halin tawaye. Dukan tarihin tawaye ya yi shaidar cewa idan ba tare da shugabancin ajin ma'aikata ba, to, tawayen turu ya kan yi

asara, amma ya kan yi nasara tare da shugabancin ajin ma'aikata.

"Kan Mulkin Shibtar Dimaƙuraɗiyyar Jama'a" (30 ga Yuni, 1949), *Zaɓaɓɓun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

Bisa ƙawancen ajin ma'aikata da manoma da kuma 'yan ƙananan tajiran maraya, kai musamman bisa ƙawancen ma'aikata da manoma ne, mulkin shibta na dimaƙuraɗiyyar jama'a ya dogara, domin kuwa su azuzuwan nan biyu suna wakiltar kashi 80 zuwa 90 na jimlar jama'ar Sin baki ɗaya. Azuzuwan nan biyu su ne muhimmin ƙarfi wajen hamɓurad da daulantaka da daular azzaluman Kuomintang. Haka kuma ƙaura daga lokacin Sabuwar Dimaƙuraɗiyya zuwa zaman gurguzu musamman ya danganta ga ƙawance tsakanin azuzuwan nan biyu.

"Kan Mulkin Shibtar Dimaƙuraɗiyyar Jama'a" (30 ga Yuni, 1949), *Zaɓaɓɓun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

Famar aji, famar kawo albarka da gwajin kimiyya, su ne manyan harkoki uku na tawayen turu don gina kasa mai karfi ta gurguzu. Wadannan harkoki su ne ginshikan da za su sa duk dan Kwaminis ya kiyaye ra'ayin nuna hakimci kuma ya guji munafuntar Marksanci-Leninanci da dogamatisanci, kuma har kullum ya zaune ya zamana gagararre ne. Haka zalika su ne ginshikan da za su sa hadin kai tsakanin talakawa da dimbin ma'aikata domin su tabbatar da mulkin shibtar dimakuradiyya. Im ba haka ba, aka bar ma'abutan kasa, mawadatan manoma, makiyan tawaye, lalatattun mutane da shaidanu suka fito gaba daya kuma ma'aikatan hukumarmu (cadres) suna gani suna kyalewa, kai har wadansu a cikinsu ma suka rasa bambanta tsakanimmu da makiyammu, har ma suna gama baki da makiya, suna bari ana ci musu hanci, ana lalata su, ana shiga tsakaninsu domin a raba su, idan ta haka har makiya suka samu suka rinjayi ma'aikatan hukumarmu, suka janye su daga jama'a ko kuwa su makiya su sami kutsa kai tsakanimmu, kuma idan dimbin ma'aikatammu da manomammu da 'yan ilmimmu sun bari makiya suka shammace su, ko suka firgita su, to kuwa, bayan dan lokaci, watakila bayan 'yan shekaru kadan ko fiye da goma kai in an dade dai shi ne 'yan shekaru gommai, ba shakka sai a ga an sake kafa mulkin kiye wa tawaye a duk mafaliyar kasa, sai kuma jam'iyya wadda ta ke ta Marksanci-Leninanci ce, take sai ta zama jam'iyyar munafuntar Marksanci-Leninanci ta zama jam'iyyar fasis, kuma sai duk kasar Sin ta sake launinta.

Daga "Kan Kwaminisancin Karya na Khrushchov da Darasunan Tarihi Da Ya Ba Duniya" (14 ga Yuli, 1964).

Mulkin shibtar dimakuradiyya ta jama'a na amfani da hanyoyi biyu. Ga makiya, sai mu yi amfani da hanyar mulkin shibta, watau kome tsawon lokacin da ya wajaba,

mu hana su sa baki a sha'anin siyasa, mu tilasta su bin dokokin Gwamnatin Jama'a, mu tilasta su yin aikin ƙarfi domin su sauya kansu su zama sababbin mutane. Amma ga jama'a ana amfani da kishiyar haka, ba a amfani da hanyar tilastawa, sai dai da hanyar dimaƙuraɗiyya, watau tilas a bar su su sa baki a sha'anin siyasa, kada a tilasta su yin kaza da kaza, sai dai a yi musu tarbiyya da aikin rarrashi ta hanyar dimaƙuraɗiyya.

Jawabin Rufe Taro a Zama na Biyu na Kwamitin Kasa na Farko na Taron Shawarar Siyasar Jama'ar Sin (23 ga Yuni, 1950).

A ƙarƙashin shugabancin Jam'iyyar Kwaminis, mutanen Sin suna tafiyar da harkar gyara da himma, domin rayad da sha'anin gurguzu na Sin da gaggawa a kan digi mafi ƙwari. Wannan harka ce ta mahawara wadda ke da shugabanci da 'yanci cikin al'umma baki ɗaya a birane da ƙauyuka kan hanyoyi biyu watau gurguzu da

jarinci, kuma kan tushen tsarin mulkin ƙasa da muhimman manufofin siyasa, haliyar aiki ta ma'aikatan gwamnati da Jam'iyya da kuma maganar kyautata zaman jama'a da sauran maganganu ta hanyar kowa ya faɗi dalilinsa a kan gaskiya kuma da cikakkiyar shaida, ta wannan hanya a daidaita duk saɓanin da ke tsakanin jama'a sosai kuma dole ne a daidaita su yanzu. Wannan harka ta gurguzu ce wadda jama'a ke tarbiyyar kansu kuma su sauya kansu daga cikinta.

"Jawabi a Majalisar Rasha don Bikin Cikon Shekaru 40 da Babban Tawayen Gurguzu na Oktoba" (6 ga Nuwamba, 1957).

Da babban aiki a gabammu wajen gineginemmu na ƙasa. Ko da ya ke muna da 'yan Jam'iyya fiye da miliyan 10, amma yawansu kaɗan ne in an kwatanta da jimlar jama'ar ƙasa baki ɗaya. A ma'aikatan

gwamnati da kungiyoyin jama'a da masana'antu, da akwai ayyuka da dama da wadanda ba 'yan Jam'iyya ba za su yi. Ba zai yiwu ba a yi wannan aiki sosai im ba mu san yadda za mu dogara sosai kan jama'a ba kuma mu hada kai da wadanda ba 'yan Jam'iyya ba. Lokacin da muke ci gaba da kokarin karfafa hadin kai cikin dukan Jam'iyya, haka kuma dole ne mu karfafa hadin kai tsakanin dukan kabilun kasa da azuzuwan dimakuradiyya da jam'iyyun dimakuradiyya da kungiyoyin jama'a, kuma mu karfafa, har ila yau mu yada hadadden goshin famar dimakuradiyya na jama'a, kuma dole mu mai da hankali mu kau da dukan abu maras kyau da zai hana hadin kai tsakanin Jam'iyya da jama'a a dukan gabobin aiki.

"Jawabin Bude Taro na Takwas na Wakilan Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (15 ga Satumba, 1956).

4. DAIDAITA SABANI SOSAI TSAKANIN JAMA'A

Akwai sabani iri biyu na zaman al'umma a gabammu, watau sabani tsakanimmu da makiya da kuma sabani tsakanin jama'a ita kanta. Wadannan sabani biyu sun sha bamban da juna a halayensu.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Domin a fahimci wadannan sabani biyu iri daban sosai, watau sabani tsakanimmu da makiyammu da kuma sabani tsakanin jama'a, da farko dai ya kamata a fahimci mene ne "jama'a" da kuma mene ne "makiya". ...

A lokaci na yanzu da mu ke gina gurguzu, duk ajujuwa, rukunin mutane da duk taron mutane a halin zaman al'umma, wadanda suka amince wa kuma suka goyi baya har suka shiga aikin gina gurguzu, suna cikin da'irar jama'a. Duk wani rukuni da wani taron mutane a halin zaman al'umma masu kiyewa tawayen gurguzu, masu gaba da kuma lalata sha'anin gina gurguzu su makiyan jama'a ne.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

A halin da kasarmu ke ciki yau, sabani tsakanin jama'a su ne sabani cikin ajin ma'aikata, sabani cikin ajin manoma, sabani cikin 'yan ilmi, sabani tsakanin ajin ma'aikata da ajin manoma, sabani tsakanin ma'aikata kuma manoma da 'yan ilmi, sabani tsakanin ajin ma'aikata kuma sauran jama'a talakawa da ajin tajiran kasa, sabani cikin ajin tajiran kasa da dai sauransu. Gwam-

natimmu ta jama'a gwamnati ce wadda ke wakiltar bukatun jama'a da gaskiya, kuma gwamnati ce da ke bauta wa jama'a, amma tsakaninta da jama'a kuma akwai wasu sabani. Wadannan sabani suna dauke da sabani tsakanin abin amfanin kasa kuma abin amfanin tarayya da abin amfanin mutum shi daya, sabani tsakanin dimakuradiyya da tattarawa (centralism), sabani tsakanin mai jan ragama da mai bin ragama, sabani tsakanin ra'ayin nuna hakimci na wadansu ma'aikatan gwamnati da jama'a. Duk wadannan ma sabani ne tsakanin jama'a. Galibi dai ana cewa, sabani tsakanin jama'a sabani ne wanda ke dogara bisa ainihin bukatu iri daya na jama'a.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Sabani tsakanimmu da makiya sabani na gaba da juna ne. Amma a cikin jama'a,

saßanin da ke tsakanin jama'a talakawa ba na gaba ba ne, kuma saßani tsakanin ajin zambatattu da na mazambata yana da halin gaba kuma yana da na rashin gaba.

"Game da Hanyar Daidaita Saßani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

A zaman siyasa na jama'ar ƙasarmu, yaya ya kamata a bambanta tsakanin gaskiya da ƙarya a maganganu da ayyukammu? A zatommu, bisa ƙa'idodin Tsarin Mulki na ƙasarmu, kuma bisa yardar dimbin yawancin jama'a da kuma shirye-shiryen siyasa waɗanda jam'iyyu da rukunan siyasa na ƙasarmu suka gabatar tare a lokatai da yawa, galibi dai ya kamata a tsai da ƙa'idodin nan kamar haka:

(1) Maganganu da ayyuka su zamana masu taimakawa ne wajen haɗin kan duk mutanen kabilun ƙasarmu, amma ba su raba su ba.

(2) Su zamana masu amfani ne amma ba masu raunana sauyin gurguzu ko ginin gurguzu ba.

(3) Su zamana masu amfani ga ƙarfafa mulkin shibta na dimaƙuraɗiyyar jama'a, amma ba masu raunana ko rusad da mulkin ba.

(4) Su zamana masu amfani ga ƙarfafa tsarin dimaƙuraɗiyya-tattarawa (democratic centralism), amma ba masu ßata shi ko rage masa ƙarfi ba.

(5) Su zamana masu amfani ga ƙarfafa shugabancin Jam'iyyar Kwaminis, amma ba masu banzatad da ko rage masa ƙarfi ba.

(6) Su zamana masu amfani ga haɗin kan ƙasashen gurguzu na duniya da haɗin kan jama'a masu son zaman lafiya na ƙasashen duniya, amma ba masu ßata su ba.

A cikin waɗannan ƙa'idodi shida, guda biyu mafiya muhimmanci su ne hanyar gurguzu da shugabancin Jam'iyya.

"Game da Hanyar Daidaita Sa-ßani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Maganar nakasa masu ƙin tawayen turu magana ce ta fama wadda ta shafi saßani tsakanimmu da makiya. A cikin jama'a da wasu da ra'ayinsu game da wannan magana ya ɗan sha bamban da namu. Mutane iri biyu ne waɗanda ra'ayinsu ya sha bamban da namu. Waɗanda ke da tunanin 'yan Dama ba su bambanta tsakanimmu da makiya, suna mai da makiya kamar mutanemmu. Suna ɗaukar waɗanda ɗimbin jama'a ke gani makiya ne kamar aminammu. Waɗanda ke da tunanin 'yan "Hagu" suna faɗaɗa fagen saßani tsakanimmu da makiya har ya kai su ga ɗaukan wasu saßani tsakanin jama'a kamar na tsakanimmu da makiya,

kuma suna ɗaukan wasu mutane waɗanda ba masu ƙin tawaye ba ne, kamar masu ƙin tawaye. Duk waɗannan ra'ayoyi biyu ba daidai ba ne. Ba ɗaya a cikinsu da zai iya daidaita maganar nakasa masu ƙin tawaye sosai ko kuwa da zai iya kimanta aikin nan daidai.

"Game da Hanyar Daidaita Sa-ßani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Ba za a iya daidaita saßani iri ɗabam ɗaban ba sai tare da hanyoyi iri ɗabam ɗaban. Misali, saßani tsakanin ajin talakawa da ajin tajirai ana daidaita shi ta hanyar tawayen gurguzu. Saßani tsakanin jama'a da tsarin mulkin gargajiya ta hanyar tawayen dimakuraɗiyya a ke daidaita shi. Saßani tsakanin mallakakkun ƙasashe da daulantaka, sai ta hanyar yaƙin tawayen 'yanta ƙasa a ke daidaita shi. Saßani tsakanin ajin ma'aikata da ajin manoma a halin zaman gurguzu ana daidaita shi ta hanyar

tarayyar noma da na'urantad da sha'anin noma ta hanyar zamani. Saßani cikin Jam'iyyar Kwaminis ana daidaita shi ne ta hanyar kushe da kushewa kai. Saßani tsakanin zaman al'umma da halitta ana daidaita shi ne ta hanyar yalwatar ƙarfin ba da albarka. ... Daidaita saßani dabam daban da hanyoyi dabam daban, wannan ƙa'ida ce wadda dole ne dukan 'yam Marksanci-Leninanci su bi ta sosai.

"Kan Saßani" (Agusta 1937), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Farko.

Tun da ya ke saßani tsakanimmu da maƙiya da kuma saßani tsakanin jama'a sun bambanta a halitta, dole ne a daidaita su ta hanyoyi dabam daban. A taƙaice dai, a saßani na farko sai a ja iyaka tsakanimmu da maƙiya, amma a saßani na biyu sai a ja iyaka tsakanin gaskiya da ƙarya. Haka ne saßani tsakanimmu da maƙiya ma, magana ce ta bambanta gaskiya

da ƙarya. Misali, maganar wa ke da gaskiya mu ko azzaluman gida da na waje kamar daulantaka, mulkin gargajiya da na tajirai-hakimai, kuma magana ce ta gaskiya da ƙarya amma halittarta daban ta ke da ta maganar gaskiya da ƙarya tsakanin jama'a.

"Game da Hanyar Daidaita Saßani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Duk wata maganar tunani da duk wata hamayya cikin jama'a ba za a iya daidaita su da dabarar tilastawa ko kuma ta danniya ba, sai dai da hanyoyin dimaƙuradiyya, hanyoyin taune-taune, kushewa, lallashi da tarbiyya.

"Game da Hanyar Daidaita Saßani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Domin tafiyar da aikinsu na ba da amfani da koyonsu sosai kuma su shirya rayu-

warsu sosai, jama'a na bukatar gwamnati da waɗanda ke shugabanci wajen aikin ba da albarka da kungiyoyin al'adu da tarbiyya su riƙa ba da umurnin da ya dace kuma wajàbabbe ne. Sananne ne ga kowa, ba za a iya tafiyar da zaman lafiya cikin jama'a ba im ba tare da ana ba da irin waɗannan umurnai ba. Umurnai da hanyar lallashi da tarbiyya taimakon juna su ke wajen daidaita saßani tsakanin jama'a. Ko umurnan da a ke bayarwa domin tafiyar da zaman lafiya a cikin jama'a, dole ne a haɗa da lallashi da tarbiyya, domin a yawancin lokaci umurnai kawai ba za su iya aiki ba.

"Game da Hanyar Daidaita Saßani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Lalle ne attajirai da ƙananan tajirai za su bayyana irin tunaninsu. Lalle za su tsaya su bayyana ra'ayinsu a kan al'amarin siyasa da tunani ta ko wace hanya. Ba

zai yiwu ba a hana su bayyana kansu. Bai kamata mu yi amfani da hanyar danniya mu hana su bayyana ra'ayinsu ba, ya kamata mu bari su yi, a wannan lokaci kuwa, mu yi muhawara da su, mu kushe musu a kan yadda ya kamata. Ba shakka dole ne mu kushe wa ko wane irin ra'ayin kuskure. Hakika ba daidai ba ne im mun bar yin suka, mun sa ido mu ga ra'ayoyin kuskure na watsuwa har mu bari su mamaye ko ina. Dole ne a kushe wa ko wane irin kuskure, haka kuma a tuge duk haki mai guba. Amma kada a yi wannan suka ta hanyar dogamatisanci (dogmatism), haka kuma ba za a yi amfani da hanyar metafisik (metaphysics) ba, kuma dole a yi ƙoƙarin amfani da hanyar diyalektik (dialectics). Abin da a ke bukata shi ne bincike ta hanyar kimiyya da cikakkiyar muhawarar shawo kai.

"Game da Hanyar Daidaita Saßani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Abin bukata ne a kushe wa aibin jama'a, ...amma wajen yin haka, dole mu tsaya cikin gaskiya bisa matsayin jama'a, mu yi magana da zuciya daya domin mu tsare su kuma mu koyar da su. Idan aka mai da abokanai makiya, daidai ne da komawa bisa matsayin makiya.

"Jawabi a Taron Yenan kan Wallafa da Fasaha" (Mayu 1942), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Uku.

Saßani da fama suna ko ina kuma sun wajaba, amma hanyoyin daidaita saßani, watau irin kamannun famar, sun bambanta bisa irin halaye daban na saßanin. Wasu saßani suna nuna hali na kiyayya a fili wasu ko ba haka ba ne. A bisa yadda abubuwa ke ci gaba, wasu saßani da su ke da farko ba na kiyayya ba ne, su kan yalwata su zama na kiyayya, haka kuma wasu da su ke na kiyayya ne da farko su kan zama na rashin kiyayya.

"Kan Saßani" (Agusta 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

A halin kullum dai, saßani tsakanin jama'a ba na kiyayya ba ne. Amma suna iya zama na kiyayya idan ba a daidaita su sosai ba, ko kuma an yi sake an nuna rashin damuwa da su. A kasashen gurguzu, kullum wannan abu ne mai iyaka ko kuma abu ne mai gudana cikin dan lokaci. Dalilin shi ne an soke tsarin wani ya zalunci wani, kuma asalin abubuwan moriya ga jama'a daya ne.

"Game da Hanyar Daidaita Saßani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

A kasarmu, saßani tsakanin ajin ma'aikata da ajin tajiran kasa saßani ne tsakanin jama'a. Famar aji tsakanin ajin ma'aikata da ajin tajiran kasa, a galibin lokaci, famar aji ce tsakanin jama'a, domin tajiran kasarmu suna da halaye biyu. A lokacin tawayen dimakuradiyyar tajirai suna da halin tawaye kuma suna da halin sassautawa. A lokacin tawayen gurguzu suna da halin

zaluncin ajin ma'aikata don samo riba kuma suna da wani hali da ke nuna goyon bayansu ga Tsarin Mulki na Kasa da yarda da rikida ta hanyar gurguzu. Tajiran kasa sun bambanta da madaulanta da ma'abutan kasa da ajin tajirai-hakimai. Saßani tsakanin tajiran kasa da ajin ma'aikata saßani ne irin wanda ke gama mai zamba da zambatacce, kuma da ma na kiyayya ne. Amma a kayyadaddun halayen Sin, saßanin kiyayya tsakanin ajin nan biyu, in an iya daidaita shi sosai, za a mai da shi cikin na lumana, kuma a iya daidaita shi ta hanyar lafiya. Idan ba mu daidaita saßani tsakanin ajin ma'aikata da ajin tajiran kasa sosai ba, idan ba mu bi manufar siyasar hadin kai, kushewa da tarbiyya ga tajiran nan ba, ko kuma su tajiran sun ki yarda da wannan manufar siyasa, to, yana iya zama saßani tsakanimmu da makiyammu.

"Game da Hanyar Daidaita Saßani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Azzaluman gida na kasar gurguzu suna gama baki da madaulanta don neman cim ma burin makarkashiyarsu ta yin amfani da saßani tsakanin jama'a wajen ta da fitina da tashin hankali. Abin da ya faru a Hungary, ya zama darasi kuma ya cancanci kowa ya kula.

"Game da Hanyar Daidaita Saßani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

5. YAKI DA ZAMAN LAFIYA

Yaki wanda aka fara shi tun daga ɓullowar mahasusin abu (private property) da ajujuwa, shi ne siffar ƙoli na fama domin daidaita saɓani, in saɓanin ya kai wani mataki tsakanin ajujuwa, ko al'umma da al'umma ko ƙasa da ƙasa ko ƙungiyoyin siyasa.

"Matsalolin Sihirin Shiri a Yakin Tawayen Sin" (Disamba 1936), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

"Yaki shi ne ci gaba na siyasa", watau a nan abin da ake nufi shi ne yaki siyasa ce kuma yaki shi kansa motsi ne na siyasa,

tun zamanin da ba a taɓa yaki maras halin siyasa ba. ...

Amma yaki na da halaye nasa na kansa, kuma a nan bai yi daidai da duka-dukan siyasa ba. "Yaki shi ne ci gaba na siyasa ga wadansu hanyoyi na takanas'". Yaki ya kan faru ne domin kau da duk wahalolin da ke bisa hanyar siyasa, idan siyasa ta ci gaba ta kai wani mataki har hanyar siyasa ba ta biyuwa kan yadda aka saba bi. ... Lokacin da aka haye wahaloli kuma aka kai ga cim ma burin siyasa, sai yaki ya ƙare. Muddin dai ba a haye wahalolin duka ba, to, ya kamata a ci gaba da yaki har ga cika burin siyasa. ... Dalili ke nan da za a iya cewa siyasa yaki ne maras zub da jini, kuma yaki siyasa ce mai zub da jini.

"Kan Yaki cikin Dogon Lokaci" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Duk yaƙe-yaƙe a tarihi ana iya raba su kashi biyu, yaƙin adalci da yaƙin rashin adalci. Duk yaƙin neman ci gaba na adalci ne, amma duk yaƙin hana ci gaba na rashin adalci ne. Mu 'yan Kwaminis muna famar ƙin duk yaƙi maras adalci na hana ci gaba, amma ba mu ƙin yaƙin adalci na neman ci gaba. Mu 'yan Kwaminis ba kawai ba mu ƙin yaƙin adalci na neman ci gaba ba ne, amma har mu kan shiga cikin ɗawainiyar da himma. Kan yaƙi maras adalci, alal misali, Yaƙin Duniya na Farko yana shaida irin yaƙi na rashin adalci, duk 'yan adawa biyu suna fama ne domin abin da zai amfani daulantaka, shi ne dalilin da ya sa 'yan Kwaminis na duniya suka tashi tsaye suka nuna cikakken ƙin goyon baya. Hanyar da za a bi wajen ƙin wannan yaƙi ita ce kafin ya faru ya kamata a nuna ƙarfin hali domin hana aukuwarsa, amma idan ya auku, kuma in dai ya yiwu ya kamata da yaƙi a

ƙiyewa yaƙi, a sa yaƙin adalci a ƙiyewa yaƙin rashin adalci.

"Kan Yaƙi cikin Dogon Lokaci" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

A cikin halin zama na aji, tawayen turu da yaƙin tawaye ba su da makawa. Idan ba da su ba, ba mai yiwuwa ba ne a sami babban ci gaban zaman al'umma kuma a hamɓurad da ajin azzalumai masu mulki, kuma ba mai yiwuwa ba ne a ce za a sa jama'a su kama ragamar mulki.

"Kan Saɓani" (Agusta 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Yaƙin tawaye abu ne mai ƙin guba, ba kawai zai share gubar maƙiya ba, amma har zai ɗauraye daudarmu. Duk yaƙin adalci na tawaye yaƙi ne mai ƙarfin gaske, yana iya rikiɗa abubuwa da yawa ko ya buɗe hanyar rikiɗa su. Yaƙin tsakanin

Sin da Japan zai rikida Sin da Japan. Muddin dai Sin ta nace ga yakin kuma ta nace ga goshin famar hadin kai sai tsohuwar Japan ta rikida ba shakka ta zama sabuwar Japan kuma tsohuwar Sin ta zama sabuwar Sin. Kuma ko a Sin ko a Japan mutane da abubuwa su ma za su rikida cikin yakin da kuma bayan yakin.

"Kan Yaki cikin Dogon Lokaci" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ya kamata ko wane dan Kwaminis ya sanad da kansa da gaskiyan nan cewa, "Daga bakin bindiga ake samun mulki."

"Matsalolin Yaki da Sihirin Shirin Yaki" (6 ga Nuwamba, 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Cibiyar aiki da mafi girman kamannu na tawayen turu, shi ne kwatar mulki ta fama da makamai, watau shi ne daidaita

al'amari ta hanyar yaki. Wannan ka'idar tawaye ta Marksanci-Leninanci tana da gaskiya a ko ina ko a Sin ko a sauran kasashe.

"Matsalolin Yaki da Sihirin Shirin Yaki" (6 ga Nuwamba, 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

A kasar Sin da ba a sanya fama ta makamai ba, da ajin talakawa bai samu wuri ba, kai har da jama'a da Jam'iyyar Kwaminis ma, da kuma ba a yi zancen nasara ta tawaye ba. Tun shekaru goma sha takwas a cikin yake-yaken tawaye ne, Jam'iyyarmu ta yalwatu, ta karfafu kuma ta dau ra'ayin Bolshefik (Bolshevic), kuma da ba famar makamai, kai da ba Jam'iyyar Kwaminis ta yau. Bai kamata ba abokanammu na Jam'iyya su ce za su manta wannan fasaha wadda muka samu da jinimmu.

"Gabatar Da Mujalla Mai Suna *Dan Kwaminis*" (4 ga Oktoba, 1939), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

A bisa ra'ayin Marksanci na game da ƙasa, rundunar soja ita ce muhimmiyar aba wajen mulkin ƙasa. Duk mai son ƙwatar mulkin ƙasa kuma ya tanada shi, tilas sai da rundunar soja mai ƙarfi. Wadansu suna yi mana dariya wai mu "masu ra'ayin yaƙi ke daidaita kome" "omnipotence of war") ne. I, haka ne mu "masu ra'ayin yaƙin tawaye ke daidaita kome" ne, wannan ba mugun abu ba ne, mai kyau ne kuma na Marksanci ne. Bindigogin Jam'iyyar Kwaminis ta Rasha suka kawo gurguzu a can. Mu, muna son ƙago jamhuriyar dimaƙuraɗiyya. Fasahar da aka samu a famar aji a zamanin daulantaka na nuna mana cewa ajin ma'aikata da ɗimbin talakawa ba su iya kada ajin tajirai masu ɗamara da ma'abutan ƙasa sai da ƙarfin bindiga. A nan, ma iya cewa ba za a iya rikiɗad da duniya ba, sai tare da bindiga.

"Matsalolin Yaƙi da Sihirin Shirin Yaƙi" (6 ga Nuwamba, 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Mu masu son a soke yaƙi ne, ba mu ƙaunar yaƙi. Amma ba za a iya soke yaƙi ba sai tare da yaƙi. Domin kada a sake ganin bindiga, tilas a ɗau bindiga.

"Matsalolin Yaƙi da Sihirin Shirin Yaƙi" (6 ga Nuwamba, 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Yaƙi, shi wannan dodo mai sa mutane kashe juna, a ƙarshe dai yalwatar halin zaman ɗan Adam zai sa a soke shi, kuma soke yaƙi abu ne da zai tabbatu ba da jimawa ba. Amma hanya ɗaya ce tak ta soke yaƙi, watau a sanya yaƙi domin ƙiye wa yaƙi, a sanya yaƙin tawayen turu domin ƙiye wa yaƙin ƙin tawaye, a sanya yaƙin tawayen al'umma domin ƙin yaƙin ƙin tawayen al'umma, kuma a sanya yaƙin tawayen aji domin ƙin yaƙin ƙin tawayen aji. ... Lokacin da zaman ɗan Adam ya ci gaba har ya kai ga soke aji, ga soke mulkin ƙasa, to, ba za a sake jin yaƙi ba ko na ƙin tawayen turu ko na tawayen turu, ko na

rashin adalci ko na adalci, wannan lokaci zai zama na zaman lafiyar dan Adam har abada. Nazarimmu na dokokin yakin tawaye na daga burin neman soke duk yaki ne. A nan ne fa bambanci ke tsakanimmu, mu 'yan Kwaminis da duk ajujuwan mazambata.

"Matsalolin Sihirin Shiri a Yakin Tawayen Sin" (Disamba 1936), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Kasarmu tare da sauran kasashen gurguzu duka suna kaunar zaman lafiya har da jama'ar duniya baki daya. Sai dai kawai wasu rukunan tarunan tajirai na 'yan kasashen daulantaka kadan wadanda suka dogara kan kai hari domin samun riba ke bidar yaki, amma ba zaman lafiya suke so ba.

"Jawabin Bude Taro na Takwas na Wakilan Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (15 ga Satumba, 1956).

Domin kafa zaman lafiyar duniya dauwamarrime, ya kamata mu ci gaba da karfafa zumunci da gama gwiwa tare da kasashe 'yanuwa na sansanin gurguzu, kuma mu kara karfafa hadin kammu da duk kasashe masu son zaman lafiya. Ya kamata mu kokarta mu kulla hulda yadda ya kamata da duk kasashe masu son zaman lafiya da mu bisa ka'idodin girmama kasa da 'yancin juna da darajanta juna da moriyar juna. Ya kamata mu ba da goyon baya sosai ga harkar neman 'yanci da suncin kai na kasashen Asiya, Afirka da Latin Amirka, da harkar tsare zaman lafiya da famar adalci na duk kasashen duniya.

"Jawabin Bude Taro na Takwas na Wakilan Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (15 ga Satumba, 1956).

Game da kasashen daulantaka, ya kamata mu gama kai tare da jama'ar da ke can, kuma mu bidi wanyewar zaman lafiya da

ƙasashen nan, mu yi ciniki da su kuma mu hana yaƙi wanda kila mai iya aukuwa ne, amma ko kusa kada mu yi tsammanin da bai shafi gaskiya ba game da su.

"Game da Hanyar Daidaita Sa-ɓani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Muna son zaman lafiya. Amma fa idan daulantaka ta nace wa yaƙi, ba abin da za mu zaɓa sai mu ƙudura niyya mu yi yaƙi sa'an nan mu nufi gina ƙasa. Ko wace rana kana tsoron yaƙi, to, idan yaƙi ya ɓullo fa? Na riga na faɗi cewa Iskar Gabas tana rinjayar Iskar Yamma kuma yaƙi ba zai faru ba, yanzu kuma na ƙara jaddadawa domin cika zance ko yaƙi yaka ɓullo. Ta haka zai zama an riga an duba halayen nan biyu kan faruwar yaƙi ko rashin faruwarsa.

Jawabi a Taron Mosko na Jam'iyyun Kwaminis da na Ma'aikata na Kasashen Duniya (18 ga Nuwamba, 1957).

Yanzu jama'a a ƙasashen duniya duka suna nan suna ta zancen ko yaƙin duniya na uku zai ɓullo. A kan wannan al'amari ma, dole ne mu shirya hankulammu kuma mu yi binciken al'amarin. Mun dage bisa son zaman lafiya da ƙin yaƙi. Amma idan madaulanta suka yi taurin kan tsakulo sabon yaƙi, bai kamata ba mu ji tsoro. Ra'ayimmu game da wannan al'amari ɗaya ya ke da ra'ayimmu kan ko wane tashin hankali, na farko, mu ƙi, na biyu, ba mu tsoro. Bayan Yaƙin Duniya na Farko, sai ƙasar Rasha ta ɓullo, ga ta kuwa da mutane miliyan 200. Bayan Yaƙin Duniya na Biyu, sai aka kafa sansanin gurguzu mai mutane miliyan 900. Ba shakkar cewa idan madaulanta za su nace ga ta da yaƙin duniya na uku, lalle ɗarurrukan miliyan na mutane za su koma ta wajen gurguzu, daga nan wurare kaɗan za su saura wa madaulanta,

mai yiwuwa ne ma tsarin mulkin daulantaka ya rushe gaba daya.

"Game da Hanyar Daidaita Saßani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Su ta da fitina, su yi asara, su sake ta da fitina, su sake yin asara, ta haka ne fa har zuwa ga hallakarsu, wannan shi ne karkon (logic) madaulanta da duk azzaluman duniya game da sha'anin jama'a kuma har abada ba za su iya ketare wannan karko ba. Wannan wata doka ce ta Marksanci. Da mu ke cewa "daulantaka keta ce", abin da muke nufi shi ne, halinta na zanen dutse ne kuma har abada madaulanta da sonsu ba za su ajiye wukarsu ta fawa ba, kuma ba za su zama mummunai (Buddhas) ba har zuwa karshensu.

Su shiga fama, su yi asara, su sake shiga fama, su sake asara, su sake shiga sabuwar fama har ga cim ma nasarar karshe, wannan shi ne karkon jama'a, ita ma jama'a

ba za ta iya ketare wannan karko ba har abada. Wannan ma wata doka ce ta Marksanci. Tawayen turun Rashawa ya bi wannan doka, haka zalika tawayen turun Sinnawa.

"A Bar Zaton Iska, A Shirya domin Fama" (14 ga Agusta, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ko ta wane hali bai kamata ba samun nasara ya sa mu sassauta lurarmu game da mummunar makarkashiyar neman huce takaici ta madaulanta da karnukansu, duk wanda ya yi sake zai ga damarar siyasarsa ta kwance kuma ya saißance.

"Furuci a Kwamitin Shiri don Sabon Taron Shawarar Siyasa" (15 ga Yuni, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Madaulanta da karnukansu azzalumai Sinnawa ba za su hakura da asarar da suka

yi a ƙasar Sin ba. Za su ci gaba da gama baki ta ko wace hanya mai yiwuwa don adawa da jama'ar Sin. Ga misali, za su dinga turo karnukansu cikin ƙasar Sin domin su farraƙa jama'a su ta da fitina. Tabbat ne cewa ba za su bar waɗannan take-take ba. Ga misali, madaulanta za su tura azzaluman Sin su done tashoshin ruwa na ƙasar Sin, har ma za su iya taimaka musu da ƙarfin kansu. Idan dai da dama, za su yi haka. Bugu da ƙari ma, in suna son shiga sabon dandi, za su aiko wasu rukunan soja su kawo wa iyakar Sin hari, wannan abu mai yiwuwa ne. Ya kamata mu yi la'akari da duk abubuwan nan sosai.

"Furuci a Kwamitin Shiri don Sabon Taron Shawarar Siyasa" (15 ga Yuni, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

Duniya ci gaba ta ke, kuma gobe na da haske, ba wanda zai iya hana wannan babbar juyawar tarihi. Ya kamata akai-akai mu rika aikin furofaganda a cikin jama'a game da halin ci gaba na duniya da gobe mai haske domin taimakawa jama'a wajen ba da imani ga nasara.

"Kan Shawarwarin Chungking" (17 ga Oktoba, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

Ko kaɗan bai kamata ba kwamandodi da sojoji na Rundunar Sunce Jama'a su ce za su ɗan sassauta himmarsu ta faɗa. Duk tunani mai sa a sassauta himmar faɗa ko a ƙankanta makiyi, ba daidai ba ne.

"Rahoto ga Cikakken Zama na Biyu na Taro na Bakwai na Kwamitin Tsakiya na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (5 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

6. DAULANTAKA DA DUK AZZALUMAI DAMISOSHIN TAKARDA NE

Duk azzalumai damisoshin takarda ne. A fuska, suna da ban tsoro, amma a gaske ba su da ƙarfin da a ke zato. Idan za mu kalli abubuwa da idon gobe, sai mu ga jama'a ce ke da ƙarfin gaske, amma ba azzalumai ba.

> "Taɗi tare da Anna Louise Strong 'yar Jarida ta Amirka" (Agusta 1946), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

Yadda dai ba wani abu a duniya maras kamanni biyu, (watau doka ce ta haɗuwar kishiyoyi) daulantaka da duk azzalumai

su ma kamanni biyu gare su. Su damisoshin gaske ne kuma har ila yau damisoshin takarda ne. A zamanin da, ajin iyayengijin bayi, ajin ma'abutan ƙasa na mulkin gargajiya da ajin tajirai kafin su sami mulki, kuma ɗan lokaci kaɗan bayan samunsa, sun nuna mazakuta, ra'ayin tawaye da neman ci gaba, su damisoshin gaske ne. Amma da zamani ya ba da baya, sabo da masu adawa da su watau ajin bayi, ajin manoma da na talakawa da kaɗan kaɗan suna yalwata kuma suna sanya fama domin ƙiye musu, wadda a kwana a tashi sai ƙara tsanani ta ke, sai da kaɗan kaɗan su ajujuwan mulkin nan suka rika rikiɗa suka zama baibai ɗin ainihinsu suka zama azzalumai, 'yan koma baya, damisoshin takarda. Kuma a ƙarshe sai jama'a ta hamɓurad da su ko za ta hamɓurad da su. Ko a famar nan ta ko rai ko mutuwa da jama'a ke yi da su, ajujuwan nan na zalunci, koma baya kuma ruɓaɓɓe na da kamanni biyu. A wani fanni damisoshin gaske ne, suna fatattaka mutane, suna fatat-

taka miliyan kai har ɗarurrukan miliyan. Al'amarin ɓamar jama'a ya ratsa lokaci mai tsananin wahala, kuma hanyarsa tana cike da zagaye-zagaye. Jama'ar Sin ta shekara fiye da ɗari kafin ta share mulkin madaulanta, mulkin gargajiya da attajirai-hakimai daga ƙasar Sin, kuma ta ba da rayuka wajen miliyoyi na ɗan Adam kafin ta kawo ga nasara a 1949. Ku duba ku gani shin su ba damisoshi ne masu rai ba, damisoshin ƙarfe da damisoshin gaske? Amma a ƙarshe sun zo sun zama damisoshin takarda, matattun damisoshi, damisoshin laka. Waɗannan abubuwan tarihi ne na gaske. Ko ba a taɓa ganinsu da jinsu ba? A gaske dai an taɓa dubu-dubbai, kai har ɗarurrukan dubbai! Don haka in an duba ainihin halinsu, in an dubi gobe kuma in an duba da ra'ayin sihirin shirin yaƙi sai mu gane cewa, daulantaka da duk azzalumai ya cancanta mu mai da su mazauninsu watau damisoshin takarda. A kan wannan ne, mu ke tsara tunani na sihirimmu na shirin yaƙi.

A wata fuska kuma su damisoshi ne masu rai, damisoshin ƙarfe, damisoshin gaske, suna cin mutum. A kan wannan ne mu ke tsara tunanimmu na dabarun yaƙi.

> Jawabi a Taron Wuchang na Kwamitin Zartaswa na Siyasa na Kwamitin Tsakiya na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin (1 ga Disamba, 1958).

Na farɗi cewa duk shahararrun azzalumai masu ƙarfi, damisoshin takarda ne kawai. Dalili shi ne sun ware kansu daga jama'a. Ku duba, Hitla, ba damishin takarda ba ne? Ba a ka da Hitla ba? Kuma na farɗi cewa sarkin Rasha (Tsar), sarkin ƙasar Sin da daulantakar Japan su ma su damisoshin takarda ne, kun dai gani ba wanda ba a kada shi ba a cikinsu. Har yanzu dai daulantakar Amirka ba a ka da ta ba tukuna, ga ta kuma da bom ɗin atom. A ganina

ita ma za ta yi kunya. Ita ma damisar takarda ce.

Jawabi a Taron Mosko na Jam'iyyun Kwaminis da na Ma'aikata na Kasashen Duniya (18 ga Nuwamba, 1957).

"Mutum ya daga dutse sama kawai don ya jefa kan kafarsa", wannan karin magana ne da Sinnawa ke siffanta take-taken wasu shashashu. Azzalumai na ko wace kasa su ne irin wadannan shashashu. Duk danniyar da su ke nuna wa jama'a 'yan tawaye ba abin da za ta sa, sai dai a karshe ta kara fadada da hasa wa tawayen jama'a wuta da hanzari. Duk taskun da sarkin Rasha da Chiang Kai-shek suka nuna wa jama'a 'yan tawaye, ashe bai yi aikin hanzarta babban tawayen turu na Rasha da na Sin ba?

"Jawabi a Majalisar Rasha don Bikin Cikon Shekaru 40 da Babban Tawayen Gurguzu na Oktoba" (6 ga Nuwamba, 1957).

Tun shekaru tara ke nan daulantakar Amirka ta mamaye yankin kasarmu na Taiwan, kuma 'yan kwanakin nan da suka shige, ta tura sojojinta suka mamaye kasar Lebanon. Amirka ta kafa darurrukan sansanin soja a dimbin kasashe na duniya. Yankin Sin na Taiwan, Lebanon da duk sansanin sojojin da Amirka ta kafa a kasashen waje, kamar azargiya ce a wuyan daulantakar Amirka. Ba wasu ba ne, Amirkawa su kansu ne su ke tuka wannan azargiya kuma suna laulayawa a wuya, kuma suna mika bakin azargiyar ga jama'ar Sin da na kasashen Larabawa da dai sauran jama'ar duniya masu son zaman lafiya kuma masu famar kin hari. Muddin dai mahara Amirkawa suna kara dadewa a wuraren nan, to kuwa, suna kara laulaya azargiyar da za ta shake musu wuya.

Jawabi a Taron Koli game da Harkokin Kasa (8 ga Satumba, 1958).

Lokacin da ya saura wa madaulanta ba mai tsawo ba ne domin kullum suna shuka ko wace irin ßarna. Sun nace ga ɗaure wa azzalumai maƙiyan jama'a na ƙasashe dabam daban gindi, sun mamaye ɗimbin ƙasashen da ke ƙarƙashin mallaka, da wasu ƙasashe masu guntun mulki da sansanin sojoji, kuma suna yi wa zaman lafiya kurari da yaƙin atom. Ta haka, sun tilasta kashi ƒiye da casa'in a ɗari na jama'ar duniya tashi tsaye ko za su tashi tsaye su yi fama da su gaba ɗaya. Amma yanzu dai madaulanta na da sauran rai, har yanzu suna taƙama suna duk mugun abin da suka ga dama a Asiya, Afirka da Latin Amirka. Har yanzu a ƙasashen Yamma suna danne jama'a na wadannan ƙasashe. Dole ne wannan hali ya sake. Aikin da ya saura ga jama'ar duniya shi ne su wargazad da hari da danniya na madaulanta musamman madaulanta Amirkawa.

Tadi da ɗan Jarida na Kamfanin Watsa Labaru na Hsinhua (29 ga Satumba, 1958).

Daulantakar Amirka tana ɗaga kai da yin ƙankanci a ko ina, ta sa kanta a matsayin gaba da jama'ar duniya, kuma sai ƙara keße kanta ta ke yi. Bom ɗin atom da na hidirojin (hydrogen) da ke hannunta ba za su iya tsorata duk waɗanda su ke ƙin zama bayi ba. Ba mai yiwuwa ba ne a ce za a iya tsai da ambaliyar ßacin ran jama'ar duniya masu ƙin mahara Amirkawa. Tabbat ne famar jama'ar duk duniya wajen ƙiyewa daulantakar Amirka da karnukanta, za ta ƙara samun nasara mafi girma.

"Jawabin Goyon Bayan Famar Gaskiya ta Kishin Kasa Da Jama'ar Panama Suke Yi don Kiyewa Daulantakar Amirka" (12 ga Janairu, 1964).

Idan rukunan tarunan tajirai na Amirka suka ƙuƙe wa manufar siyasarsu ta kai hari da yaƙi, ba makawa, lalle, rana na zuwa da jama'ar duniya za su rataye su. Irin

karkon da ke jiran duk masu taya Amirkawa makarkashiya ke nan.

Jawabi a Taron Koli game da Harkokin Kasa (8 ga Satumba, 1958).

Domin yin fama da makiyi, mun yalwata ra'ayin nan a dogon lokaci cewa, ta wajen sihirin shirin yaki, ya kamata mu kankanta duk makiyi, amma ta wajen dabarun fada, ya kamata mu dauke shi bisa gaskiya. Watau wannan yana nufi dole mu kankanta makiyi sukutum, amma dole mu dauke shi bisa gaskiya a ko wace kayyadaddiyar matsala. Idan muka ki kankanta sukutum din makiyi, to kuwa, za mu fada cikin kuskuren zarafintaka. Marks da Engels su biyu kadai ne, amma a lokacin can sun fadi cewa, tabbat ne za a hamburad da tajirci a duniya. Amma a bisa ko wane kayyadadden al'amari, bisa duk al'amari wanda ya shafi ko wane makiyi takanas, idan muka ki ba da gaskiya, to ku-

wa, za mu fada cikin kuskuren dandintaka (adventurism). A cikin yaki, fada da daya daya a ke yi, kuma da daya daya a ke cinye karfin rukuni-rukuni na makiya. Da dai dai a ke gina ma'aikata. Manomi, sai da kunya kunya ya ke hude gonarsa. Haka ma ya ke wajen cin abinci. A sihirin shirin yaki, muna kankanta cin abinci—mun tabbata za mu iya cinyewa. Amma wajen ci, sai da loma loma mu ke yi. Ba ya yiwuwa mu ce za mu hadiye duk abinci gaba daya a wurin liyafa. Wannan shi ne abin da a ke kira warware al'amura da dai dai, a sojance sai a kira haka fatattaka makiyi da daya daya.

Jawabi a Taron Mosko na Jam'iyyun Kwaminis da na Ma'aikata na Kasashen Duniya (18 ga Nuwamba, 1957).

Ina zato fa, halin da kasashen duniya ke ciki yanzu ya kawo ga wani sabon juyi.

Yanzu da iska iri biyu a duniya, watau Iskar Gabas da Iskar Yamma. Da wani karin magana na Sinnawa, "Ko Iskar Gabas ta haye kan Iskar Yamma ko kuwa Iskar Yamma ta haye kan Iskar Gabas". A ganina, bisa yadda halin matsayin duniya ya ke yanzu Iskar Gabas ce ta ke haye wa Iskar Yamma, watau ma'anar haka ita ce karfin gurguzu ya samu fifita sosai kan karfin daulantaka.

Jawabi a Taron Mosko na Jam'iyyun Kwaminis da na Ma'aikata na Kasashen Duniya (18 ga Nuwamba, 1957).

7. A IYA FAMA, A IYA NASARA

Jama'a na duniya, ku hada kai, ku naushe mahara Amirkawa da dukan karnukansu! Jama'ar duniya duka ku nuna karfin hali ku nuna jaruntaka ga sanya fama, kar ku ji tsoron wahaloli, ku ci gaba da fama bisa fama, daga nan ba shakka duniya baki daya za ta zama ta jama'a. Duk shaidanu za a hallaka su.

"Sanarwar Goyon Bayan Jama'ar Kongo (L.) kan Kiyewa Harin Amirka" (28 ga Nuwamba, 1964).

Bayan Jam'iyyar Kwaminis ta Sin ta kimanta irin halin da kasashen duniya da na gida ke ciki sosai bisa kimiyyar Mark-

sanci-Leninanci, sai ta gane cewa duk hari na azzalumai ko na gida ko na waje, ba kawai wajibi ne a rugurguje shi ba amma har a iya tabbatar da haka. Lokacin da girgije ya duhunta samaniya, muna cewa wannan abu ne na ɗan lokaci kawai, duhun zai baje nan da nan, kuma rana za ta ɓullo ba da jimawa ba.

"Halin Da Ake ciki Yanzu da Ayyukan Gabammu" (25 ga Disamba, 1947), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

A bisa tarihi, duk tarkacen azzalumai da suka kusa rushewa tilas ne za su nemi yin shure-shuren mutuwa domin ƙiyewa ƙungiyoyin tawaye, amma wasu 'yan tawaye su kan rikice wani ɗan lokaci domin irin babakeren tarkacen azzaluman nan, ba su ganin muhimmin abu cewa maƙiyi ya kusa hallaka, su kuma nasararsu ta gabato.

"Juyi a Yaƙin Duniya na Biyu" (12 ga Oktoba, 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Idan suna (watau Jam'iyyar Kuomintang) son faɗa, to kuwa, za mu hallaka su kwata-kwata. Ga dai yadda abubuwa su ke, idan sun taɓa mu, za mu hallaka su sai su ji dadi, idan hallaka su muka yi kaɗan, sai su ji ɗan dadi, idan mun ƙara hallaka su, sai su ƙara jin dadi, idan mun hallaka su gaba ɗaya sai su ji dadi gaba ɗaya. Al'amuran Sin rikitattu ne domin haka zai bukaci mu ƙara wasa kwaƙwalwarmu. Idan sun zo domin faɗa, lalle za mu yi faɗa, za mu yi faɗa domin samo zaman lafiya.

"Kan Shawarwarin Chungking" (17 ga Oktoba, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

Idan wani ya kawo mana hari, idan hali ya dace da yin faɗa, to, tilas ne Jam'iyyarmu ta ɗau matsayin tsare kai kuma kai tsaye mu hallaka shi kwata-kwata (kada mu mai da faɗa kamar abin wasa, kada mu ce za mu yi faɗa sai muna da imanin samun nasara).

Ko ta wace hanya bai kamata ba mu bari babakeren azzalumai ya tsorata mu.

"Sanarwar Da Kwamitin Tsakiya na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin Ya Yi game da Shawarar Zaman Lafiya da Kuomintang" (26 ga Agusta, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Bisa burimmu, ba mu son fada ko da na yini daya ne. Amma fa idan hali ya tilasta mu yin fada, to kuwa, za mu yi fama har karshe.

"Tadi tare da Anna Louise Strong 'yar Jarida ta Amirka" (Agusta 1946), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Mu fa muna son zaman lafiya. Amma muddin dai daulantakar Amirka ba ta bar son keta da hilarta ta neman yada hari ba, niyyar jama'ar Sin ita ce kawai mu ci gaba da yaki tare da jama'ar Koriya. Ba shi ne wai muna son yaki ba. A gare mu mu-

na son a daina yaki nan da nan kuma nan gaba a sulhunta sauran al'amura. Amma daulantakar Amirka ba ta son haka. To, sai a ci gaba da yaki. A shirye mu ke mu ci gaba da fada bisa kome yawan shekarun da daulantakar Amirka za ta so yaki da mu har lokacin da ta yarda ta bari, har lokacin da jama'ar Sin da ta Koriya suka samu cikakkiyar nasara.

Jawabi a Zama na Hudu na Kwamitin Kasa na Farko na Taron Shawarar Siyasar Jama'ar Sin (7 ga Fabrairu, 1953).

Ya kamata mu soke duk tunanin jin tsoro da ragwanci tsakanimmu. Duk ra'ayi mai daukaka karfin makiya fiye da kima da kuma kaskasta karfin jama'a fiye da kima kuskure ne.

"Halin Da Ake ciki Yanzu da Ayyukan Gabammu" (25 ga Disamba, 1947), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Dannannun mutane da dannannun al'ummai ko kaɗan bai kamata ba su sa tsammaninsu na samun 'yanci bisa "hankali" na daulantaka da karnukanta. Sai dai kawai tare da ƙarfafa haɗin kansu da nacewa ga fama, za su iya nasara.

> "Sanarwar Kin Hari da Kashe-Kashe a Vietnam ta Kudu Da Tarkacen Amirka da Ngo Dinh Diem Ke Yi" (29 ga Agusta,1963).

Ko da wane lokaci ne yaƙin basasa a cikin dukan ƙasa zai ɓullo, dole mu shirya sosai. Idan ya ɓullo da wuri, misali gobe da safe, mu ma ya kamata mu shirya. Wannan shi ne abu na farko. A bisa yadda halin da ƙasashen duniya da gida ke ciki yanzu, mai yiwuwa ne a wani lokaci a sa yaƙin basasa ya zama yana da iyaka kuma ya zama yaƙi ne na wasu wurare. Wannan shi ne na biyu. Na ɗaya shi ne mu ke yi wa shiri, na biyu shi ne abin da ke zaune da mu tun da daɗewa. Kai a taƙaice dai, ya kamata mu yi shiri. Idan a shirye mu ke, za mu iya fuskantar ko wane irin rikitaccen hali kamar yadda ya kamata.

> "Halin Da Ake ciki da Manufar Siyasarmu bayan Nasara a Yaƙin Kare Harin Japan" (13 ga Agusta, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

8. YAKIN JAMA'A

Yakin tawayen turu yaki ne na jama'a, ba za a iya yinsa ba sai an ta da jama'a kuma an dogara kansu.

"A Lura Da Zaman Jama'a, A Maida Hankali ga Dabarun Aiki" (27 ga Janairu, 1934), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Farko.

Wace ganuwar karfe ce ta gaskiya? Ita ce jama'a, watau miliyoyi bisa miliyoyi na mutane wadanda da zuciya daya da tunani daya su ke goyon bayan tawayen turu. Wannan fa ita ce ganuwar karfe ta gaskiya wadda ba wani karfi kuma har abada ba wani karfi mai iya rusa ta. Kin

tawaye ba zai iya rugurguza mu ba, sai dai mu jama'a mu rugurguza kin tawaye. Muddin im mun hallara miliyoyi bisa miliyoyi na mutane a kewaye da gwamnatin tawaye, kuma muka yalwata yakin tawaye, ba shakka za mu iya hallaka duk kin tawaye kuma mu kwace duk kasar Sin.

"A Lura Da Zaman Jama'a, A Maida Hankali ga Dabarun Aiki" (27 ga Janairu, 1934), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Farko.

Sai a cikin jama'a ne a ke samun cibiyar wadataccen karfin yaki. Babban dalilin da ya sa Japan ta samu hanyar wulakantarmu shi ne musamman domin jama'ar Sin ba a shirye su ke ba. Idan mun gyara wannan lahani, tabbat mahara Japanawa za su fada cikin zoben da darurrukan miliyan na jama'armu masu tashi suka yi musu, kamar mahaukaciyar guna ta auka wa wutar

daji, da mun yi ihu sai mahara su firgita su faɗa wuta su ƙone.

"Kan Yaƙi cikin Dogon Lokaci" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Wulakancin da madaulanta ke nuna mana ya kai innanaha, har ya cancanci sai mun tasa musu tsaye sosai. Ba kawai ya kamata mu sami babbar rundunar sojan kullum ba, har ma mu kafa ƙungiyar soja ta farar hula ko ina. Ta haka za mu hana madaulanta walawar yin wani abu, idan sun mamaye ƙasarmu.

Tadi da dan Jarida na Kamfanin Watsa Labaru na Hsinhua (29 ga Satumba, 1958).

Idan an dubi duk yaƙin tawaye, sai a ga yaƙin sari-ka-noƙe na jama'a da Jar Rundunar Soja wadda ta ke ita ce muhimmiya a yaƙi suna taimakon juna kamar hannun dama da na hagu, kuma idan mun

samu Jar Rundunar Soja wadda ta ke ita ce muhimmiya ba tare da yaƙin sari-ka-noƙe na jama'a ba, za mu zama kamar mayaƙi mai hannu ɗaya. A ƙayyadaddiyar magana, kuma musamman idan za a duba ta wajen tafiyad da ayyukan soja, yayin da mu ke maganar jama'a wadda ta ke a sansanin tawaye cewa, suna ɗaya daga cikin abin yaƙi, muna nufi muna da jama'a masu makamai. Wannan shi ne babban dalili da ke sa maƙiyi jin tsoro, ba ya iya sa ƙafa a sansanin tawayemmu.

"Matsalolin Sihirin Shiri a Yaƙin Tawayen Sin" (Disamba 1936), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Tabbat ne cin nasara ko rashin nasara a yaƙi ya danganta musamman ga sharuɗan soja, siyasa, tsimi da irin halitta waɗanda masu adawan nan biyu ke ciki. Amma ba haka ya ke kawai ba, ya kuma danganta kan basirar ko wane gefe a zuci wajen ja gaban yaƙi. A wajen ƙokarinsa na samun

nasara a yaki, mashirin sihirin yaki (strategist) ba ya iya wuce iyakar sharudan kayayyaki, amma a cikin wannan iyakar dole ya kokarta ya samo nasara. Fagen aiki na mashirin sihirin yaki na samuwa ne bisa sharadin tahakikanan kayan yaki, amma a wannan fage ma zai iya tafiyad da aikace-aikace da yawa masu gwanin kyau da girman gaske.

"Matsalolin Sihirin Shiri a Yakin Tawayen Sin" (Disamba 1936), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Nufin yaki ba don kome ba sai dai don "ka kiyaye karfinka, ka nakasa na makiyi" (nakasa karfin makiyi, kwance masa damara ne, watau "ka hana shi duk wani karfin kariya", ba wai tilas ne a hallaka ko wane mutum a kungiyarsa ba). A irin yakin zamanin da, da mashi da garkuwa a ke amfani da su wajen yaki, amfanin mashi, kai hari da kuma hallaka makiyi ne, garkuwa kuwa, tsare kai da tattalin

karfin kai. Har yanzu, yalwatar duk makami na bin sawun mashi da garkuwa. Jiragen jefa bom, bindiga mai ruwa da igwa mai zuwa nesa, iskar gas mai sa hawaye, dukansu yalwata ce ta mashi, kuma su ramin fakewa, hular karfe, ginin buya na sumunti da takunkumin tare gas mai sa hawaye, dukansu daga yalwatar garkuwa su ke. Tanki (motar yaki) sabon makami ne wanda ya hada aikin mashi da garkuwa. Kai hari shi ne muhimmiyar hanyar hallaka karfin makiyi, amma bai kamata a bar tsari ba. Nufin kai hari shi ne kai tsaye a hallaka karfin makiyi, kuma a yi tattalin kai, domin idan ba ka hallaka makiyi ba, to kuwa, shi zai hallaka ka. Tsarin kai abin da a ke nufi shi ne domin kai tsaye a yi tattalin kai, amma kuma wata irin hanya ce mai taimaka kai hari, ko kuwa mai sa shirin kai hari. Ja da baya na cikin inuwar tsari, shi ne ci gaban tsari. Amma bin sawu shi ne ci gaba na kai hari. Ya kamata a nuna cewa

a duk burin yaƙi, hallaka ƙarfin maƙiyi shi ne babban abu, tattalin kai kuwa shi ne abu na biyu, domin sai da ɗimbin hallaka ƙarfin maƙiyi za a tabbatad da tattalin kai da gaske. Sabo da haka, kai hari babbar hanya ce wajen hallaka ƙarfin maƙiyi, yana aiki wanda shi ke muhimmi. Amma, tsari wanda ya ke mataimakiyar hanya ce wajen hallaka ƙarfin maƙiyi, kuma ɗaya ce daga hanyoyi wajen tattalin kai, yana aikin taimako. A cikin yaƙi ko da ya ke ana bukatar lokatai da yawa musamman domin tsaro, sauran lokaci kuma musamman domin kai hari, amma idan an dubi sukutum ɗin yaƙi, kai hari kuma shi ne mafi muhimmanci.

"Kan Yaƙi cikin Dogon Lokaci" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Duk ƙa'idodin jan gaban aikin soja na daga digin ƙa'ida ɗaya tak, watau ƙoƙarin tattalin kai da kuma hallaka maƙiyi. ... Yaya za a iya bayyana bajintar sadakad da

rai a wajen yaƙi? Duk yaƙi sai da sadakad da rai, wani gami ma sadakar ta kan yi yawan gaske. Ashe wannan abu ba ya da saɓani da "tattalin kai"? A hakika ba wani saɓani, in an bayyana shi sosai, sadakad da rai da tattalin kai, ko da ya ke kishiyoyin juna ne, amma suna taimakon juna. Sabo da ba kawai ana bukatar irin wannan sadaka wajen hallaka ƙarfin maƙiyi ba, har ma wajen tattalin kai, ana bukatar sadaka—wannan "ƙin tattalin kai" a wani wuri kuma na ɗan lokaci ne (watau sadaka, ko kuma hakkin da za a biya) tilas a yi shi domin tattalin kai ɗin sukutum na har abada. Daga digin ƙa'idan nan duk ƙa'idodi na jan gaban duk aikin soja suka auku, tuń daga ƙa'idar fara harbi (watau mutum ya ɓuya, kuma ya more da ƙarfin wutar da zai buɗe, na farko domin tattalin kai, na biyu kuma domin hallaka ƙarfin maƙiyi), har zuwa ga ƙa'idar sihirin shirin yaƙi, dukansu suna bayyana halin ƙa'idan nan. Duk ƙa'idodin da suka shafi nakaltar fanni na soja, ko dabarun yaƙi,

ko kamfen, ko sihirin shirin yaki, dukansu sharuda ne da a ke tafiyar da wannan digin ka'ida. Ka'idar tattalin kai da hallaka makiyi ita ce tushen dukan ka'idodin sha'anin soja.

"Matsalolin Sihirin Shiri a Yakin Sari-ka-noke don Kiyewa Japan" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ga ka'idodimmu game da sha'anin soja:

(1) Da farko dai a kai hari ga makiya wadanda ke a watse kuma a kebe, sa'an nan ga makiya masu karfi wadanda ke tattare.

(2) A fara kwace kananan birane, maraya da kuma dimbin yawan kauyuka kana a fada wa kasaitattun birane.

(3) Babban nufimmu shi ne, hallaka makiya ginshikai amma ba tsaro ko kwatar birni ko wuri ba. Rikewa da kwace birni ko wuri akibar hallaka makiya ginshikai ne, kuma ba kasau ba a ke iya kwacewa

kuma a rike birni ko wuri har kullum, sai bayan sun yi ta juyin masa tukuna.

(4) A ko wane fada a tattara karfi sosai (wanda zai ninka karfin makiyi gida biyu, uku, hudu kai wani gami ma har zuwa biyar, shida), a yi wa makiya zobe, a kokarta wajen hallaka su duka, kada a ba su sararin da za su tsere. A wadansu halaye musamman, a yi amfani da dabarar kai wa makiyi duka mai tsanani, watau a tattara duk karfi domin fuskantar makiyi, kuma wani karfi ya far masa ta gefe guda ko kuma ta duk gefe biyu, a hallaka kashi guda kuma a rugurguje sauran kashi domin rundunarmu ta samu ta kaura da sauri wajen hallaka wadansu makiya. A yi kokarin kiyaye fadan ta'adi cikin wanda riba ta kan yi wa asara gaira, ko kuwa su tashi daidai. Ta haka, ko da ya ke a yaki gaba daya (ta wajen yawan soja) karfimmu dan kadan ne, amma za mu sami tabbatacce fifiko a ko wane sashi da ko wane

fada, kuma wannan shi ne zai tabbatad mana da nasara a ko wane fada. Da sannu sannu za mu haye wa makiya a sukutum har mu hallaka su duka baki daya.

(5) Kada a shiga fada wanda ba a yi wa shiri ba, ko fada wanda ba a tabbata za a yi nasara a cikinsa ba. A yi cikakken kokari domin shirin kirki a duk fadan da za a shiga, kuma a tabbatar da nasara a duk irin halayen da ke tsakanimmu da makiya.

(6) A yi amfani sosai da halimmu na fama, watau bajinta a fagen fama, babu tsoron mutuwa, babu tsoron gajiya da kuma ci gaba da yaki (watau a yi ta yin fama bisa fama a gajeren lokaci ba hutu).

(7) A yi kokarin hallaka makiyi a lokacin kaura. Kuma a ba da karfi wajen dabarar kai hari ga matsayi, a kwace muhimman wurare da biranen da ke hannun makiyi.

(8) Ta wajen kai hari ga birane, a tsaya ga kwace duk muhimman wurare da duk birane da makiyi ya yi wa sake. A duba lokacin da ya dace domin kwace muhimman wurare da birane wadanda makiya ba su tsare su ba sosai amma fa sai idan hali ya yi. Game da muhimman wurare da birane wadanda makiya ke tsaro sosai, a dakata sai kome ya shiryu kana a kwace su.

(9) Mu cika karfimmu da duk makamai da kuma yawancin makiya da muka kama. Babbar cibiya ko ta mutum ko ta kayan yaki ta rundunarmu musamman tana fagen fama.

(10) A iya amfani da dan lokacin da ke tsakanin wannan fada da wannan domin hutu, a koyad da, kuma a karfafad da sojojimmu. Galibi dai bai kamata ba lokacin hutu, koyo da karfafawa ya cika tsawo, kuma a kokarta hana makiyi samun damar hutawa domin ya samu ya sake jin karfin jiki.

Wadannan su ne muhimman dabarun da Rundunar Sojan Sunce Jama'a ta yi amfani da su wajen cin Chiang Kai-shek. A cikin dimbin shekaru na famar kin makiyan gida da na waje ne, Rundunar Sojan Sunce Jama'a ta kago su, kuma sun dace sosai da irin matsalarmu ta yau. ... sihirin shirin yaki da dabarummu na yaki sun kafu bisa tushen yakin jama'a. Ba runduna mai kin jama'a wadda za ta iya amfani da sihirin shirin yaki da dabarun yaki irin namu.

"Halin Da Ake ciki Yanzu da Ayyukan Gabammu" (25 ga Disamba, 1947), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Idan ba shiri, fifiko tsakanin karfi da karfi ba zai iya zama fifikon gaske ba, kuma ba za a iya buga gaba na yin wani abu ba. Idan an fahimci wannan gaskiya, rukunai masu karamin karfi amma shiryayyu, su kan iya doke makiyi mai fifiko, idan sun kai masa hari ba zato.

"Kan Yaki cikin Dogon Lokaci" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

9. RUNDUNAR SOJA TA JAMA'A

Idan da ba rundunar soja ta jama'a, da jama'a ba ta da kome.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Wannan runduna tana da karfi domin duk sojojinta suna da lamirin biyayya, sun gamu ne suna fama ba don wai tsare mahasusin amfanin tsirarrun mutane ba, ko wani dan rukuni ba, amma domin tsare amfanin dimbin jama'a da amfanin al'umma baki daya. Nufin wannan runduna daya tak shi ne ta tsaya sosai wajen jama'ar

Sin kuma ta bauta wa jama'ar Sin da zuciya guda.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Jar Rundunar Soja ta Sin kungiya ce mai damara wadda ke tafiyad da aikin siyasa na tawaye. Musamman ma a zamanin yau, aikin gaban Jar Rundunar Soja bai tsaya ga fada ba kawai, ban da fadan da za ta yi domin nakasa karfin makiyi, kuma ya kamata ta dau muhimman ayyuka, kamar su yin furofaganda a jama'a, shirya jama'a, yi wa jama'a damara da taimaka wa jama'a domin kafa mulkin tawaye kai har da kafa kungiyoyin Jam'iyyar Kwaminis. Jar Rundunar Soja ba ta yaki domin yaki kawai, amma tana yaki ne domin furofaganda a jama'a, ta shirya su, ta yi musu damara, ta taimaka musu kafa mulkin tawaye. Idan ba wannan nufi, da kuwa yaki ba ya

da ma'ana, kuma ba amfanin rayuwar Jar Rundunar Soja.

"Kan Daidaita Ra'ayin Kuskure a cikin Jam'iyya" (Disamba 1929), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Har kullum Rundunar Soja ta Suncin Jama'a kungiya ce ta fada. Ko ma bayan nasara a kasa baki daya, rundunarmu za ta zama kungiya ce ta fada a cikin lokacin tarihi da ba a soke ajujuwa a kasarmu ba kuma da tsarin daulantaka a duniya. Game da wannan, ko kusa bai kamata ba mu nuna rashin jituwa ko wani dan wasuwasi.

"Rahoto ga Cikakken Zama na Biyu na Taro na Bakwai na Kwamitin Tsakiya na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (5 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Muna da runduna ta fada kuma da runduna ta aiki. Domin fada muna da Rundunar Hanya ta Takwas da kuma Sabuwar

Runduna ta Hudu, amma ko su ma suna da ayyuka biyu, fada da aikin kawo albarka. Da irin wadannan rundunoni biyu da kuma rundunar yaki wadda ta gwaninta a wadannan ayyuka biyu tare da iya aiki a jama'a, za mu haye duk wahala kuma mu hallaka daulantakar Japan.

"Ku Shirya Kanku!" (29 ga Nuwamba, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Tsaron kasarmu zai karfafa kuma ba za mu yarda madaulanta ko wadanne iri su sake mamaye kasarmu ba. Ya kamata mu zaunad da karfin sojojimmu na jama'a, mu yalwata shi bisa digin jarumar Rundunar Soja ta Suncin Jama'a wadda ta nuna ranarta. Ba kawai rundunar kasa mai karfi za mu samu ba har da rundunar sojojin sama da na ruwa.

Jawabin Bude Taro a Cikakken Zama na Farko na Taron Shawarar Siyasar Jama'ar Sin (21 ga Satumba, 1949).

Ka'idarmu ita ce Jam'iyya ke iko da bindiga, kuma har abada kada a yarda bindiga ta yi ikon Jam'iyya.

"Matsalolin Yaki da Sihirin Shirin Yaki" (6 ga Nuwamba, 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Duk hafsoshi da sojojimmu dole kullum su fahimci cewa mu babbar Rundunar Soja ta Suncin Jama'a ne, mu sojoji ne wadanda babbar Jam'iyyar Kwaminis ta Sin ke ja mana ragama. Muddin dai muna bin umurnin Jam'iyya akai-akai, ba shakka za mu ci nasara.

"Sanarwar Rundunar Sunce Jama'ar Sin" (Oktoba 1947), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

10. SHUGABANCIN KWAMITOCIN JAM'IYYA

Tsarin kwamiti na Jam'iyya muhimmin tsari ne na Jam'iyya domin tabbatad da shugabancin tarayya, kuma a hana mutum daya mamaye dukan sha'ani. Kwanan nan an lura a wadansu kungiyoyin shugabanci (amma ba a duka ba), ana ta ganin mutum daya yana mamaye duk sha'anin aiki kuma ya kan dau shawara shi daya game da wadansu al'amura muhimmai. Ba taron kwamiti na Jam'iyya ne mai daukan shawarar daidaita muhimman al'amura ba, mutum daya ne kawai ke yi, kuma duk sauran 'yan kwamitin Jam'iyya suna nan kawai kamar mutum-mutumi. Saßanin ra'ayi tsakanin 'yan kwamiti na nan an bari kuma ya

dade ba a daidaita shi ba. Hadin kan da ke tsakanin 'yan kwamitin Jam'iyya yana nan kawai a suna, ba na gaske ba ne. Dole a yi wa wannan hali magani. Daga yau ya kamata a shirya cikakken tsarin taro na kwamitin Jam'iyya a dukan kungiyoyin shugabanci daga hedkwatocin jihohi na Kwamitin Tsakiya zuwa ga kwamitocin manyan gundumomi na Jam'iyya, daga kwamitocin Jam'iyya na fagen fama zuwa ga kwamitocin Jam'iyya na birgad har da jihohin sojoji (kananan kwamishoshin da ke karkashin Babban Kwamishin Tawaye na Sojoji ko rukunan ja gaba), rukunai masu ja gora na Jam'iyya a kungiyoyin gwamnati da kungiyoyin jama'a har da kamfanin ba da labaru da jaridu. Duk muhimman al'amura (amma ban da kananan sha'anoni marasa muhimmanci ko kuma al'amura wadanda aka zartad da su a taro, kuma sai kawai jira a ke a aikata su) ya kamata a gabatad da su a kwamiti domin tattauna su, ya kamata 'yan kwamitin da suka halarta su

fadi ra'ayinsu ba tare da shakka ba domin su kai ga tsai da tabbatacciyar shawara, sa'an nan 'yan kwamitin da abin ya shafa su aikata. ... Ya kamata a raba shawarar kwamitin Jam'iyya gida biyu: shawarar kwamitin kullum da shawarar cikakken zama, kada fa a gama su. Har ila yau, ya kamata mu lura cewa jan gaban tarayya ko daukan dawainiyar mutum daya bai kamata ba a darajanta daya a kankanta daya. A cikin soja, lokacin yaki ko kuma idan sharadi ya kama, mai ba da umurni na da hujjar daukar shawarar gaggawa.

"Kan Inganta Tsarin Kwamitin Jam'iyya" (20 ga Satumba, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ya kamata sakataren kwamitin Jam'iyya ya iya zama "babban sikwata". Kwamiti daya na Jam'iyya na da mutane goma zuwa ashirin, kamar sikwata ya ke a cikin soja kuma sakatare kamar "babban sikwata" ya ke. Tafiyad da sikwata din nan da kyau,

lalle ba abu ne mai sauki ba. A yanzu haka ko wace hedkwatar jiha ko karamar hedkwata ta Kwamitin Tsakiya na shugabantar babbar jiha, kuma tana dauke da dawainiya mai nauyi kwarai. Jan ragama ba kawai yana nufin kudura hanyar bi da musamman halaye na manufar siyasa ne ba, amma har da kago dabarun aiki masu kyau. Ko da akwai hanyar bi mai kyau da musamman halaye, wahaloli na iya ßullowa idan ba a mai da hankali ga dabarun aiki ba. Don cika aikinsa na jan ragama dole kwamitin Jam'iyya ya dogara kan "mutanen sikwata", kuma ya bari su yi iyakacin kokarinsu wajen tafiyar da aikinsu sosai. Domin ya zama "babban sikwata" na kirki dole sakataren kwamiti ya yi nazari da bincike sosai. Ko sakatare ko mataimakinsa zai ji wuyar jan ragamar "sikwata" dinsa sosai idan dai bai kula da yin aikin furofaganda da na shirye-shirye tsakanin "mutanen sikwata" dinsa, kuma bai san yadda zai daidaita dangantaka tsakaninsa da mambobin kwamitin, ko

kuma bai nakalci hanyar gudanad da taro sosai ba. Idan duk "mambobin sikwata" ba su yi taki iri daya ba, kada su zata za su iya jan ragamar mutane miliyoyi wajen yaki da aikin gina kasa. Amma, dangantaka tsakanin sakatare da mambobin kwamiti dangantaka ce wadda a cikinta tsirarru dole su bi ra'ayin masu yawa, sabo da haka dabam ta ke da dangantaka tsakanin babban sikwata da mutanensa. A nan dai kwatanci kawai muka yi.

"Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

A gabatad da duk matsaloli a taro. Wannan ba "babban sikwata" ne kawai ya kamata ya yi ba, amma har da mambobin kwamiti. Kada ku yi shawara a bayan mutane. Da al'amari ya samu, ku kira taro, ku gabatad da shi ku tattauna shi, ku dau shawarwari, ta haka sai a daidaita shi. Idan da akwai al'amura kuma ba a gabatad

da su a taro ba, za su jima kuma ba a daidaita su ba, har wani gami ma za su kai shekara da shekaru suna sintiri. Ya kamata da "babban sikwata" da mambobin kwamiti su nuna fahimtar juna cikin dangantakarsu. Babu wani abu muhimmi wanda ya fi fahimtar juna da goyon baya da aminci tsakanin sakatare da mambobin kwamiti, tsakanin Kwamitin Tsakiya da hedkwatocin jihohi na Kwamitin Tsakiya kuma tsakanin hedkwatocin jihohi na Kwamitin Tsakiya da kwamitocin rassan Jam'iyya.

> "Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

"Ku ba juna labari". Watau ya kamata mambobin kwamitin Jam'iyya suna ba juna labari, su rika musayar ra'ayi game da abubuwan da suka sani. Wannan muhimmin abu ne wajen samun baki daya. Amma wadansu ba su yin haka, kuma kamar mutanen da Lao Tzu ya siffanta, "Duk rayu-

warsu, ko da ya ke daga gidajensu suna jin carar zakarunsu da haushin karnukansu, amma ba su ziyarar juna". Daga karshe sun kasa samun baki daya tsakaninsu.

> "Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ku shawarci abokanai mabiya bayanku game da duk abubuwan da ba ku fahimta ko ba ku sani ba, kada ku nuna yardarku da abu sama sama ko ku ki yarda masa. ... Har abada kada mu nuna sanin abin da ba mu sani ba kuma "kada mu ji kunyar tambaya da koyo daga mabiyammu", kuma ya kamata mu saurari ra'ayin kananan ma'aikatan hukuma. Ku fara zama dalibai kana ku zama malaman koyarwa, ku shawarci kananan ma'aikatan hukuma kana ku ba da umurni. ... Cikin abin da kananan ma'aikatan hukuma suke fadi, akwai na gaskiya kuma akwai na kuskure, bayan saurarawa ya kamata mu bincika. Dole

mu saurari ra'ayin gaskiya kuma mu yi aiki da shi. ... Ra'ayin kuskure na ma bi mana, ya kamata shi ma a saurare shi, kuskure ne a ki saurare ko kadan, amma maimakon yin aiki da ra'ayin sai a kushe masa.

"Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

A koyi "buga fiyano (piano)". Idan ana son buga fiyano sai tare da motsa yatsu goma, ba ya yiwuwa a motsa 'yan yatsu kawai a bar sauran. Amma fa, idan an tausa duk yatsu goma gaba daya babu armashin kida. Idan ana son kida mai dadi tilas sai ya zamana motsin yatsu goma na tafiya cikin armashi kuma bi da bi. Ya kamata duk kwamitin Jam'iyya ya kama muhimmin aikin gabansa sosai, kuma gaba daya tare da wannan aiki ya tafiyad da ayyuka na sauran fannoni. Yanzu dai muna kula da fannoni da yawa, dole mu kula da ayyukan duk jihohi, duk kungiyoyin

soja da duk ofisoshi, bai kamata mu ba da kula ga wadansu matsaloli kawai mu bar wadansu ba. Duk inda matsala ta samu, mu sa hannu a kai, wannan ko dabara ce wadda dole mu rike. Wadansu sun iya buga fiyano sosai, wadansu kuma ba su iya ba, kuma da babban bambanci tsakanin armashin kidansu. Mambobin kwamitin Jam'iyya dole su koyi "buga fiyano" da kyau.

"Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

"Ku kama aikin gabanku sosai". A nan ana nufin ba kawai ya kamata kwamitin Jam'iyya ya "kama" muhimmin aiki a hannu ba, amma kuma dole ne ya "danke shi sosai". Ba a iya rike wani abu sosai, sai tare da an kama shi sosai kada a yi dan sakosako da hannu. Rashin kamawa da karfi kamar kin kamawa ne duka duka. Da ma kome ba ya kamuwa hannuwa a bu-

de. Lokacin da aka rufe hannu, amma ba a matse da ƙarfi ba, kamar an kama wani abu amma cikin gaskiya ba a kama ba. Akwai waɗansu abokanammu masu kama muhimman ayyukan gabansu, amma da ya ke ba su kama su sosai ba, yin aikin kirki na faskararsu. Aiki ba ya yiwuwa sai an kama, haka kuma ba ya yiwuwa idan ba a kama shi sosai ba.

"Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

"A san adadi a zuci". Watau ana nufi cewa dole mu kula da adadin halaye da matsaloli kuma mu yi binciken tushen adadi. Duk ingancin abu na bayyana kansa a cikin ƙayyadadden adadin abin, kuma idan ba adadin babu ingancin. Har yanzu da akwai abokanammu da yawa waɗanda ba su san ya kamata su kula da adadin fannin abubuwa ba, ba su san ya kamata su

kula da digin ƙididdiga da muhimmin kasafi da iyakar adadi mai nuna ingantar abubuwa ba. Ba su san "adadin" kome a zuci ba, kuma da ƙarshe ba za su kiyaye kuskure ba.

"Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

"A Yi Shela ga Jama'a." Ya kamata a sanad da mutane kafin yin taro, watau dai kamar yin "Shela ga Jama'a", domin kowa ya san abin da za a tattauna da kuma irin al'amuran da za a zartar kuma kowa ya shirya tun da wuri. A waɗansu wurare ana kiran taron ma'aikatan hukuma ba tare da an shirya rahoto da kuma ƙudurin shawarar da a ke nufi ba, sai kawai mutane sun iso ne domin taron a ke shirye-shirye, watau dai kamar a ce, "Sojoji da dawaki sun iso, amma ba a shirya abinci da harawa ba", kuma wannan ba shi da kyau. Kada

a yi saurin kiran taro idan ba a ƙarasa shirye-shirye ba.

"Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

"A sami rundunoni kaɗan amma mafiya kyau da kuma saukaƙaƙkiyar hukuma". Maganganu, jawabai, rubuce-rubuce da kudurin shawarwari ya kamata su zamana gajeru masu ma'ana. Kuma bai kamata lokacin taro ya cika tsawo ba.

"Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ku mai da hankali wajen haɗa kai ɗa yin aiki tare da abokanai masu ra'ayi dabam da naku. Dole a mai da hankali kan wannan ko a wurare, ko a cikin rundunar soja. Haka kuma abin ya ke wajen dangantaka da mutanen da su ke ba 'yan Jam'iyya ba ne. Mun zo ne daga ko wane lungu na ƙasa,

kuma ya kamata mu san haɗa kai a wurin aiki ba ma tare da abokanai masu ra'ayi ɗaya da namu kawai ba, amma har da waɗanda ra'ayinsu ya sha bamban da namu.

"Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ku yi ƙoƙarin gudun zaman fariya. Wannan maganar ƙa'ida ce ga duk majagora kuma muhimmin sharaɗi ne wajen rike hadin kai. Ko ma waɗanda ba su yi laifi mai tsanani ba kuma suka samu babbar nasara cikin aikinsu bai kamata su yi alfahari ba.

"Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ku zana iyaka biyu. Na farko, tsakanin tawaye da ƙin tawaye, tsakanin Yenan da Sian. Waɗansu ba su san ya kamata su zana wannan iyaka ba. Misali, lokacin

da su ke la'antar ra'ayin nuna hakimci sai su rika maganar Yenan kamar a nan "ba wani abu nagari", kuma ba su kwatanta ko bambanta tsakanin ra'ayin nuna hakimci a Yenan da ra'ayin nuna hakimci a Sian. Wannan kuskure ne na ainihi. Na biyu, a jerin 'yan tawaye, ya kamata a zana iyaka tsakanin gaskiya da rashin gaskiya, tsakanin nasarori da aibobi, kuma a gane sosai tsakanin biyu din nan wanda ya ke muhimmi da wanda ba muhimmi ba. Misali, nasarorin da aka samu sun kai kashi 30 ko 70 daga kashi dari? Ba a yarda a kaskanta ko a daukaka. Ya kamata mu san kimar aikin mutum, kuma mu san ko nasarorinsa sun kai kashi 30 daga dari ko kuskurensa ya kai 70, ko akasin haka ya faru. Idan nasararorin mutumin nan sun kai kashi 70 a dari ya kamata a amince wa galibin aikinsa. Zai zama kuskure ne da gaske in an dauki aiki wanda a cikinsa nasarori ne muhimmai kamar aiki ne wanda a cikinsa kuskure ne muhimmi. A tinkararmu ga dukan matsa-

loli, kada mu manta zana iyaka biyu: tsakanin tawaye da kin tawaye, kuma tsakanin nasarori da aibobi. Za mu iya tafiyad da abubuwa sosai im mun rike bambancin iyakan nan biyu a hankulammu, idan ba haka ba, za mu yamutsa duk halittar matsaloli. Amma in za a zana iyakan nan biyu sosai, ya wajaba a yi nazari da bincike a cikin nitsuwa. Ya kamata mu dau halin yin nazari da bincike ga ko wane mutum da ko wane al'amari.

"Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

A game da shirye-shiryen kungiyoyi, a tabbatad da zaman dimakuradiyya a karkashin shugabancin tarayya. Ya kamata a yi haka ta wadannan hanyoyi:

(1) Kungiyoyin shugabanci na Jam'iyya ya kamata su ba da gaskantacciyar hanyar jagora, da matsala ta samu ya kamata su sami dabaru domin su kafa kansu kamar cibiyar shugabanci.

(2) Ya kamata manyan ƙungiyoyi su san halin da a ke ciki a ƙananan ƙungiyoyi da kuma rayuwar jama'a, domin su sami hakikanan tushen jagora na gaske.

(3) Kada wata ƙungiyar Jam'iyya ta ko wane mataki ta yi shawarar daidaita matsaloli sama sama. In dai an tsai da shawara, dole a tsaya ga yin aiki da ita sosai.

(4) Duk shawarwarin da manyan ƙungiyoyin Jam'iyya suka tsayar in dai su ne muhimmai, ya kamata nan da nan a sanad da ƙananan ƙungiyoyi da duk mambobin Jam'iyya. ...

(5) Kananan ƙungiyoyi na Jam'iyya da dukan mambobin Jam'iyya, ya kamata sosai da sosai su tattauna umurnan manyan ƙungiyoyi domin su fahimci ma'anarsu sosai kuma su tsara dabarun aikata su.

"Kan Daidaita Ra'ayin Kuskure a cikin Jam'iyya" (Disamba 1929), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

11. HANYAR JAMA'A

Jama'a, sai jama'a kaɗai, su ne ƙarfin ingiza da ƙaga tarihin duniya.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Jama'a su ne jaruman gaske, mu ko wani sa'i ma muna nuna halin yarantaka da jahilci, kuma im ba tare da gane wannan ba, ba ya yiwuwa a sami ilmi ko mafi sauƙi ne.

"Gabatarwa da Karin Bayani ga *Yin Bincike a Kauyuka*" (Maris da Afril 1941), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Karfin kage maras iyaka na tare da jama'a. Suna iya shirya kansu, su dosa wa ko wane wuri, ko wane reshe inda za su iya amfani da karfinsu, suna iya dosan aikin kawo albarka kome fadinsa kome zurfinsa, kuma su kara kaga dimbin abubuwa domin wadatar kansu.

Gabatarwa ga "An Samo Wa Sauran Leburori Hanya" (1955).

Tashen yanzu na harkar manoma, babbar aba ce mai muhimmiyar ma'ana. Cikin dan gajeren lokaci, a lardunan Sin na tsakiya, kudu da arewa, za a ga darurrukan miliyan na manoma sun taso da gaggawa da zafi, sun yi rak, sun gagara kamar hadari da guguwa, kuma ba wani karfi da zai iya tsai da su. Za su tsinka duk malwar bauta, su kama hanyar suncin kai. Za su gina kaburan duk madaulanta, azzalumai jarrababbun yaki, shagwaɓaɓɓun mahukunta da azzaluman kauyuka da miyagun sabbinanai. Za su taga duk jam'iyyun tawaye,

duk abokanai 'yan tawayen turu, su ga wadanne ne za su amince musu kuma wadanne ne ba za su amince musu ba. A shiga gaban manoma ne a ja musu ragama? Ko a tsaya bayansu, ana feleke ana kushe musu? Ko tare musu za a yi domin kinsu? Duk Basinne na da 'yancin zaɓen daya daga cikin hanyoyin nan uku, amma arili zai tilasta kowa ya yi zaɓen nan cikin gaggawa.

"Rahoto kan Binciken Harkar Manoma a Lardin Hunan" (Maris 1927), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

A yanzu dai, tashen rikidar halin zama na harkar gama gwiwa a kauye ya auku a wadansu kauyuka kuma ba da dadewa ba zai barbazu a duk kasar baki daya. Wannan harka ce ta tawayen gurguzu mai fadin gaske wadda ta shafi jama'ar kauye fiye da miliyan 500, kuma tana da babbar ma'ana a kasashen duniya kwarai da gaske. Ya kamata bisa tsari mu ja mata ragama cikin him-

ma da annashuwa, amma ba kokari za mu yi wajen mai da ta baya ba. A irin wannan harka, wadansu goce-goce ba su da makawa, kuma abubuwa ne da za a iya fahimta, kuma babu wuyar daidaita su. Aibobi da kuskuren da ke tare da ma'aikatan hukuma da manoma, za su iya gyara su ko su iya haye musu, idan dai mun taimake su tare da kwazo.

"Kan Al'amarin Gama Gwiwa wajen Noma" (31 ga Yuli, 1955).

Jama'a na da kasaitacciyar sha'awar gurguzu. Wadanda a lokacin tawaye ba su iya kome ba sai bin tsohon sawu, tabbat fahimtar wannan sha'awa zai gagare su. Su makafi ne, ganin duhun kome su ke. Wani gami ma su kan kai ga jirkita abubuwa su mai da gaskiya rashin gaskiya, kuma su dau baki gurbin fari. Ko ba mu sha ganin irin wadannan mutane ba? Wadanda sai dai bin tsohuwar hanya suka sani, kullum sai raina annashuwar jama'a su ke. Da sabon abu ya bullo kullum ba

su amince masa, kai tsaye su ke kiye masa. Daga baya, sai su yarda sun yi kuskure, su dan kushe kansu. Amma a gaba idan wata sabuwa ta samu, sai su sake maimaita tsofaffin halayensu. Haka halinsu ya ke game da duk abu sabo. Irin wadannan mutane kullum a saibance su ke, abada ba su motsawa cikin muhimmin lokaci, kullum bukata su ke sai an ingiza su kafin su yi gaba.

Gabatarwa ga "A Shekaru Biyu Garin Nan Ya Tabbatar Da Hadin Gwiwa wajen Noma" (1955).

Tun fiye da shekaru ashirin ke nan Jam'iyyarmu ke tafe da aiki cikin jama'a ko wace rana, kuma tun fiye da shekarun nan goma kullum tana maganar hanyar jama'a. Kullum mun dage cewa ya kamata tawayen turu ya dogara kan jama'a kuma kowa ya taimaka, muna kin a dogara kan umurnin da wadansu tsirarrun mutane ke bayarwa.

Duk da haka waɗansu abokanai a cikin aikinsu ba su bin hanyar jama'a yadda ya kamata, dangana kawai su ke bisa waɗansu 'yan tsirarrun mutane suna aiki a keɓe. Daya daga dalilai shi ne kome suka yi, sai su ki bayyana wa waɗanda su ke ja wa ragama kuma ba su san yadda za su yalwata hanzari da ƙarfin ƙage na waɗanda su ke ja wa ragama ba. A zuci so su ke kowa ya halarci aiki, amma ba su sanad da mutane da abin da za a yi da kuma yadda za a yi abin ba. Ta wannan hanya, yaya za a zata kowa ya kama aikin gabansa kuma ya yi shi da kyau? Idan ana son daidaita wannan matsala, abin yi da farko shi ne tarbiyyar tunani bisa hanyar jama'a kuma dole a koya wa waɗannan abokanai ɗimbin ƙayyadaddun dabarun aiki.

"Taɗi da Editocin Jaridar Ranarana ta Shansi-Suiyuan" (2 ga Afril, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

Fasahar da muka samu a shekaru ashirin da huɗu na nuna mana cewa duk aiki, manufar siyasa da haliyar aiki na gaskiya, kullum suna dacewa da bukatun jama'a a wani lokaci a wani wuri, kuma suna ƙarfafa cuɗuwarmu da jama'a. Amma duk aiki da manufar siyasa da haliyar aiki na kuskure, kullum ba su dacewa da bukatun jama'a a wani lokaci a wani wuri, kuma suna raba mu da jama'a. Dalilin da ya sa waɗannan cuce-cuce kamar su, "dogamatisanci", "fasahantaka" (empiricism), "umurnintaka", "kanzaganci", "rukunantaka", "ra'ayin nuna hakimci" da halin alfarma wajen aiki, lalle ba su da kyau kuma ba a iya hakuri da su, kuma dalilin da ya sa kowa ya ke da waɗannan cuce-cuce dole ya warkad da kansa shi ne domin suna sa keɓe kai daga jama'a.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Idan ana son haɗuwa da jama'a, ya kamata a yi aiki bisa bukatarsu da muradinsu. Duk aiki na jama'a dole a fara shi daga bukatar jama'a, amma ba daga muradin mutum guda kome kyaun nufinsa ba. Sau da yawa ya kan faru cewa, a hakikanan halaye jama'a na bukatar wani sauyi, amma a zuci ba su da lamirin wannan bukata ko kuma ba su da niyya ko muradin yin wannan sauyi. A wannan hali, ya kamata mu yi haƙurin jira. Ba za mu yi wannan sauyi ba sai bayan aikimmu, idan galibin jama'a sun fahimci bukatar wannan sauyi kuma suna da niyya da muradin yin wannan sauyi. Idan ba haka ba, to kuwa, za a ɓalle kai daga jama'a. Duk aiki mai bukatar jama'a su halarce shi, muddin dai ba su ɗau lamirin yi ko sa niyyar yin wannan aiki ba, to, zai zama harbati kuma ya kawo asara. ... Da akwai ƙa'idodi biyu a nan: ta farko, bukatar gaskiya ta jama'a, ba abin da mu ke tsammani suna bukata ba, ta biyu kuma muradin jama'a waɗanda ya

kamata su ɗau niyya da kansu maimakon mu ɗaura musu niyyar.

"Haɗaɗɗen Goshin Fama a cikin Aikin Al'adu" (30 ga Oktoba, 1944), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ya kamata babban tarommu na wakilai ya yi kira ga duk Jam'iyya wajen ƙara kula, kada dai wani aboki a ko wane matsayi ya ɓalle daga jama'a. Ya kamata a koya wa ko wane aboki ƙaunar jama'a, ya kasa kunnen saurarensu sosai, duk inda ya tafi ya yi cuɗanya da jama'a, ya narku da su, ba ya haye musu ba, ya wayentad da su, ya ta da lamirin siyasarsu sama gwargwadon matsayin lamirinsu, kuma ya taimaka bisa yardarsu su shirya kai da kaɗan-kaɗan kuma a hankali a hankali su kama wajababbun fama da sharuɗan ciki da na waje suka kawo a wani wuri a wani lokaci.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Im mun yi shirin kai farmaki lokacin da jama'a ba su farka ba, lalle wannan zai zama dandintaka. Idan mun nace ga ja wa jama'a ragamar yin wani abu ba da ganin damarsu ba, ba shakka za mu yi asara. Idan mun ki ci gaba lokacin da jama'a ke son ci gaba, wannan zai zama zarafintaka ta Dama.

"Tadi da Editocin Jaridar Ranarana ta Shansi-Suiyuan" (2 ga Afril, 1948), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Hudu.

A duk ko wane aiki, umurnintaka kuskure ne domin ta wuce matsayin lamirin siyasar jama'a kuma ta keta ka'idar ganin damar sa kai na jama'a kuma tana nuna cutar shirin garaje. Bai kamata ba abokanammu su zaci cewa duk abin da suka fahimta, dimbin jama'a ma sun fahimta. Da shiga cikin jama'a ne kawai da kuma yin bincike, za a gane ko sun fahimta kuma a shirye su ke su kama aiki. Im mun yi

haka, za mu kiyaye umurnintaka. A duk ko wane aiki, "kanzaganci" ma kuskure ne domin ya kasa cim ma matsayin lamirin siyasar jama'a, kuma ya keta ka'idar jan ragamar jama'a wajen ci gaba, kuma wannan yana nuna cutar nawa a aiki. Bai kamata ba abokammu su zaci cewa jama'a ba su fahimci abin da su kansu ba su fahimta ba tukuna. Ya kan faru kullum cewa jama'a na shige gabammu su nuna babbar bukatar ci gaba, amma duk da haka abokanammu su kan kasa zaman shugabannin jama'a, su bi bayan wadansu marasa ci gaba, suna nuna ra'ayoyinsu kuma suna daukarsu bisa kuskure kamar na jama'a.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Uku.

A tattara ra'ayoyin jama'a, kana a mai da su ga jama'a kuma a nace ga yin aiki da ra'ayoyi din domin a samu gaskan-

tattun ra'ayoyin shugabanci, wannan shi ne tushen dabarar shugabanci.

"Wasu Maganganu game da Dabarun Shugabanci" (1 ga Yuni, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

A duk hakikanin aiki na Jam'iyyarmu, ya kamata dukan shugabancin gaske "a fara shi daga jama'a, kuma a mayar wa jama'a". Watau ma'anar ita ce a tattara ra'ayoyin jama'a (wadanda su ke a warwatse ba shiryayyu ba) a gama su wuri guda (bayan nazari a gama su kuma a mai da su shiryayyu), sa'idin nan a sake komawa ga jama'a a yi furofaganda a bayyana su sai jama'a sun mai da ra'ayoyi din kamar nasu, sun rike su sosai kuma su yi aiki da su, kana a duba daidaituwar ra'ayoyin nan cikin aikin jama'a. Kuma har ila yau a sake tattara ra'ayoyin jama'a, a sake mayar musu domin a nace ga aikata su sosai. Haka ya

kamata a rika yi har abada, domin ra'ayoyin nan kara gaskantuwa su ke, suna kara rayuwa, suna kara azurtuwa a ko wane lokaci. Wannan shi ne sanin-ka na Marksanci game da ilmi.

"Wasu Maganganu game da Dabarun Shugabanci" (1 ga Yuni, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ya kamata mu je cikin jama'a, mu yi koyi daga gare su, mu takaita fasaharsu domin mu samu shiryayyun ka'idodi da dabaru mafiya kyau, sa'idin nan mu yi furofaganda cikin jama'a, mu yi kira gare su a kan su yi amfani da su wajen daidaita matsalolinsu kuma mu taimake su samun 'yanci da zaman jin dadi.

"Ku Shirya Kanku!" (29 ga Nuwamba, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Da akwai wadansu mutane cikin kungiyoyimmu na shugabanci a wadansu wurare, wadanda ke tsammanin sanin manufofin siyasar Jam'iyya ga shugabannin kawai ya isa, wai babu amfani a bar jama'a su san su. Wannan yana daya daga tushen dalilai da suka sa wasu ayyukammu ba a yi su sosai ba.

"Tadi da Editocin Jaridar Ranarana ta Shansi-Suiyuan" (2 ga Afril, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

A duk harkokin jama'a ya kamata mu yi bincike da kididdiga masu digi domin sanin adadin masu goyon baya, da masu kin goyon baya da 'yan tsaka-tsakiya. Kuma bai kamata ba mu tsai da shawararmu bisa zaton zuci ba tare da wani tushe ba.

"Dabarun Aiki na Kwamitocin Jam'iyya" (13 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Duk inda ke da jama'a, a takaice dai ana iya kasa su gida uku: wadanda ke da zafin nama bisa kwatanci, da wadansu su ke tsaka-tsakiya da wadansu su ke na baya bisa kwatanci. Sabo da haka dole ne shugabanni su gwanance wajen hada 'yan zafin naman nan kuma su mai da su ginshikansu, su dogara kansu domin ta da 'yan tsaka-tsakiya kuma su shawo kan 'yam baya.

"Wasu Maganganu game da Dabarun Shugabanci" (1 ga Yuni, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

A iya mai da manufar siyasar Jam'iyya ta zama aikin jama'a, kuma a iya sa ba wai kawai manyan ma'aikatan hukuma ba amma har da dimbin jama'a su fahimci kuma su sarrafa ko wace harka da ko wace famarmu, wannan fasaha ce ta shugabanci na Marksanci-Leninanci. Kuma wannan iyaka ce

wadda ke nuna mana ko mun yi kuskure ko ba mu yi ba cikin aikimmu.

"Tadi da Editocin Jaridar Ranarana ta Shansi-Suiyuan" (2 ga Afril, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Kome himmar rukunin shugabanci, himmarsa za ta zama ta banza ta wasu tsirarrun mutane, idan dai ba ta cudu da himmar jama'a ba. Haka kuma idan jama'a ce kawai ke da himma, amma ba tare da rukunin shugabanci wanda zai shirya ta yadda ya kamata ba, himmar ba za ta dore ba, balle a ci gaba da ita ta hanyar gaskiya har ta cim ma matsayin koli.

"Wasu Maganganu game da Dabarun Shugabanci" (1 ga Yuni, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ya kamata manyan ma'aikatan hukuma su rika mai da hankali kullum ga aikin kawo albarka na jama'a, abubuwan moriyarsu, fasaharsu da irin jinsu.

Rubuta Wasu Maganganu domin Nunin Kayayyakin Albarkar Da Kungiyoyi Wadanda Kai Tsaye Ke Karkashin Kwamitin Tsakiya na Jam'iyya da Babbar Hedkwatar Rundunar Hanya ta Takwas Suka Shirya (24 ga Nuwamba, 1943).

Ya kamata mu kai nitsattsiyar kula ga al'amura wadanda suka shafi rayuwar jama'a, daga sha'anin gona da aiki har zuwa ga ba da kiraren wuta, shinkafa, mai da gishiri. ... Duk wadannan sha'anoni da suka shafi rayuwar jama'a, ya kamata mu gabatar da su a ajendarmu. Ya kamata mu tattauna su, mu tsai da shawara, mu aikata su kuma mu duba yadda aikin ke tafiya. Ya kamata a sanad da jama'a cewa mu masu

tsare abubuwan moriyarsu ne, numfashi iri ɗaya mu ke da su. Ya kamata mu taimake su su fara daga waɗannan abubuwa, su fahimci waɗansu ayyuka mafiya daraja da muka gabatar, watau ayyukan yaƙin tawayen turu, domin su goyi bayan tawaye, su yaɗa shi a dukan ƙasar, su amsa kirarmu ta siyasa, su yi fama har nasarar ƙarshe ta tawayen turu.

"A Lura Da Zaman Jama'a, A Maida Hankali ga Dabarun Aiki" (27 ga Janairu, 1934), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Farko.

12. AIKIN SIYASA

A rundunar soja aka taɓa kafa (Lokacin Yaƙin Basasar Tawaye na Farko daga 1924-1927—wannan bayani na mai shirya littafin ne) tsarin wakilan Jam'iyya da na yankin siyasa, wanda ba a taɓa saninsa ba a tarihin Sin, kuma bisa dogara kan wannan tsari ne aka sauya wa runduna sabuwar kama sosai. Jar Rundunar Soja wadda aka kafa ta a 1927, wadda yau ita ce Rundunar Hanya ta Takwas ta gaji wannan tsari kuma ta yalwata shi.

"Ganawa Da dan Jarida na Ingila James Bertram" (25 ga Oktoba, 1937), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Biyu.

Bisa dogara kan yaƙin jama'a da ƙa'idodin haɗa kai tsakanin runduna da jama'a, tsakanin hafsoshi da ƙananan sojoji kuma da lalata ayarin sojan maƙiya ne, Rundunar Sunce Jama'a ta kafa gawurtaccen aikin siyasarta na tawaye, wannan shi ne muhimmin dalilin nasararmu bisa maƙiya.

"Halin Da A Ke ciki Yanzu da Ayyukan Gabammu" (25 ga Disamba, 1947), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

Wannan runduna ta kafa tsarin aikin siyasa wanda ya wajaba ga yaƙin jama'a, kuma aikin tsari ne yin ƙokarin kawo haɗin kai cikin rundunarmu, haɗin kai da rundunar aminai kuma da haɗin kai da jama'a da lalata ayarin sojan maƙiya da tabbatar da nasara a cikin faɗa.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Aikin siyasa shi ne ran duk aikimmu ta wajen tsimi. Wannan gaskiya ce musamman a lokacin da a ke muhimmin sauyi na tsarin halin zama da tsimi.

Gabatarwa ga "Darasi Mai Tsanani" (1955).

"Reshen Jam'iyya an shirya shi bisa tushen kamfanin soja", wannan shi ne ɗaya daga cikin muhimman dalilai da ya sa Jar Rundunar Soja ta iya mawuyacin faɗa ba tare da rugurgujewa ba.

"Fama a Duwatsun Chingkang" (25 ga Nuwamba, 1928), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Aikin siyasa na Rundunar Hanya ta Takwas ya dogara ne bisa ƙa'idodi uku na digi. Ta farko ita ce ta haɗin kai tsakanin hafsoshi da ƙananan sojoji watau a kau da mulkin gargajiya cikin runduna, a hana tsarin duka da zagi, a kafa tsarin yin biyayya a cikin lamiri kuma a yi zaman raba daɗi da wuya

tare — wannan ya kawo hadin kai sosai cikin runduna. Ta biyu ita ce gama kai tsakanin runduna da jama'a, watau tana haramta ɓata ko da 'yar kwayar zarrar abubuwan moriyar jama'a kuma runduna ta yi furofaganda tsakanin jama'a, ta shirya su, ta yi musu damara, ta saukaka musu nauyin fatara kuma ta danne maciyan amanan kasa da masu yi wa jama'a da runduna ɓarna. Ta haka ne runduna ta cudu da jama'a kuma ko ina tana samun maraba. Ta uku ita ce ta lalata karfin ayarin sojan makiya da nuna afuwa ga 'yan fursunan yaki. Nasararmu ba kawai kan fadan rundunarmu ta dogara ba amma har da lalata karfin ayarin sojan makiya.

"Ganawa Da dan Jarida na Ingila James Bertram" (25 ga Oktoba, 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Dole rundunar sojojimmu ta yi biyayya ga gaskantattun ka'idodi wajen cudanya

tsakanin soja da jama'a, tsakanin soja da gwamnati, tsakanin soja da Jam'iyya, tsakanin hafsoshi da kananan sojoji da tsakanin aikin soja da aikin siyasa kuma da cudanya tsakanin ma'aikatan hukuma. Ko kusa kada ta kuskura ta yi laifin zaluncin jarrabawun yaki (warlordism). Dole hafsoshi su so kananan sojoji, kada su nuna kamar ba ruwansu da rayuwar kananan sojoji ko su nuna musu azaba. Dole runduna ta so jama'a, kada ta taɓa abubuwan moriyar jama'a. Dole rundunar soja ta girmama gwamnati da Jam'iyya, kada ta ce tana son ""yancin kanta".

"Ku Shirya Kanku!" (29 ga Nuwamba, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Manufar siyasarmu ta game da 'yam fursunoni wadanda aka kama daga rundunar Japan ko daga munafukan ayari ko daga rundunar kin Kwaminis, ita ce a sake su amma ban da wadanda jama'a ke

nuna wa matsananciyar ƙiyayya kuma dole a kashe su kuma waɗanda manyan mahukunta sun tabbatad da hukuncin kisa a kansu. A tsakanin fursunoni waɗanda aka tilasta suka shiga sojan azzalumai kuma waɗanda suka nuna ɗan son tawaye, ya kamata a shawo hankalin yawancinsu domin su yi wa rundunar sojammu aiki, sauran kuwa a sake su. Idan sun sake faɗa da mu, aka sake kama su sai a sake su. Kada mu ce za mu wulakantad da su, mu ƙwace halaliyarsu ko kuma mu tilasta su tuba, amma dukansu ya kamata mu nuna musu gaskiya mu sake musu fuska. Kome zaluncinsu wannan manufar siyasarmu ce gare su. Hanya ce sosai ta kaɗaita sansanin azzalumai ke nan.

"Kan Tsarin Manufar Siyasa" (25 ga Disamba, 1940), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Makami muhimmin abu ne a yaƙi, amma ba shi ne mai ƙudura yaƙi ba. Mutum

shi ne mai ƙudura yaƙi ba abubuwa ba. Gasar nuna ƙarfi ba gasa ce kawai ta ƙarfin soja da na tsimi ba, amma kuma gasa ce ta nuna ƙarfin mutum da irin ƙarfin halin da jama'a ke nunawa. Mutum ne mai sarrafa ƙarfin soja da na tsimi.

"Kan Yaƙi cikin Dogon Lokaci" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Bom ɗin atom damishin takarda ne wanda azzalumai Amirkawa ke amfani da shi domin firgita mutane. Yana da kamannun ban tsoro, amma a gaske ba ya da shi. Ba shakka, bom ɗin atom makami ne wanda zai iya kisan gaske, amma jama'a ce mai iya ƙudura ƙarshen yaƙi ba ɗaya ko biyu daga cikin sababbin makamai ba.

"Tadi tare da Anna Louise Strong 'yar Jarida ta Amirka" (Agusta 1946), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Tushen runduna shi ne sojoji, idan ba a yi wa runduna tarbiyya ta ra'ayin siyasar ci gaba ba, idan ba a tafiyar da wannan tarbiyya da aikin siyasar ci gaba ba, ba za a iya samun hadin kan gaskiya ba tsakanin hafsoshi da kananan sojoji kuma ba ya yiwuwa a ta da iyakacin himmarsu a Yakin Kare Hari, kuma ba ya yiwuwa a ba da digi mafi kyau domin amfani sosai da nakaltar fanni da dabarun yaki.

"Kan Yaki cikin Dogon Lokaci" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ra'ayin zalla na soja ya bazu kwarai a tsakanin wadansu abokanai a Jar Rundunar Soja. Ga abin da ra'ayin ke nunawa:

(1) Wadannan abokanai sun dauki sha'anin soja da na siyasa kamar sun saba wa juna ne, kuma sun ki yarda cewa sha'anin soja daya ne kawai daga cikin hanyoyin cika dawainiyar siyasa. Har wadansu suna jaddadawa cewa, "Idan kome ya yi kyau ta

fannin soja, ba shakka ya yi kyau ta fannin siyasa. Idan ya baci ta fannin soja, ba zai yi kyau ta fannin siyasa ba." Wannan zuwa nesa ne har ma a ce sha'anin soja na jan ragamar sha'anin siyasa.

.....

"Kan Daidaita Ra'ayin Kuskure a cikin Jam'iyya" (Disamba 1929), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Sarrafa tarbiyyar tunani muhimmiyar gaba ce wajen hada kan dukan Jam'iyya domin yin manyan fama na siyasa. Idan ba a yi wannan tarbiyya ba, Jam'iyya ba za ta iya cika dukan ayyukanta na siyasa ba.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

A kwanakin nan, aikin tunani da na siyasa a tsakanin 'yan ilmi da dalibai ya dan raunana, har ma wadansu munanan goce-goce sun bullo. A ganin wadansu mutane kamar bai bukaci a kai kula ga siyasa da goben

kasarsu da burin dan Adam ba. A ganinsu Marksanci ya yi tashe na dan lokaci, amma yanzu kwarjininsa ya ragu. Tun da ya ke haka ne, ya kamata yanzu mu karfafa aikimmu na tunani da na siyasa. Ya kamata da 'yan ilmi da dalibai duka su himmantu wajen nazari. Ban da nazarinsu wajen gwanancewa a wasu ayyukan musamman, ya kamata su sami ci gaba a fannin tunani da siyasa, don haka ya bukaci su nazarci Marksanci da al'amuran siyasa da al'amuran yau da kullum. Idan ba a da gaskantaccen ra'ayin siyasa, kamar ba a da kurwa ne. ... Duk ofisoshi da kungiyoyi ya kamata su dau nauyin aikin tunani da na siyasa. Kuma wannan dawainiya ta wajaba ga Jam'iyyar Kwaminis, ga Kungiyar Samari da kungiyoyin gwamnati wadanda kai tsaye abin ya shafe su, musamman ma ga darektocin makarantu da malamai.

"Game da Hanyar Daidaita Saɓani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Bayan an yi wa sojojin Jar Rundunar Soja tarbiyyar siyasa, sai suka fahimci ma'anar aji kuma suka sami ilmi game da rarraba ganduna da kafa mulki da yi wa ma'aikata da manoma damara da dai sauransu. Kuma dukansu sun gane suna fama domin kansu, domin ajin ma'aikata da manoma. Sabo da haka ne su ke jure wa wahaloli cikin fama ba tare da kuka ba. Ko wane kamfani ko bataliya ko rejimanti na da kwamitin sojoji wanda ke wakiltar abubuwan moriyar sojoji kuma yana tafiyad da aikin siyasa da aikin jama'a.

"Fama a Duwatsun Chingkang" (25 ga Nuwamba, 1928), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Tafiyad da harka ta bayyana koke-koke cikin gaskiya (watau tone azabar da azzalumai da tsohon zama suka nuna wa jama'a talakawa) da ta bincike a fannoni uku (wa-

tau binciken aji, binciken yadda ake aiki da binciken niyyar fada) ya kara ta da lamirin siyasar hafsoshi da kananan sojoji na dukan runduna cikin famarsu ta neman 'yanta jama'a talakawa zambatattu domin raba ganduna a duk kasar da kuma hallaka makiyan jama'a gaba daya, tarkacen Chiang Kai-shek. Kuma ya kara karfafa hadin kai mai kwari na dukan hafsoshi da kananan sojoji a karkashin shugabancin Jam'iyyar Kwaminis. Bisa wannan digi ne runduna ta kara tsabtata kanta, ta inganta biyayya, ta kara inganta babbar harkar jama'a wajen horon sojoji, ta kara yalwata dimakuradiyya wajen siyasa, tsimi da sha'anin soja bisa cikakken shugabanci da tsari nagari. Sabo da haka rundunar ta gama kai ta zama kamar mutum daya, kowa da kowa na kawo ra'ayinsa da karfinsa. Rundunar ba ta jin tsoron sadakad da rai, tana iya haye dukan wahaloli na rashin kayan aiki, kuma tana nuna jaruntakar tarayya da karfin hali wajen hallaka

makiya. Irin wannan runduna gagararriya ce.

> "Bayani game da Babbar Nasarar Da Aka Ci a Arewa Maso Yamma da Kuma Wata Irin Sabuwar Harkar Tarbiyyar Tunani a Rundunar Sunce Jama'a" (7 ga Maris, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

A 'yan watannin nan da suka wuce, kusan dukan Rundunar Sunce Jama'a ta yi amfani da lokacin shakatawa tsakanin fada domin tafiyad da babban aikin horo da karfafawa. Wannan aiki an yi shi ne a karkashin cikakkiyar ragamar kirki, cikin tsari kuma ta hanyar dimakuradiyya. A nan ne aka ta da himmar tawayen dukan hafsoshi da kananan sojoji, kuma an sa sun gane a fili manufar yaki, an kau da wasu miyagun nufi ta wajen tunani da wasu take-taken banza da suka bayyana cikin runduna, an yi tarbiyyar ma'aikatan hukuma da sojoji kuma an kara karfin fadan runduna kwarai.

Daga yanzu ya kamata mu ci gaba da irin wannan harkar tarbiyyar tunani a cikin runduna, watau harkar jama'a mai dimaku-radiyya da sabon salo.

"Jawabi a Taron Ma'aikatan Hukuma a 'Yantacciyar Jihar Shan-si-Suiyuan" (1 ga Afril, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Manufar ba da ilmi ta Kolejin Soja da Siyasa na Kin Japan ita ce a samo tsayayyiyar hanyar siyasa ta gaskiya da haliyar aiki mai tanadi da sauki da sihirin shirin yaki da dabarun yaki masu laudi. Wadannan ne wajababbun abubuwa uku wajen samun soja dan tawaye a yakin kin Japan. Bisa wadannan wajababbun abubuwa uku ne ma'aikatan kolejin da malamai da dalibai ke aiki da koyo.

"Abu Mai Kyau Ne Ba Mugu Ba Ne ga Makiyi Ya Zarge Ka" (26 ga Mayu, 1939) .

Tun asali al'ummarmu tana da halin yin fama mai daci, ya kamata mu yalwata wannan hali. ... Tun asali ma kullum Jam'iyyar Kwaminis tana ba da shawarar bin tsayayyiyar hanyar siyasa ta gaskiya. ... Wannan hanya ba ta rabuwa da halin yin fama mai daci. Idan ba tsayayyiyar hanyar siyasa ta gaskiya, ba ya yiwuwa a ta da halin yin fama mai daci. Kuma idan babu halin yin fama mai daci, ba ya yiwuwa a rike tsayayyiyar hanyar siyasa ta gaske.

"Jawabi a Babban Taro a Yenan don Bikin Sallar Ma'aikatan Duniya" (1 ga Mayu, 1939).

Ku hada kai, ku himmantu, ku nitsu, ku rika fara'a.

Taken Kolejin Soja da Siyasa na Kin Japan.

Muhimmin abu a duniya shi ne "mai da hankali", kuma shi ne abin da Jam'iyyar Kwaminis ta fi girmamawa.

Ganawa Da Dalibai Sinnawa da 'yan Kos a Mosko (17 ga Nuwamba, 1957).

13. DANGANTAKA TSAKANIN HAFSOSHI DA SOJOJI

Kullum rundunarmu tana da manufofin siyasa biyu. Na farko, kada mu ji tausayin makiyi, mu take shi, mu hallaka shi. Na biyu, ya kamata mu nuna alheri ga namu, ga jama'a, ga abokanammu, ga manyammu da na baya da mu, kuma mu hada kai da su.

Jawabi a Liyafar Da Kwamitin Tsakiya na Jam'iyya Ya Shirya don Wakilai Masu Nazari da Kyau daga Rejimantocin Tsaro (18 ga Satumba, 1944).

Mun zo ne daga ko wane lungun kasa kuma buri daya na tawaye ya hada mu. ...

Ya kamata ma'aikatan hukuma su rika kula da ko wane soja, kuma duk mutanen da ke cikin jerin tawaye ya kamata su rika kula da juna, su so juna, su taimaki juna.

"Bautawa Jama'a" (8 ga Satumba, 1944), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Uku.

A ko wane rukunin runduna, ya kamata a ta da harkar goyon bayan ma'aikatan hukuma da son sojoji, kuma a yi kira ga ma'aikatan hukuma su so sojoji, sojoji kuwa su goyi bayan ma'aikatan hukuma. Ya kamata su gaya wa juna aibobinsu da kuskurensu, su gyara su da wuri. Ta haka ne za su cim ma burin hadin kan gaske a jerinsu.

"Ayyukan 1945" (15 ga Disamba, 1944).

Dimbin mutane suna zaton cewa munanan dabaru ke ßata dangantaka tsakanin

hafsoshi da kananan sojoji kuma tsakanin runduna da jama'a, amma kullum ina fada musu cewa wannan maganar digin hali ce (ko digin ka'ida ce), kuma hali ne na girmama sojoji da jama'a. Daga wannan hali ne a ke samun manufofin siyasa, dabaru da kamannu iri iri. Idan an goce wa wannan hali, tabbat wadannan manufofin siyasa, dabaru da kuma kamannu ba za su yi daidai ba, kuma ko kadan ba mai yiwuwa ba ne cewa za a samu dangantakar arziki tsakanin hafsoshi da kananan sojoji kuma tsakanin runduna da jama'a. Manyan ka'idodi uku na aikin siyasa a cikin rundunar soja su ne: ta farko, hadin kai tsakanin hafsoshi da kananan sojoji, ta biyu, hadin kai tsakanin runduna da jama'a, ta uku, lalata karfin ayarin sojan makiyi. Domin aikata wadannan ka'idodi sosai, tilas sai a fara daga digin hali na girmama sojoji da jama'a, da kuma girmama mutuncin 'yam fursunan yaki wadanda suka ajiye makamansu. Wadanda ke zato ba maganar digin hali ce ba amma ta

nakaltar fanni ce, lalle sun yi kuskure kuma ya kamata su gyara kuskurensu.

"Kan Yaki cikin Dogon Lokaci" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Lokacin da 'yan Kwaminis su ke aiki tsakanin jama'a talakawa, ya kamata su yi amfani da hanyar dimakuradiyya ta lallashi da tarbiyya, kuma ko kadan kada su yi amfani da umurnintaka ko hanyar karfi. Jam'iyyar Kwaminis ta Sin tana biyayya sosai ga wannan ka'ida ta Marksanci-Leninanci.

"Game da Hanyar Daidaita Saɓani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Dole ne abokanammu su fahimci cewa aikin sauya tunani aiki ne mai bukatar dogon lokaci, tilas sai da hakuri da nitsuwa, kada a yi tsammanin 'yan darasuna da shawarwari suna iya sauya tunanin jama'a wanda ya zaunu a zukatansu tun shekaru gommai. Ba a iya shawo hankalinsu sai tare da lallashi, amma ba tare da karfi ba. Shawo hankalinsu da karfi ba abu ne mai yiwuwa ba. Wannan dabara ta iya aikatuwa ga makiya, amma ko kusa ba ga abokanai ko ga aminai ba.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

Ya kamata mu yi bambancin gaske tsakanimmu da makiya, kada mu dau matsayin gaba ga abokanammu, kada mu nuna musu halin da za mu nuna wa makiya. Wajen yin magana ya kamata mu nuna cikakken halin sha'awar tsare sha'anin jama'a da ta da matsayin lamirin siyasarsu, amma kada mu yi musu dariya ko suka.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

14. DANGANTAKA TSAKANIN RUNDUNAR SOJA DA JAMA'A

Ya kamata runduna ta cudu da jama'a su zama daya domin ta haka jama'a ta ga rundunar tata ce. Irin wannan runduna za ta zama gagararra, ...

"Kan Yaki cikin Dogon Lokaci" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ya kamata a fahimtad da ko wane aboki cewa muddin dai muna dogara kan jama'a, muna amince wa karfin kagensu maras iyaka sosai kuma muna ba su gaskiya, muna cuduwa da su, za mu iya haye ko wace

wahala, kuma ba makiyin da zai iya haye mu, amma mu za mu iya haye ko wane makiyi.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Duk inda abokanammu suka je, ya kamata su kafa kyakkyawar dangantaka da jama'a, su nuna musu kula kuma su taimaka musu haye wahalolinsu. Ya kamata mu hada kai da dimbin jama'a, kuma gwargwadon yawansu gwargwadon kyaun harkarmu.

"Kan Shawarwarin Chungking" (17 ga Oktoba, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

A Suntattun Wurare, ya kamata runduna ta yi aikin goyon bayan gwamnati da na son jama'a, kuma ya kamata gwamnatin dimakuradiyya ta shiga gaban jama'a wajen aikin goyon bayan runduna, kuma wajen

fin kiyaye iyalin sojojin da ke kare harin Japan. Ta haka, za a ƙara kyautata dangantaka tsakanin runduna da jama'a.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ya kamata a runduna mu yi wa hafsoshi da ƙananan sojoji tarbiyyar tunani domin su fahimci muhimmancin goyon bayan gwamnati da ƙaunar jama'a sosai. Idan dai runduna da kanta ta aikata wannan dawainiya sosai, hukumar wuri da jama'a za su kyautata dangantakarsu da runduna.

"Manufar Aiki ta 1946 a Suntattun Wurare" (15 ga Disamba, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

A yayin wadannan kamfen biyu, watau na "goyon bayan gwamnati da son jama'a" da "goyon bayan runduna da kula da iyalin sojojin da ke kare harin Japan", runduna da Jam'iyya da gwamnati ya

kamata ko waccensu ta bincika aibobinta da kuskurenta na 1943 sosai, kuma ta tsaya ta gyara su a cikin 1944. Daga yau a ko wane farkon tsayuwar wata na ko wace sabuwar shekara, ya kamata a ta da irin wadannan kamfen a ko ina kuma a yayin yinsu a rika karanta alkawuran nan biyu, watau "goyon bayan gwamnati da son jama'a" da kuma "goyon bayan runduna da kiyaye iyalin sojojin da ke kare harin Japan", kuma ya kamata a rika kushe wa kai a gaban jama'a game da laifin runduna ga Jam'iyya ko ga gwamnati ko ga jama'a a wuraren sansani ko kuma game da ko wane rashin kula na Jam'iyya ko gwamnati ko jama'a ga runduna (ko wane gefe ya kushe wa kansa ba wani ba) domin a gyara aibobi da kuskure duka sosai.

"Ruwaita Kamfen din Rage Bashi, Kara Albarka da Kuma 'Goyon Bayan Gwamnati da Son Jama'a' a Sansani" (1 ga Oktoba, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

15. DIMAKURADIYYA A MANYAN FANNONI UKU

Ya kamata a tabbatad da gwargwadon dimakuradiyya a runduna, muhimmin abin yi shi ne a kau da tsarin duka da zagi na mulkin gargajiya, kuma hafsoshi da kananan sojoji su raba dadi da wuya a zamansu. Ta haka za mu iya cim ma burin hadin kai tsakanin hafsoshi da kananan sojoji, rundunar za ta kara karfin fada kwarai kuma ba za mu yi shakkar cewa ko ma iya dagewa kan tsanantaccen yaki mai dogon lokaci ba.

"Kan Yaki cikin Dogon Lokaci" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ban da aikin da Jam'iyya ta yi, dalilin da ya sa Jar Rundunar Soja ta ke iya nace wa aikinta duk da tsananin halin zama da yawan yake-yake, shi ne aikata dimakuradiyya a rundunar. Hafsoshi ba su bugun kananan sojoji, da hafsoshi da kananan sojoji suna moriya da irin sharadi mai daraja daya, kananan sojoji suna da 'yancin yin taro da magana, an soke kananan tsabi'o'i marasa amfani, sha'anin kudi na tafiya tare da sani da jin kowa. ... Ba kawai jama'a ke bukatar dimakuradiyya ba a Sin, har ma rundunar soja na bukatarta. Tsarin dimakuradiyya a runduna muhimmin makami ne wajen wargaje duk rundunar haya ta mulkin gargajiya.

"Fama a Duwatsun Chingkang" (25 ga Nuwamba, 1928), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Manufar aikin siyasa cikin rundunarmu ita ce a ta da sojoji kanana tsaye da kwamandodi da dukan ma'aikatan runduna,

domin cim ma manyan buri uku ta harkar dimakuradiyya a karkashin hadadden shugabanci, watau su ne: babban hadin kai wajen siyasa da kyautata halayen rayuwa kuma da kara gyara nakalta da dabarun yaki a sojance. "Bincike a Fannoni Uku" da "Gyara a Fannoni Uku" da yanzu a ke tafiyar da su da sha'awa a rundunarmu, ana son su cim ma buri biyu na farko daga burin nan uku tare da dabarun dimakuradiyya ta wajen siyasa da tsimi.

Game da dimakuradiyya wadda ta shafi tsimi, wakilan sojoji ya kamata su samu hujjar taimakon shugaban kamfani (amma kar su wuce gona da iri) wajen abubuwan da ake kawowa da abincin kamfani.

Game da dimakuradiyyar da ta shafi soja, a lokacin horo dole hafsoshi da kananan sojoji su koyad da juna, haka kuma tsakanin sojojin su-ya-su. A lokacin fada kamfanonin da ke fagen fama ya kamata su rika taro iri iri manya ko kanana. A karkashin ragamar shugaban kamfani, ya kamata

a ta da sojoji su rika shawarar yadda a ke kai hari da kwace matsayin makiyi da kuma yadda ake cika sauran ayyukan fada. Lokacin da aka ci gaba da fama har 'yan kwanaki, ya kamata a yi irin wadannan shawarwari. Irin wannan dimakuradiyyar soja an aikata ta a lokacin fadan Panlung a arewacin lardin Shensi da kuma a fadan Shihchiachuang a jihar Shansi-Chahar-Hopei, kuma an samu babbar nasara. Aikata haka ya nuna cewa abu ne mai albarka, babu hasara ko kadan.

"Harkar Dimakuradiyya cikin Rundunar Soja" (30 ga Janairu, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

A cikin babbar fama da ta ke yi yanzu, Jam'iyyar Kwaminis ta Sin tana rokon duk kungiyoyin shugabancinta da duk mambobinta da ma'aikatanta su ta da iyakacin himmarsu, domin ta haka ne kawai za a iya cin nasara. Abin da a ke nufi da

wannan himma, shi ne ƙungiyoyin shugabanci da ma'aikatan hukuma da dukan 'yan Jam'iyya ya kamata su nuna ta a basirarsu ta ƙage a aiki, kuma su nuna ta cikin halinsu na ɗaukar ɗawainiya, a cikin ƙwazon da su ke nunawa a aikinsu, a cikin ƙarfin halinsu wajen iya tambayoyi, wajen faɗin ra'ayoyinsu da sukar aibobi da kuma cikin duba aikin ƙungiyoyin shugabanci da manyan ma'aikata cikin lumana. Idan ba haka ba, wannan "himma" za ta zama ta banza. Amma yalwata wannan himma ya danganta ga yaɗa dimaƙuraɗiyya a Jam'iyya. Ba za a iya cim ma burin ta da himma ba, idan ba tare da isasshiyar dimaƙuraɗiyya a Jam'iyya ba. Haka ma ba za a iya shirya ɗimbin cancantattun mutane ba sai tare da gudanad da zaman dimaƙuraɗiyya a Jam'iyya.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yaƙin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ya kamata a bar kowa ya yi magana, ko wane ne shi, muddin ɗai shi ba magauci ba ne ƙuma ba muguwar suka zai yi ba, kuma ba kome ko da kuskure ne. Hakki ne ga duk shugabanni kome matsayinsu su saurari sauran mutane. Ya kamata a tafiyar da ƙa'idodin nan biyu: (1) Ka faɗi duk abin da ka sani, kada ka ɓoye kome. (2) Mai magana ba shi da laifi, ya kamata masaurari ya mai da maganganun kamar gargaɗi. Idan ɗai ba a tafiyar da ƙa'idar "Mai magana ba shi da laifi" da gaske kuma ba cikin ƙarya ba, ƙarshen abin ba zai zama "Ka faɗi duk abin da ka sani, kada ka ɓoye kome" ba.

"Ayyukan 1945" (15 ga Disamba, 1944).

Ya kamata a yi tarbiyyar dimaƙuraɗiyya cikin Jam'iyya domin mambobinta su fahimci mene ne zaman dimaƙuraɗiyya a Jam'iyya, mene ne dangantaka tsakanin dimaƙuraɗiyya da tattarawa (centralism)

da kuma yadda a ke tafiyar da dimakuradiyya-tattarawa. Ta haka kawai za a iya fadada dimakuradiyya a gaske cikin Jam'iyya, kuma a kiyaye dimakuradiyyar hauka (ultra-democracy) da sake mai lalata biyayya.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ko a runduna ko a kungiyoyin wuri, dimakuradiyya cikin Jam'iyya ya kamata a yi amfani da ita domin karfafa biyayya da kara karfin fada amma ba raunana su ba.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ta fannin tsarin sanin-ka, ya kamata a kashe saiwar dimakuradiyyar hauka. Da farko dai ya kamata a nuna hadarin dimakuradiyyar hauka domin tana raunana har ma tana ßata kungiyoyin Jam'iyya kwata

kwata, tana raunana har ma tana lalata bajimtakar Jam'iyya wajen fada, tana hana Jam'iyya cika ayyukanta na fada, har ma tana jawo asara ga tawaye. Na biyu, ya kamata a nuna asalin dimakuradiyyar hauka na daga kin biyayya na kananan tajirai. Idan dai an kawo wannan hali cikin Jam'iyya zai zama ra'ayin dimakuradiyyar hauka a fannin siyasa da fannin shirye-shirye. Wannan ra'ayi ko kusa bai dace da dawainiyar famar talakawa ba.

"Kan Daidaita Ra'ayin Kuskure a cikin Jam'iyya" (Disamba 1929), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

16. TARBIYYA DA HORON SOJOJI

Ya kamata manufarmu ta tarbiyya ta ba masu samunta damar shirya kansu wajen hali, ilmi da lafiyar jiki domin su zama ma'aikata masu lamirin gurguzu da ilmi.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Game da tarbiyya ga ma'aikatan hukuma ko a wurin aiki ko a makarantun ma'aikatan hukuma ya kamata a kafa manufar siyasa ta mai da irin wannan tarbiyya kan nazarin ainihin matsalolin tawayen Sin da kuma amfani da tushen ka'idodin Mark-

sanci-Leninanci kamar ja gora, kuma ya kamata a bar nazarin Marksanci-Leninanci ta kaɗaitacciyar hanya wadda kuma a kafe ta ke.

"Kyautata Nazarimmu" (Mayu 1941), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ga wata makarantar soja, sha'anin mafi muhimmanci shi ne zaben direkta da malaman koyarwa da shirya manufar tarbiyya.

"Matsalolin Sihirin Shiri a Yakin Tawayen Sin" (Disamba 1936), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

A makaranta mai mutane dari, ba za a iya tafiyad da sha'aninta sosai ba, idan ba a sami kungiyar shugabanci ta mutane kadan ko fiye da goma ba, wadda aka kafa ta bisa halayen da a ke ciki sosai (ba wai kawai a gama su hakanan ba), kuma kungiyar ta kasance tana da malamai, sauran

akawuna da ɗalibai mafiya zafin nama, tsayayyu da mafiya basira.

"Wasu Maganganu game da Dabarun Shugabanci" (1 ga Yuni, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ya kamata duk hafsoshi da ƙananan sojoji na rundunarmu su inganta kai wajen fasaharsu ta yaki, su mike da ƙwazo su ci gaba a yaki inda nasararmu tabbat ce, kuma kai tsaye su hallaka dukan makiyammu kwata-kwata.

"Sanarwar Rundunar Sunce Jama'ar Sin" (Oktoba 1947), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Shirin gina ƙarfi da horo na shekara guda a fannin soja da siyasa wanda aka fara yanzu, ya kamata a ba su daraja ɗaya kuma a haɗa su. Da farko, ya kamata a fi ba da ƙarfi kan fannin siyasa, kan kyautata dangantaka tsakanin hafsoshi da ƙa-

nanan sojoji, a ƙarfafa haɗin kai na ciki kuma a ta da muzakkarancin jama'a ma'aikatammu da mayaka. Sai ta haka ne kawai za a iya gina ƙarfi da horo na yaki ba tare da wuya ba kuma a samu kyakkyawar nasara.

"Ayyukan 1945" (15 ga Disamba, 1944).

Game da dabarun horon sojoji, ya kamata mu yalwata babbar harka inda hafsoshi za su koyad da ƙananan sojoji, ƙananan sojoji su koyad da hafsoshi, kuma ƙananan sojoji su koyad da juna.

"Manufar Aiki ta 1946 a Suntattun Wurare" (15 ga Disamba, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Kirarmu ga kowa ta horon sojoji ita ce: "Hafsoshi su koyad da ƙananan sojoji, ƙananan sojoji su koyad da hafsoshi kuma ƙananan sojoji su koyad da juna". Maya-

kammu na da fasahar aikatawa ta fada da yawa. Ya kamata hafsoshi su yi koyo daga mayaka, kuma idan sun mai da fasahar wadansu kamar tasu, za su kara zama gogaggu.

"Tadi da Editocin Jaridar Ranarana ta Shansi-Suiyuan" (2 ga Afril, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Game da abubuwan da suka shafi horon sojoji, burimmu na farko shi ne mu kara gwaninta a harbi, fada da banati, da jifan gurned da sauransu, na biyu, a kara dabarar yaki, musamman a ba yakin dare muhimmiyar daraja.

"Manufar Aiki ta 1946 a Suntattun Wurare" (15 ga Disamba, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

17. BAUTAWA JAMA'A

Dole mu zama kamilai, masu hankali, mu kiyaye kammu daga alfarma da kaudi, kuma mu bauta wa jama'ar Sin da zuciya daya, ...

"Kaddarori Biyu na Sin" (23 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Masomimmu shi ne bauta wa jama'a da zuciya daya kuma ko da dan lokaci, kada mu nisanci jama'a, mu fara kome daga bukatun jama'a ba daga bukatar son zuci na wani ko bukatar wata karamar kungiya ba, kuma mu mai da dawainiyarmu ga jama'a

tare da ɗawainiyarmu ga ƙungiyoyin shugabanci na Jam'iyya kamar abu guda.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ofisoshin mulkin ƙasa dole su aikata dimakuraɗiyya-tattarawa, dole su dogara kan jama'a kuma dole ne ma'aikatansu su bauta wa jama'a.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Halin Aboki Bethune na bauta wa wasu sosai ba tare da wani son kai ko kaɗan ba, ya bayyanu a cikin cikakkiyar lurarsa ga aikinsa da kuma cikakkiyar soyayyarsa ga abokanai da jama'a. Ya kamata ko wane ɗan Kwaminis ya yi koyi da shi.

. . . . . .

Dole dukammu mu koyi halin rashin son zuci daga gare shi. Da irin wannan hali kowa zai zama mai amfani ƙwarai ga

jama'a. Iyawar mutum za ta zamana babba ce ko ƙarama, amma muddin ɗai yana da irin wannan hali, ya rigaya ya zama mutum mai daraja, kamili, nagari wanda ya fi ƙarfin ƙananan bukatun zuci kuma mutum mai amfani ga jama'a.

"Tunawa Da Norman Bethune" (21 ga Disamba, 1939), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Jam'iyyarmu ta Kwaminis ɗa Rundunarmu ta Hanya ta Takwas da Sabuwar Runduna ta Huɗu waɗanda Jam'iyyarmu ke wa ja gaba, su ne bataliyoyi na tawayen turu. Waɗannan bataliyoyimmu sun ba da kansu ɗungum ga 'yanta jama'a kuma suna aiki don bukatun jama'a ba tare da son zuci ko kaɗan ba.

"Bautawa Jama'a" (8 ga Satumba, 1944), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Dukan ma'aikatammu na hukuma kome darajarsu, bayin jama'a ne, kuma kome

mu ke yi domin mu bauta wa jama'a ne. Sabo da haka, don me za mu yi jinkiri wajen barin duk munanan halayemmu ba?

"Ayyukan 1945" (15 ga Disamba, 1944).

Hakkimmu shi ne mu ɗauki ɗawainiyar jama'a. Ko wace magana, ko wane aiki da ko wane tsarin manufar siyasa dole su dace da bukatun jama'a, in kuma an yi kuskure dole a gyara—wannan shi ne abin da a ke nufi da ɗaukar ɗawainiyar jama'a.

"Halin Da Ake ciki da Manufar Siyasarmu bayan Nasara a Yaƙin Kare Harin Japan"(13 ga Agusta, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

In dai ana fama sai tare da sadakar da rai, kuma mutuwa ta kan auku ko yaushe. Amma muna da bukatun jama'a a zuka-tammu kuma muna jin tausayin da yawa game da wahalolin da su ke sha, kuma im mun mutu domin jama'a, mutuwa ce da ta dace. Duk da haka, ya kamata mu yi ƙoƙarin kare mutuwar da ba ta kamata ba.

"Bautawa Jama'a" (8 ga Satumba, 1944), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Uku.

Dukan mutane za su mutu, amma mutuwa ta kan bambanta a daraja. Szuma Chien, marubucin Sin na zamanin da ya ce, "Ko da ya ke mutuwa ta kan zo wa mutane duka, wata mutuwa tana fin Dutsen Tai nauyi, wata kuwa tana kasa jawaska rashin nauyi." A mutu domin jama'a ya fi Dutsen Tai nauyi, amma a yi aiki ga fasis kuma a mutu domin mazambata da masu danniya, mutuwar ta kasa jawaska rashin nauyi.

"Bautawa Jama'a" (8 ga Satumba, 1944), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

18. KISHIN KASA DA ZUMUNTAR DUNIYA

Ko dan Kwaminis mai son zumuntar duniya ya iya zama dan kishin kasa kuma? Mun dauka ba wai kawai zai iya zama ba, amma dole ne ya zama. Kayyadaddun abubuwan da kishin kasa ke kunshe da su sun danganta ne bisa ga halayen tarihi. Da akwai "kishin kasa" irin na mahara Japanawa da na Hitler. Da akwai kuma irin namu kishin kasa. Dole 'yan Kwaminis su tsaya sosai su yaki irin "kishin kasa" na mahara Japanawa da na Hitler. 'Yan Kwaminis na Japan da na Jamus, masu son a ci kasashensu ne a yake-yaken da kasashensu ke yi. Cin nasara bisa mahara Japanawa da Hitler ta ko wace hanya

mai yiwuwa, wannan bukatar mutanen Japan da Jamus ne, kuma cinsu kwata-kwata zai fi kyau. ... Domin yake-yaken da mahara Japanawa da Hitler suka tayar ba cutar mutanen duniya kawai su ke yi ba har da na gida duka. Amma a maganar Sin, abin ya sha bamban, domin ita ce ke shan wahalar hari. Sabili da haka, 'yan Kwaminis na Sin dole su hada kishin kasa da son zumuntar duniya. Mu masu son zumuntar duniya ne kuma 'yan kishin kasa ne, kuma kirarmu ga kowa ita ce, "A yi yaki a kare mahaifa daga mahara". A gare mu sadakarwa (defeatism) laifi ne, kuma mu kokarta domin cin nasara a Yakin Kare Harin Japan wajibi ne. Domin sai wajen yakin kare mahaifarmu ne kawai za mu iya cin mahara mu samo 'yancin kasarmu. Kuma sai da 'yanta kasarmu ne, zai yiwu talakawa da sauran jama'a ma'aikata da manoma su sami 'yancinsu. Nasarar Sin da kuma cin mayaudara masu hari za su taimaki mutanen sauran kasashe. Sabo

da haka wajen yaƙin 'yanta ƙasa, kishin ƙasa tafiyad da zumuntar duniya ne.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yaƙin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Wane irin hali ne ya sa bare mai da sha'anin 'yanta jama'ar Sin kamar nasa ba tare da son zuci ba ko kaɗan? Halin zumuntar duniya ne, halin kwaminisanci ne wanda ya ke ko wane ɗan Kwaminis na Sin ya kamata ya koya. ... Dole mu haɗu da dukan talakawan ƙasashe masu jari, da talakawan Japan, Ingila, Amirka, Jamus, Italiya da duk sauran ƙasashe masu jari, kafin a sami hanyar ka da daulantaka, a 'yanta al'ummarmu da jama'armu kuma da duk al'umma da jama'a na duniya. Wannan ita ce zumuntarmu ta duniya, da wannan zumunta ne mu ke ƙin ƙaramin son al'umma (narrow nationalism) da ƙaramin kishin ƙasa (narrow patriotism).

"Tunawa Da Norman Bethune" (21 ga Disamba, 1939), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

A wajen yaƙin neman cikakken suncin kai, dannannun mutane da farko dole su dogara ga famar kansu, kana su dogara ga taimakon duniya. Mutanen da suka ci nasara a tawayen turunsu, dole su taimaki waɗanda ke fama domin 'yancinsu. Wannan shi ne hakkimmu na zumuntar duniya.

Hira da Aminai Afirkawa (8 ga Agusta, 1963).

Kasashen gurguzu waɗansu irin sabbin ƙasashe ne ɗungum inda aka ka da ajin mazambata, kuma jama'a talakawa suka kama mulki. Ana amfani da ƙa'idar haɗa zumuntar duniya da ƙishin ƙasa wajen dangantaka tsakanin ƙasashen nan. A haɗe

mu ke sosai da bukatu iri daya da buri iri daya.

> "Jawabi a Majalisar Rasha don Bikin Cikon Shekaru 40 da Babban Tawayen Gurguzu na Oktoba" (6 ga Nuwamba, 1957).

Ya kamata mutanen da ke cikin kasashen sansanin gurguzu su hadu, mutanen Asiya, Afirka da Latin Amirka su hadu, mutanen dukan kwantinan su hadu, dukan kasashe masu son zaman lafiyar duniya su hadu kuma dukan kasashen da ke shan wahalar harin Amirka ko mulki ko tsoma baki ko wulakanci su hadu, su kafa babban hadadden goshin fama, su yaki manufar hari da yaki ta daulantakar Amirka kuma su kare zaman lafiyar duniya.

> "Jawabin Goyon Bayan Famar Gaskiya ta Kishin Kasa Da Ja-ma'ar Panama Suke Yi don Kiye-wa Daulantakar Amirka" (12 ga Janairu, 1964).

Abuba ci gaba su ke babu fasawa. Yanzu shekaru 45 ne kawai tun da aka yi Tawaye na 1911, amma fuskar Sin ta sake sosai. A wasu shekaru 45 kuma, watau a shekara ta 2001 ko kuma cikin farkon karni na 21, Sin za ta kara sakewa kwarai. A lokacin za ta zama kasar gurguzu mai karfi kuma mai sana'a. Kuma haka ne ya kamata ta zama. Sin kasa ce mai fadin murabba'in kilomita 9,600,000 da kuma yawan mutane miliyan 600, sabili da haka dole ne ta ba da babban taimako ga dan Adam. Taimakonta a shekaru da yawa da suka shige kadan ne kwarai. Kuma mun yi bakin cikin haka.

Amma dole mu zama kamilai, ba yanzu kadai ba, har ma a shekaru 45 masu zuwa, kuma kullum mu zamana kamilai. A cudanyarmu da kasashen duniya mu Sin-nawa dole mu sa niyya mu cire duk irin nuna fifiko na babbar kasa (chauvinism) daga zukatammu sosai da sosai.

> "Tunawa Da Dr. Sun Yat-sen" (Nuwamba 1956).

Kada mu ɗauki halin girman kai na nuna fifikon babbar ƙasa, mu yi alfarma domin nasararmu a tawaye da wasu nasarori da muka samu a aikin gina ƙasa. Ko wace ƙasa babba ko ƙarama tana da halayenta masu kyau da marasa kyau.

"Jawabin Buɗe Taro na Takwas na Wakilan Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (15 ga Satumba, 1956).

19. JARUMTAKAR TAWAYE

Wannan rundunar soja na da halin bajinta, kuma ta ɗau niyya ta lashe dukan maƙiya ba tare da sadakarwa ba har abada. Kome wahala, kome wuya, muddin mutum ɗaya ya ringi, zai ci gaba da fama.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

A yi amfani sosai da halimmu na fama, watau bajinta a fagen fama, babu tsoron mutuwa, babu tsoron gajiya da kuma ci gaba da yaƙi (watau a yi ta yin fama bisa fama a gajeren lokaci ba hutu).

"Halin Da Ake ciki Yanzu da Ayyukan Gabammu" (25 ga Disamba, 1947), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

Jarumai dubu-dubbai sun ba da rayukansu domin bukatun jama'a, bari mu ɗaga tutarsu sama mu ci gaba a bisa hanyar da ta yi ja wur da jininsu!

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

A ƙudura niyya, kada a ji tsoron mutuwa, a haye ko wace wahala, a ciwo nasara.

"Wawan Tsoho Wanda Ya Ture Duwatsu" (11 ga Yuni, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

A muhimmin lokacin da Yaƙin Cin Arewa (Northern Expedition) ke ci gaba, ... hanyoyin cin amana da ƙin jama'a na wai "tsarkaka jam'iyya" da kashe jama'a da hukumar Kuomintang ta ɗauka sun wargaza wannan haɗaɗɗen goshin fama na ƙasa, watau haɗaɗɗen goshin fama tsakanin Kuomintang da Jam'iyyar Kwaminis da duk rassan mutane, wanda ke wakiltar sha'anin 'yanta mutanen Sin da kuma dukan hanyoyinta na

tawaye. ... Daga nan yaƙin basasa ya ɗauki gurbin haɗin kai, mulkin-kama-karya ya ci gurbin dimaƙuraɗiyya, kuma Sin mai cike da haske ta zama Sin cike da duhu. Amma Jam'iyyar Kwaminis ta Sin da jama'ar Sin ba a tsoratad da su ba, ba a ci su ba kuma ba a kashe su sam ba. Sun tashi tsaye, suka share jininsu, suka bizne abokanansu da suka faɗi, kuma suka ci gaba da fama. Sun ƙara ta da babbar tutar tawaye, suka tasam ma famar kare hari da makamai, kuma a yankin ƙasar Sin mai faɗi, sun kafa gwamnatocin jama'a, suka rarraba ganduna, suka kafa rundunar sojojin jama'a, watau Jar Rundunar Soja ta Sin, kuma suka tanada suka yalwata ƙungiyoyin tawayen jama'ar Sin.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Kuna da kyawawan halaye da yawa kuma kun yi babban aiki, amma ɗole ku

rika tunawa kullum a kan kada ku zama masu girman kai. Ana girmama ku, wannan haka ne, amma wannan ba wuya ya kai ga girman kai. In kun zama masu girman kai, in kun bar zama kamilai kuma kun bar kokari, im ba ku girmama wasu, kuma ba ku girmama ma'aikatan hukuma da jama'a, lalle kun bar zama jarumai kuma wadanda za a yi koyi da su ke nan. A da an sami irin wadannan mutane, amma ina fata ba za ku bi kafarsu ba.

"Dole Mu Koyi Yin Aikin Tsimi da Tanadi" (10 ga Janairu, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

A wajen famar cim makiya da famar mai da aikin kawo albarka na sana'o'i da na noma kuma a yalwata albarkarsu, kun haye dimbin wahaloli masu tsanani, kun nuna bajinta sosai da basira da kuma himma. Kun zama abubuwan koyi ga dukan al'ummar Sin, ku ne jigunan ingiza ci gaban sha'anin jama'a cikin nasara ta ko wane

fanni, ku ne amintattun ginshikai na Gwamnatin Jama'a, kuma ku ne kadarkai masu hada Gwamnatin Jama'a da dimbin jama'a.

Sakon Gaisuwa da Sunan Kwamitin Tsakiya na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin zuwa ga Taron Wakilan Kasa na Jaruman Yaki da Gwanayen Ma'aikata Wadanda Suka Cancanci A Yi Koyi da Su. (25 ga Satumba, 1950).

Mu al'ummar Sin, muna da halin mu yaki makiyi har karshen jinimmu, muna da niyyar kwato duk abubuwan da suka bace mana da karfin kammu kuma muna da karfin mu tsaya kan kafafummu tsakanin al'umman duniya.

"Kan Dabarun Yaki wajen Kin Daulantakar Japan" (27 ga Disamba, 1935), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

20. MU GINA KASARMU CIKIN KWAZO DA TSIMI

Dole mu sa dukan ma'aikatammu na hukuma da dukan jama'armu su rika tunawa cewa kasarmu babba ce ta gurguzu amma matalauciya ce maras ci gaba wajen tattali, wannan babban sabani ne. Mai da Sin kasa mai arziki kuma mai karfi na bukatar shekaru gommai na jan aiki sosai, wanda shi ke har da himmar yin tanadi da hana facaka, watau hanyar gina kasarmu cikin kwazo da tsimi.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Dole ne a yi amfani da kwazo da tsimi a wajen gudanad da aikin ma'aikatai, kantuna, dukan masana'antu na kasa da na tarayya (co-operative) da duk sauran wuraren aiki. Ka'idar kwazo da tsimi dole a bi ta cikin yin kome. Wannan ka'ida ce ta tattali kuma daya ce daga cikin tushen ka'idodin tattalin gurguzu. Sin babbar kasa ce, amma har yanzu matalauciya ce, zai dauki shekaru gommai kafin a mai da Sin wadatacciya. Ko lokacin ma dole ne mu bi ka'idar kwazo da tsimi. Amma a cikin shekaru gommai masu zuwa din nan, a cikin shirye-shiryen raya kasa na shekaru biyar biyar ne musamman ma dole mu dauki kwazo da tsimi, dole mu mai da hankali kan tattali.

Gabatarwa ga "Yadda Ake Gudanad Da Kungiyar Hadin Kan Manoma cikin Kwazo da Tsimi" (1955).

Ko ina mu ke, dole mu daukaka karfimmu da arzikimmu, kuma kada mu yi gajeruwar

lura mu shiga facaka da almubazzaranci. Ko ina mu ke, daga shekararmu ta farko wajen aiki dole mu yi la'akari da shekaru da yawa masu zuwa, da tsayuwa ga yaki mai tsawon lokaci, da mai da hari, kuma da aikin ginę-gine bayan an kori makiya. Kada a yi ßarna ko almubazzaranci, kuma a kokarta wajen yada aikin kawo albarka. Ba da jimawa ba a wasu wurare mutane sun sha wahala sosai domin ba su yi dogon la'akari ba, ba su mai da hankali kan tattali da karfi da arziki na jama'a da kuma kan yada aikin kawo albarka ba. Wannan darasi na nan kuma sai a mai da hankali.

"Dole Mu Koyi Yin Aikin Tsimi da Tanadi" (10 ga Janairu, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Domin mu gaggauta mayarwa da kuma yalwatawa na aikin noma da masana'antu a kananan garuruwa, dole mu yi iyakacin kokarimmu, a cikin wannan fama ta kau da tsarin zaman mulkin gargajiya, mu adana

dukan hanyoyin kawo albarka da na raya zaman jama'a masu amfani, kuma mu dauki matakan gaske mu hana kowa ßata su ko yin banza da su, kuma mu hana yawan ci da sha na banza kuma mu mai da hankali bisa tsimi da tanadi.

"Jawabi a Taron Ma'aikatan Hukuma a 'Yantacciyar Jihar Shansi-Suiyuan" (1 ga Afril, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Tsimi dole ya zama ka'idar ja gora a wajen kashe kudin gwamnatimmu. Dole a fahimtad da dukan ma'aikatan gwamnati cewa cin hanci da shiga facaka manyan laifuffuka ne. Yakimmu kan cin hanci da facaka ya sami 'yan nasarori, amma ana bukatar kara kokari. Tsarin lissafin kudi, dole ya bi ka'idar tanada ko wane anini domin yaki, domin sha'anin tawaye da kuma domin aikin gina tattalimmu.

"Tsarin Manufar Siyasarmu wajen Tsimi da Tanadi" (23 ga Janairu, 1934), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Wani mugun nufi mai hadari ya ɓullo yanzu tsakanin ma'aikatammu da yawa, watau rashin son raba dadi da wuya da jama'a, da kuma mai da hankali kan yin suna da samu. Wannan ba shi da kyau ko kadan. Hanya daya ta hana wannan ita ce mu saukaka kungiyoyinmu a wannan kamfen din kara aikin kawo albarka da yin tsimi, kuma mu mai da ma'aikatan hukuma ga kananan gurabu domin da yawa daga cikinsu su koma aikin kawo albarka.

> "Game da Hanyar Daidaita Saɓani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Aikin kawo albarka da sojoji ke yi domin ciyad da kansu ba kawai ya kyautata zaman sojoji kuma ya saukaka wa jama'a wahala ba, kuma ta haka an sami damar kara sojoji, bugu da kari, ya kawo wasu abuba masu amfani. Su ne:

(1) Ya kyautata dangantaka tsakanin hafsoshi da kananan sojoji. Hafsoshi da

kananan sojoji suna aikin kawo albarka tare kuma sun zama kamar 'yanuwa.

(2) Ya karfafa hali mai kyau a aiki. ... tun da sojoji suka fara aiki domin ciyad da kansu, halin son aiki ya karfafu, kuma an cire halayen son sauki.

(3) Ya karfafa biyayya. Maimakon raunana biyayya a fagen fama da kuma zaman sojoji, yin biyayya wajen aikin kawo albarka ya karfafa ta.

(4) Ya kyautata dangantaka tsakanin sojoji da jama'a. Muddin dai sojoji sun fara "ajiye wa kansu gida", ɓata kayan jama'a ya ragu ko ma ba ya aukuwa sam. In sojoji da jama'a suna musayar aiki kuma suna taimakon juna wajen aikin kawo albarka, aminci tsakaninsu zai kara karfi.

(5) Ya rage koke-koke cikin rundunar soja ga gwamnati, kuma ya gyara dangantaka tsakaninsu.

(6) Ya kara karfi ga babban kamfen din aikin kawo albarka na jama'a. In dai sojoji sun shiga aikin kawo albarka,

bukatar gwamnati da wasu kungiyoyi su yi haka ita ma za ta kara wajaba, kuma za su yi haka da niyya sosai. Alhali kuwa bukatar yin babban kamfen na dukan jama'a su kara aikin kawo albarka za ta kara wajaba, kuma za a yi ta da niyya sosai.

> "Kan Aikin Kawo Albarka na Rundunar Soja domin Ci Da Kansu da Kuma kan Muhimmancin Manyan Harkokin Gyara da Aikin Kawo Albarka" (27 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Uku.

Wasu mutane na cewa kadan kungiyoyin sojoji sun shiga aikin kawo albarka, ba za su iya koyo ko yin yaki ba, kuma wai in gwamnati da wasu kungiyoyinta sun shiga su ma ba za su iya yin aikinsu ba. Wannan magana ba daidai ba ne. A 'yan shekarun baya kungiyoyin sojoji na Jihar Iyaka sun yi babban aikin kawo albarka, sun ba kansu abinci mai yawa da kuma tufafi isassu, kuma

a lokacin sun yi koyonsu na yaki, kuma sun koyi siyasa da yaki da jahilci, a duk ayyukan nan sun sami babbar nasara fiye da da, kuma hadin kai tsakanin sojoji ya karu fiye da da, haka kuma tsakanin sojoji da jama'a. Lokacin da a ke babban kamfen din aikin kawo albarka a fagen fama bara, an sami manyan nasarori a wajen yaki har ma am fara babban kamfen din horon sojoji. Albarkacin aikin kawo albarka, ma'aikatan gwamnati da wasu kungiyoyi zamansu ya kara kyau kuma suna kara kwantad da hankali da gyara hannu (efficiency) wajen aiki, wannan haka ne a Jihar Iyaka da fagen fama.

> "Dole Mu Koyi Yin Aikin Tsimi da Tanadi" (10 ga Janairu, 1945), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Uku.

21. DOGARA BISA KARFIN KAI DA JUREWA MADACIYAR FAMA

A kan wane tushe ne manufarmu za ta dogara? Dole ta dogara bisa karfin kammu, wannan shi ne a ke kira dogara bisa karfin kai. Ba mu kadai mu ke ba, dukan kasashe da mutane na duniya masu kin daulantaka aminammu ne. Amma duk da haka, dole mu karfafa dogara bisa karfin kai. Da dogara bisa rundunonin da mu kammu muka kafa, za mu ci dukan azzaluman Sin da na waje.

"Halin Da Ake ciki da Manufar Siyasarmu bayan Nasara a Yakin Kare Harin Japan" (13 ga Agusta, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Mun tsaya wa dogara kan karfin kai. Muna fatan samun taimako daga waje, amma ba za mu dogara bisansa ba, mu dogara bisa kokarimmu, bisa karfin kage na dukan rundunar soja da jama'a.

"Dole Mu Koyi Yin Aikin Tsimi da Tanadi" (10 ga Janairu, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Cin nasara a kasa duka taki na farko ne kawai cikin doguwar tafiya ta *li* dubu goma. ... Tawayen Sin babba ne amma hanyar da ke shimfide bayan tawayen ta fi tsawo, aikin kuma ya fi girma da wuya. Wannan ya kamata a bayyana shi a fili cikin Jam'iyya tun yanzu. Dole a taimaki abokai su ci gaba da zama kamilai, masu hankali, marasa girman kai da kaudi a cikin haliyar aikinsu. Dole a taimaki abokanai su ci gaba da tsare haliyar zama mai sauki da fama mawuyaciya.

"Rahoto ga Cikakken Zama na Biyu na Taro na Bakwai na Kwamitin Tsakiya na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (5 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Dole mu kau da dukan tunani tsakanin ma'aikatan hukumarmu na cin nasarori cikin ruwan sanyi da katari, ba tare da mummunar fama, shan wahala game da zub da jini ba.

"A Gina Sansani Mai Karfi a Arewa Maso Gabas" (28 ga Disamba, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ya kamata mu rika yin furofaganda tsakanin mutane bisa gaskiyar ci gaban duniya da kuma gobe mai haske domin su amince da cin nasara. Haka kuma, dole mu shaida wa jama'a da abokai cewa hanyarmu ba a mike ta ke ba. Har yanzu da akwai mani'i da wahaloli da yawa a kan hanyar tawaye. Taron Jam'iyyarmu na Bakwai ya hanga cewa da akwai wahaloli da yawa a gabammu, mu ma mun fi son mu ji da wahaloli da yawa a kan a ce da kadan. Wasu abokai ba su son tunanin wahaloli da yawa. Tabbat ne dai da akwai wahaloli, dole mu san yawan wahalolin da ke da akwai, kada mu

dauki halin "rashin gane haka". Dole mu san da su mu bincike su, mu yake su. Babu mikakkun hanyoyi a duniya, dole mu shirya mu bi hanya mai karkata, kada mu yi kokarin samun kome cikin sauki. Kada a zata cewa wata safiya dukan azzalumai za su durkusa bisa ra'ayinsu. A takaice dai, da akwai haske a gaba, amma hanyar tana da karkata. Har yanzu da akwai wahaloli da yawa a gaba da bai kamata a kasa lura da su ba. Im mun hadu da dukan jama'a, mu yi kokari tare, lalle ne za mu haye dukan wahaloli, mu ci nasara.

"Kan Shawarwarin Chungking" (17 ga Oktoba, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ko wane ne ya ke ganin wurin haske kawai ba tare da ganin wahaloli ba, ba zai iya yaki sosai domin cika dawainiyar Jam'iyya ba.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Dukiyar zaman al'umma, ma'aikata da manoma da masana ma'aikata su ke ƙago ta. Muddin sun ɗauki ƙaddararsu a hannunsu, kuma suka bi tafarkin Marksanci-Leninanci, a himmance suka ɗauki halin warware matsaloli maimakon guje musu, babu wata wahala a duniyan nan da ba za su haye ta ba.

Gabatarwa ga "Sakataren Jam'iyya Ya Kama Shugabanci Kuma Dukan Mambobin Jam'iyya Suna Taimakawa wajen Gudanad Da Kungiyar Haɗin Kan Manoma" (1955).

Abokanammu na dukan Jam'iyya dole su lura da wannan sosai kuma su shirya su haye dukan wahaloli da halin bajinta kuma bisa shiri. Tarkacen azzalumai da mu duka muna da wahaloli. Amma wahalolin tarkacen azzalumai ba su hayuwa, domin tarkacen azzaluman su ne rundunonin da ba su da gobe kuma suna bakin mutuwa.

Wahalolimmu kuwa za mu haye su, domin mu sabbin rundunoni ne masu tashi kuma da haske a gabammu.

"A Yi Maraba da Sabon Tashe na Tawayen Sin" (1 ga Fabrairu, 1947), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Huɗu.

A lokacin wahala, kada mu kasa ganin nasarorimmu, dole mu ga gaba mai haske kuma mu ƙara himma.

"Bautawa Jama'a" (8 ga Satumba, 1944), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Duk sabbin abubuwa kullum suna gamuwa da wahaloli da abubuwan faɗi-ka-tashi in suna girma. Zaton iska ne kawai a zata sha'anin gurguzu abu ne mai sauƙi, mai saurin nasara ba tare da wahaloli da abubuwan faɗi-ka-tashi ko ba da iyakacin ƙoƙari da himma ba.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

A wasu lokatai na famar tawaye, wahaloli na danne halayen dadi, kuma a wannan hali, wahaloli na zama muhimman fannonin saßani, kuma halayen dadi na zama fannoni marasa muhimmanci. Amma da kokarinsu 'yan tawaye na iya haye wahalolin da hankali hankali, har su bude sabon hali mai dadi, sabo da haka halin wuya ya kan ba da gurbinsa ga halin dadi.

"Kan Saßani" (Agusta 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Mene ne aiki? Aiki fama ne. Da akwai wahaloli da matsaloli a wadannan wurare domin mu haye su, kuma mu daidaita su. Za mu can aiki da fama domin haye wadannan wahaloli. Abokin kirki shi ne wanda ya fi dokin tafiya wurin da wahaloli suka fi yawa.

"Kan Shawarwarin Chungking" (17 ga Oktoba, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Da akwai wata tatsuniyar Sin mai suna "Wawan Tsoho Wanda Ya Ture Duwatsu". Tana ba da labarin wani tsoho ne wanda ya zauna a arewacin Sin shekaru aru-aru kuma ana kiransa Wawan Tsoho na Dutsen Arewa. Gidansa na duban kudu kuma a kofar gidansa da manyan tuddai biyu, Taihang da Wangwu, wadanda su ke tare masa hanya. Tare da niyya, ya shugabanci 'ya'yansa wajen hake wadannan duwatsu da fartanya. Wani tsoho mai suna Tsoho Mai Wayo, da ya gan su, ya shiga dariya yana musu ba'a cewa "Wace wauta ce ku ke yi haka! Ai ba shi yiwuwa sam ga ku 'yan kadan haka ku hake wadannan manyan duwatsu biyu." Wawan Tsoho ya amsa, ya ce, "In na mutu, 'ya'yana za su ci gaba, in su kuma sun mutu, jikokina sa ci gaba da yi har zuwa ga tattaßa kunnena da haka za a ci gaba. Da tsayinsu din nan duka, duwatsun ba za su kara wani tsayi ba, kuma ko wane hako muka yi raguwa su ke. To, me zai hana mu kau da su?" Da ya karya-

tad da ra'ayin kuskure na Tsoho Mai Wayo, sai ya ci gaba da haƙo ko wace rana ba tare da ya karaya ba. Allah ya ji tausayinsa ya turo mala'iku biyu waɗanda suka ɗauke duwatsun nan biyu. A yau da manyan duwatsu biyu kamar kaya a bayan Sinnawa, ɗaya daulantaka, ɗaya kuma mulkin gargajiya. Jam'iyyar Kwaminis ta Sin da jimawa ta ɗaura niyyar kauda waɗannan duwatsu. Dole mu dage mu yi aiki ba tare da hutawa ba, mu ma Allah zai ji tausayimmu. Allah ɗimmu ba wani ba ne da ya wuce ɗimbin mutanen Sin. In sun tashi su haƙe duwatsun nan tare da mu, me zai hana mu kau da su?

"Wawan Tsoho Wanda Ya Ture Duwatsu" (11 ga Yuni, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

22. HANYOYIN TUNANI DA HANYOYIN AIKI

Tarihin ɗan Adam, tarihi ne mai ci gaba kullum daga daular larura zuwa ga daular 'yanci. Wannan ko ba shi ƙarewa har abada. A ko wane halin zama na al'umma inda a ke da ajujuwa, fama tsakanin ajujuwa ba ta ƙarewa. A halin zaman al'umma inda ba ajujuwa, fama tsakanin sabo da tsoho, tsakanin gaskiya da ƙarya ba ta ƙarewa har abada. A cikin famar aikin kawo albarka da gwajin kimiyya, ɗan Adam kullum yana ci gaba, kuma halitta na ta sakewa, ba su taɓa tsayuwa a matsayi guda ba. Sabili da haka, mutum sai ya ci gaba da tara fasaha, ya yi ta ganowa da sanabe da ƙago-

wa da kuma ci gaba. Tunanin rashin ci gaba da na karaya da na son sauki da na girman kai duka ba daidai ba ne. Abin da ya sa ba daidai ba ne domin ba su dace da gaskantattun abubuwan tarihin ci gaban zaman dan Adam tun wajen shekaru miliyan ba, kuma ba su dace da gaskantattun abubuwan tarihin halitta yadda muka sani ba (watau halitta kamar yadda aka nuna a tarihin sammai, "taurari, wata da rana" da kassai, da rayuwa da wasu sauye-sauyen halitta).

Daga "Rahoton Waziri Chou En-lai kan Aikin Gwamnati a Zama na Farko a Taro na Uku na Wakilan Jama'ar Jamhuriyar Jama'ar Sin"(21-22 ga Disamba, 1964).

Kimiyyar halitta tana daya daga cikin makaman dan Adam wajen famarsa ta neman 'yanci. Domin samun 'yanci a zaman al'umma, dan Adam dole ya yi amfani da kimiyyar zaman al'umma domin ya fahimci zaman al'umma, ya sauya zaman al'umma kuma ya yi tawaye. Domin samun 'yanci ta wajen halitta, dan Adam dole ya yi amfani da kimiyyar halitta domin ya fahimci halitta, ya haye kuma ya sauya ta, ta haka ya sami 'yancinsa daga halitta.

Jawabi a Taron Kafa Kungiyar Binciken Kimiyyar Halitta ta Jihar Iyaka (5 ga Fabrairu, 1940).

Filosofiya (philosophy) ta Marksanci kan materiyalisanci na diyalektisanci na da sannun halaye biyu. Na farko halinta na aji, watau ta nuna a fili materiyalisanci na diyalektisanci abin bauta wa talakawa ne. Na biyu halin aikatawarta, watau ta karfafa dogarar sanin-ka kan aikatawa, ta karfafa sanin-ka ya dogara ne kan aikatawa kuma ya juya yana bauta wa aikatawa.

"Kan Aikatawa" (Yuli 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Filosofiya ta Marksanci ta ɗauka cewa muhimmiyar matsala ba ta ga fahimtar dokokin hakikanan halayen duniya kuma ta haka a bayyana ta ba, sai dai wajen yin amfani da sanin waɗannan dokoki domin a himmanta wajen canja duniya.

"Kan Aikatawa" (Yuli 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Daga ina ne ra'ayoyi masu kyau su ke? Daga sama ne suka faɗo? A'a. An halicce su ne a zukata? A'a. Sun zo ne kawai daga aikatawar mutum a halin zama, sun zo daga aikatawa uku na mutum a halin zama, watau daga famar kawo albarka, fama tsakanin ajujuwa da kuma jarrabe-jarraben kimiyya.

"Daga Ina Ra'ayoyi Masu Kyau Suka Zo?" (Mayu 1963).

Irin halin zaman mutum a al'umma ne ke ƙudura tunaninsa. Muddin in jama'a sun fahimci gaskantaccen tunanin da ke

wakiltar ajujuwa masu ci gaba, wannan tunani zai zama ƙarfin abu da zai sake zaman al'umma ya kuma sake duniya.

"Daga Ina Ra'ayoyi Masu Kyau Suka Zo?" (Mayu 1963).

A aikatawarsu cikin zaman al'umma, mutane na shiga fama iri daban daban, kuma su sami wadatacciyar fasaha daga nasararsu da faɗuwarsu. Dimbin abubuwa masu faruwa a kewaye da mu na ganuwa cikin hankalin mutum ta hanyoyi biyar na jikinsa, watau hanyoyin gani, ji, shaƙa, ɗanɗana da taɓawa. Da farko dai sani abin gani ne. Tashi zuwa fahimtar ilmi, watau zuwa wani ra'ayi, yana faruwa ne lokacin da aka sami isasshen ilmin gani. Wannan hanya ce ɗaya ta ganewa. Mataki ne na farko a cikin dukan hanyar ganewa watau mataki mai kaiwa daga hakikanin abu (objective matter) zuwa ga abin tunanin zuci (subjective consciousness), daga kasancewar abu zuwa ga tunani. Ko hankalin

wani ko tunaninsa (har da sanin-ka, manufofin siyasa, shirye-shirye da dabaru) suna bayyana dokokin hakikanan halayen abuba da ke kewaye da mu sosai ba za a tabbatar ba a wannan mataki, watau a lokacin ba za a iya cewa su daidai ne ko ba daidai ba. Daga nan sai mataki na biyu a hanyar ganewa, watau mataki mai kaiwa daga hankali zuwa ga abu dahir, daga tunani zuwa ga kasancewar abu, wurin da ilmin da aka samu a mataki na farko an yi amfani da shi a aikatawar zaman al'umma don tabbatar da ko sanin-ka da manufofin siyasa da shirye-shirye da dabaru sun sami nasarar da a ke tsammani. Galibi dai waɗanda suka yi nasara daidai ne, waɗanda ba su yi nasara ba kuma ba daidai ba ne, wannan ko gaskiya ce musamman a famar mutum bisa halitta. A famar zaman al'umma, kungiyoyin da ke wakiltar ajin ci gaba, wani lokaci suna faduwa ba domin tunaninsu ba kyau ba ne sai dai a yawan kungiyoyin da ke famar, ba su da karfi a lokacin kamar kungiyoyin zalunci,

sabo da haka ana cinsu na dan lokaci, amma tabbas ne za su ci nasara ko ba daɗe ko ba jima. Sanin mutum na babbar karuwa ta wajen gwajin aikatawa. Wannan karuwa ta fi ta farko ma'ana. Domin wannan karuwa ce kawai za ta iya nuna daidaici ko rashin daidaici na karuwar ganewa ta farko, watau tunani da sanin-ka da manufofin siyasa da shirye -shirye da dabaru da aka samu a lokacin nuna hakikanan halaye a kewaye da mu. Babu wata hanyar gwada gaskiya daban.

"Daga Ina Ra'ayoyi Masu Kyau Suka Zo?" (Mayu 1963).

Galibi, a kan sami sanin gaske bayan an yi ta maimaitawa da yawa ta hanyar ɗaukar abu dahir ga hankali, daga nan kuma a mayar ga abin, watau tashi daga aikatawa zuwa ga sani, daga sani zuwa ga aikatawa. Wannan tsarin Marksanci ne game da sani,

watau tsarin materiyalisanci na diyalektisanci game da sani.

"Daga Ina Ra'ayoyi Masu Kyau Suka Zo?" (Mayu 1963).

Duk wanda ke son sanin wani abu ba ya da hanyar yin haka sai ta yin cudanya da abin, watau ya yi zama (ko ya yi aiki) a wurin abin. ... In kana son samun ilmi dole ka shiga aikin sauya hakikanan abuba. In kana son jin yadda faya (pear) ta ke, dole ka sauya fayar ta hanyar taunawa da kanka. ... In kana son ka san tsarin sanin-ka da hanyoyi na tawaye, dole ka shiga tawaye. Ko wane ilmi na sosai ya taso ne daga fasahar da aka samu kai tsaye.

"Kan Aikatawa" (Yuli 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Sani na farawa daga aikatawa, kuma tsarin sanin-ka (theoretical knowledge) wanda aka samu daga aikatawa dole a mayar ga aikatawa. Babban aikin sani na bayyana

kansa ba kawai a saurin tashi daga saningani zuwa ga sanin-hankali ba, amma — wannan ko mafi muhimmanci ne — dole ya bayyana kansa wajen tashi daga sanin-hankali zuwa ga aikin tawaye.

"Kan Aikatawa" (Yuli 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

An sani sosai cewa kome za ka yi, muddin ba ka fahimci asalin halayensa ba da halittarsa da dangantakarsa ga wasu abuba, ba za ka san dokokinsa ko kuma ka san yadda a ke yinsa ko a ke iya yinsa sosai ba.

"Matsalolin Sihirin Shiri a Yakin Tawayen Sin" (Disamba 1936), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Im mutum na son nasara a aikinsa, watau yana son samun abin da ya ke tsammani, dole ya kawo ra'ayoyinsa su dace da dokokin hakikanan halaye a kewaye da mu, im ba su dace ba, zai fadi a aikinsa. Bayan ya fadi, sai ya sami darasi daga faduwar, ya gyara ra'ayoyinsa ya sa su dace da dokokin

halaye a kewaye da mu, sai ta haka zai mai da rashin nasara cikin nasara, wannan ne abin da a ke nufi da "rashin nasara ce uwar nasara" da kuma "faɗuwa cikin rami, ƙaruwa ga wayonka".

"Kan Aikatawa" (Yuli 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Mu 'yan Marksanci ne, kuma Marksanci na koya mana cewa a tinƙararmu ga ko wace matsala dole mu fara daga hakikanin abu, ba daga bayanin iska ba, kuma za mu sami ƙa'idodimmu na bi, manufofin siyasa da dabaru daga cikin binciken wannan hakikanin abu.

"Jawabi a Taron Yenan kan Wallafa da Fasaha" (Mayu 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ainihin hanyar aiki wadda mu 'yan Kwaminis dole ne mu rike sosai a zuci, ita ce ta ɗaukar manufofin siyasar ayyukammu bisa ga halayen gaske. Im mun dubi dalilan kuskure-kuskuren da muka yi, sai mu

ga duka sun taso ne domin mun bar halin gaske a wani lokaci a wani wuri, kuma muna bin tunanin zuci (subjective) wajen ɗaukar manufofin aikimmu.

"Jawabi a Taron Ma'aikatan Hukuma a 'Yantacciyar Jihar Ṣhansi-Suiyuan" (1 ga Afril, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Tunanin idiyalisanci da tunanin metafisik abubuwa ne kawai mafiya sauki a duniya, domin nan ne mutane za su yi ta maganar banza yadda su ke so ba tare da ɗora ta bisa wani hakikanin abu ba, ko tare da gwada ta da abin gaskiya ba. Materiyalisanci da diyalektisanci suna bukatar himma. Dole a ɗora bisa kuma a gwada su da hakikanin abu. Im mutum bai ɗaura himmar ba, lalle zai faɗa kan idiyalisanci da metafisik.

Gabatarwa ga "Rubutun Dà Aka Yi kan Kungiyar Makiyan Tawaye ta Hu Feng" (Mayu 1955).

Im mun dubi abu, dole mu jarraba halittarsa, kuma mu ɗauki siffarsa kamar hanya mai kaiwa ga dokin ƙofa kuma bayan mun shige dokin ƙofar, dole mu fahimci halittar abin sosai, wannan ita ce kawai amintacciyar hanyar bincike kuma ta kimiyya.

"Garwashi Daya Kan Tada Wutar Jeji" (5 ga Janairu, 1930), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Babban sanadin ci gaban abu ba a waje ya ke ba sai a ciki, ya danganta ga saɓanin da ke cikin abin. Wannan saɓani na ciki yana tare da ko wane abu, shi ya sa abu ya ke motsi da girma. Saɓani cikin abu shi ne babban sanadin ci gaban wannan abu, kuma dangantakarsa da kuma aikinsa da wasu abuba su ne na biyu.

"Kan Saɓani" (Agusta 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Diyalektisanci na materiyalisanci na ganin dalilan waje su ne sharuɗan kawo sauyi, kuma dalilan ciki su ne tushen sauyin, kuma

dalilan waje sai da dalilan ciki su ke aiki. A gumin da ya dace ƙwai na zama kaza, amma babu gumin da zai sauya dutse zuwa kaza, domin ko wannensu na da tushe daban.

"Kan Saɓani" (Agusta 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Filosofiya ta Marksanci ta ɗauka cewa doka ta haɗuwar kishiyoyi ita ce tushen doka ta duniya. Wannan doka tana amfani a duk duniya, ko a halitta, ko a zaman ɗan Adam ko a tunanin mutum. Tsakanin kishiyoyin da ke cikin saɓani da akwai haɗuwa da fama, kuma wannan ne ke sa abuba yin motsi da kuma sauyawa. Da saɓani ko ina, amma saɓani na bambanta bisa bambancin halittar abuba daban daban. A ko wane ƙayyadadden abu haɗuwar kishiyoyi bisa sharaɗi ne, ba mai jimawa ba ne kuma mai wucewa ne, sabo da haka aka sami dangantaka, amma famar kishiyoyi wajibi ne.

"Game da Hanyar Daidaita Saɓani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Hanyar bincike ta diyalektisanci ce. Da bincike muna nufin binciken saßani cikin abuba. Bincike sosai ba shi yiwuwa im ba tare da ilmin rayuwa sosai ba kuma ba tare da fahimtar saßanin da a ke batu a kai da gaske ba.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

Lenin ya ce, kayyadadden bincike na kayyadaddun halaye shi ne "abu mafi digi a Marksanci, kuma shi ne ruhun Marksanci". Abokanammu da yawa sun rasa sanin hanyar yin bincike, ba su son yin zurfi cikin rikitattun abuba, su bincika, su duba sosai da sosai, amma sun fi son yanke magana cikin sauki ko tabbas daidai ne ko ba daidai ba. ... Daga yanzu ya kamata mu gyara irin wannan hali.

"Kan Nazari da Halin Da Ake ciki Yanzu" (12 ga Afril, 1944), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Hanyar da wadannan abokai ke duban matsaloli ba daidai ba ne. Ba su duban fannoni masu tushe ko muhimmai na matsaloli, sai dai karfafa marasa tushe da muhimmanci su ke. Ya kamata a nuna cewa kada a kasa lura da wadannan fannoni marasa tushe da muhimmanci kuma dole ne a warware su daya daya. Amma kada a dauke su kamar masu tushe ko muhimmai, in an yi haka za mu rudu mu rasa hanyar bi.

"Kan Al'amarin Gama Gwiwa wajen Noma" (31 ga Yuli, 1955).

A wannan duniya, abuba rikitattu ne kuma dalilan kudura suna da yawa. Dole mu dubi matsaloli ta hanyoyi daban daban, ba kawai ta hanya daya ba.

"Kan Shawarwarin Chungking" (17 ga Oktoba, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Sai kawai wadanda ke tinkarar matsaloli ta hanyar tunanin zuci, ta gefe daya da kuma

sama sama ne, za su yi kazallahar ba da iko ko umurni lokacin da suka isa wani wuri ba tare da lura da halayen ba, ba tare da duba yadda sukutum din abuba su ke sosai ba (watau tarihinsu da kuma halin da su ke ciki yanzu a sukutum) kuma ba tare da samun asalin abuban ba (watau halittarsu da kuma dangantakar da ke tsakanin wani da wani). Irin wadannan mutane lalle ne za su fadi.

"Kan Aikatawa" (Yuli 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Im mun zo nazarin matsala, dole mu bar tunanin zuci, da jingina gefe daya da duba sama sama. Zama mai tunanin zuci yana nufin kasa duba matsaloli yadda su ke, watau kasa yin amfani da ra'ayin materiyalisanci wajen duba abuba. Na yi magana kan wannan a rubutuna "Kan Aikatawa". Kuma a jingina gefe daya, yana nufin rashin duban matsaloli ta dukan gefe. ... Ko kuma za a ce, ganin rabi ba duka ba, ko

kuma ganin itatuwa ba tare da ganin jeji ba. Ta haka, ba shi yiwuwa a sami hanyar warware saɓani, ba shi yiwuwa a cika ayyukan tawaye, a tafiyar da aikin da aka bayar sosai ko a ci gaba da famar tunani cikin Jam'iyya da kyau. Lokacin da Sun Wu Tzu ya ce a maganar sha'anin soja, "Ka san makiyi, ka san kanka, nan za ka iya yaki dari ba tare da kasadar faduwa ba", yana magana ne kan gefe biyu na yaki. Wei Cheng na Zamanin Sarautar Tang, shi ma ya fahimci laifin jingina gefe daya sa'in da ya ce, "Ka ji duk gefe biyu nan za ka waye, amma ka saurari gefe daya sai ka duhunce". Amma abokanammu galibi duka suna ganin matsaloli ta gefe guda ne, sabo da haka su kan shiga wahala. ... Lenin ya ce, "Domin mu san abu sosai, dole mu rungume kuma mu nazarci duk gefensa da dangantakarsa da 'mahadinsa'. Ko kusa ba za mu iya samun haka gaba daya ba, amma neman sanin duk gefe makari ne ga kuskure da tauri." Dole mu tuna da maganarsa. Kuma duba

sama-sama yana nufin a kasa duba halayen saßani gaba ɗayansa ko halayen ko wane gefen abu nasa, watau yana nufin a musanta wajabtar bincike sosai cikin abu ɗa kuma nazarin halayen saßaninsa cikin tsanaki, sai ɗai kawai a duba daga nesa, bayan an duba haka nan, sai a yi saurin neman warware saßani (watau ko amsa tambaya, ko sasanta gardama, ko shirya aiki ko ba da umurnin yaƙi). Wannan hanya ta yin abuba ba shakka za ta kai ga wahala. ... A jingina gefe ɗaya kuma a duba sama-sama daidai da bin tunanin zuci ne. Domin dukan abuban gaske da dangantaka tsakaninsu kuma dokokin ciki ke mallakarsu, amma maimakon nuna abuba yadda su ke, waɗansu mutane sai kawai suna duban abuba ne ta gefe ɗaya ko kuma sama-sama, ba su san ko dangantakarsu ba ko dokokinsu na ciki, sabo da haka hanyarsu ta tunanin zuci ce.

"Kan Saßani" (Agusta 1937),
Zababbun Ayyuka, Littafi na Farko.

Jingina gefe ɗaya yana nufin yin tunani ta hanya ɗaya tak, watau tinƙarar matsala tà hanyar metafisik. Im mun zo duba aikimmu, jingina gefe ɗaya ne im mun ga dukan kome ɗaidai ne ko ba ɗaidai ba. ... A ga abu duka daidai, shi ne a ga mai kyau ba tare da ganin maras kyau ba, watau a yarda da yabo a ƙi yarda da suka. A yi magana cewa kamar dukan aikimmu mai kyau ne ta ko wane fanni, wannan bai dace da gaskiya ba. Ba gaskiya ba ne a ce kome na da kyau, da akwai marasa kyau da kuma kuskure. Amma kuma ba za a ce kome ba kyau ba, wannan ma bai dace da gaskiya ba. A nan ya kamata a yi bincike. A musanta kome, daidai ne da yin tunani ba tare da bincike ba, cewa babu abin da aka yi sosai, kuma wannan bąbban aikin gina gurguzu, babbar fama da mutane ɗarurrukan miliyan suka shiga kamar aikin banza ne babu abin yabo sam. Ko da ya ke da akwai bambanci tsakanin mutane da yawa da ke da wannan ra'ayi da waɗanda ke gaba

da tsarin zaman gurguzu, amma wadannan ra'ayoyi kuskure ne kuma cuta ce ƙwarai, sai ɓata wa jama'a zuciya kawai za su yi. Kuskure ne mu dubi aikimmu da ra'ayi cewa kome daidai ne ko da ra'ayi cewa kome ba daidai ba ne.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

A fuskantar ko wace matsala dan Marksanci ba kawai ya kamata ya dubi sashe-sashen abin ba har ma da sukutum dinsa. Kwadɔ a cikin rijiya ya ce, "Samaniya ba ta fi bakin rijiya fadi ba". Wannan ba gaskiya ba ce, domin samaniya ba daidai ta ke da fadin bakin rijiya ba. Da ya ce, "Wani yankin samaniya daidai ne da fadin bakin rijiya", da wannan zai zama gaskiya, domin ya dace da hakika.

"Kan Dabarun Yaki wajen Kin Daulantakar Japan" (27 ga Disamba, 1935), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Dole mu koyi duban matsaloli ta dukan gefe, ba kawai mu ga gaban abubuwa ba, har ma da baibai dinsu. A wadansu halaye, abu maras kyau na kai ga samun sakamako mai kyau, kuma mai kyau na kai ga samun sakamako maras kyau.

"Game da Hanyar Daidaita Saɓani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Mun gane cewa a ci gaban tarihi duka, abubuwa ke sarrafa hankali, zaman cikin al'umma ke sarrafa tunanin zama. Mu ma mun gane kuma tilas mu gane irin aikin mayarwa ta hankali kan abubuwa, da kuma aikin mayarwa ta hankalin zama bisa zama cikin al'umma da kuma aikin mayarwa ta tsarin koli (superstructure) bisa tushen tattalin arzikin kasa. Wannan hanya ba ta gocewa materiyalisanci ba, sai dai ta guji abin da a ke kira bin materiyalisanci a duhunce (mechanical materialism) kuma tana

rike da abin da a ke kira materiyalisanci na diyalektisanci.

"Kan Saßani" (Agusta 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Wajen neman nasara, wadanda ke shugabantar yaki ba za su wuce iyakar da hakikanan sharuda suka sa ba, duk da haka a cikin iyakar, za su iya kuma tilas su himmantu wajen neman nasara. Fagen aiki ga kwamandai a yaki dole a gina shi bisa yardar hakikanan sharuda, amma a wannan fage za su iya tafiyad da manyan ayyukan kirki masu ma'ana iri ta jaruntaka.

"Kan Yaki cikin Dogon Lokaci" (Mayu 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Mutane dole su mai da tunaninsu ya dace da halayen da aka sauya. Amma fa, ko wane ne bai kamata ya shiga tunanin iska maras kan gado ba, ko ya yi shirin yin

aikin da hakikanan sharuda ba su yarje masa ba ko kutsa kai ga yin abuban da ba su yiwuwa.. Amma matsalar yau ita ce, tunanin gargajiya na 'yan Dama har yanzu yana kawo fitina a fannoni da yawa, yana hana aiki a wadannan fannoni tafiya daidai da ci gaban hakikanan halaye. Matsalar yanzu ita ce mutane da yawa suna tsammani ba shi yiwuwa su aikata wasu abuba wadanda da ma za a iya aikata su in sun ta da himma.

Gabatarwa ga Littafi Mai Suna "Tashen Gurguzu a Kauyukan Sin" (27 ga Disamba, 1955).

Dole kullum mu yi amfani da hankulammu, mu tuna kome sosai. Da akwai wata sananniyar magana cewa, "Ka hada girar idonka, za ka fid da dabara." Watau, tunani da yawa na kawo basira. Domin mu kau da irin makanci mai tsanani da ke cikin Jam'iyyarmu, dole mu himmanta abokanammu su yi tunani, su koyi hanyar

binciken abubuwa kuma su sami halin bincike.

"Kan Nażari da Halin Da Ake ciki Yanzu" (12 ga Afril, 1944), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Idan a ko wace gudanarwar aiki da akwai saɓani da yawa, dole ɗayansu ya zama muhimmi wanda shi ke aikin gaba kuma yana aikin ƙudurawa, sauran kuwa a matsayi na biyu su ke suna taimakawa. Sabili da haka, in an zo nazarin ko wace rikitacciyar gudanarwar aiki wadda ke da saɓani biyu ko fiye da haka, dole mu yi iyakacin ƙoƙari wajen gane muhimmin saɓani. Muddin an fahimci wannan muhimmin saɓani, duk matsaloli za a warware su nan da nan.

"Kan Saɓani" (Agusta 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

A fannonin saɓani biyu, dole ne ɗaya ya zama muhimmi, ɗayan ko maras muhimmanci. Muhimmin fanni shi ne wanda ke aikin gaba a cikin saɓanin. Halittar abu,

ana ƙudura ta galibi bisa muhimmin fannin saɓani, fanni wanda ya fi samun mazauni mai ƙarfi.

Amma wannan hali ba tabbatacce ba ne, muhimmin fanni da maras muhimmanci na saɓani su kan sauya, wannan ya karɓi gurbin wannan, kuma halittar abin na sauyawa bisa haka.

"Kan Saɓani" (Agusta 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Bai isa ba kaɗai mu ba da ayyuka, dole kuma mu warware matsalar hanyoyin aikata su. In aikimmu ne mu ƙetare kogi, ba za mu ƙetare ba im babu kadarko ko jirgi. Im ba a warware maganar kadarko ko ta jirgi ba, zancen iska ne a yi maganar ƙetare kogin. Muddin ba a warware matsalar hanyar aiki ba, maganar aiki ba ta da amfani.

"A Lura Da Zaman Jama'a, A Maida Hankali ga Dabarun Aiki" (27 ga Janairu, 1934), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

A ko wane aiki, im ba a yi babbar kira ga kowa ba, ba za a ta da ɗimbin jama'a ga yi ba. Amma im mutanen da ke muƙamin shugabanci sun zauna ne kawai ga babbar kirar — in su da kansu a waɗansu ƙungiyoyi ba su shiga aikin da aka yi kira a kai da gaske ba, su ci nasara a wani fanni, su sami fasaha su yi amfani da fasahar domin ja gorar wasu ƙungiyoyi — to, ba za su sami wata hanya ta jarraba daidaicin kira ga kowa ko ingantar ma'anarta ba, kuma da haɗarin babu abin da za a ƙulla.

> "Wasu Maganganu game da Dabarun Shugabanci" (1 ga Yuni, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Babu wani a muƙamin shugabanci da ya isa ba da babban umurnin aiki ga dukan ƙungiyoyi im ba tare da ya sami fasahar gaske daga wasu mutane ko wasu abuba a wasu ƙungiyoyi da ke ƙarƙashinsa ba. Wannan hanya dole a yaɗa ta ko ina domin

ma'aikatan hukuma da ke muƙamin shugabanci na ko wane mataki su koya su yi amfani da ita.

> "Wasu Maganganu game da Dabarun Shugabanci" (1 ga Yuni, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

A ko wane wuri, ba za a ba da muhimman ayyuka da yawa ba a lokaci ɗaya. A ko wane lokaci, sai a sami aiki ɗaya babba da wasu marasa nauyi ko muhimmanci masu taimakawa. Sabo da haka, mutumin da ke ɗauke da dukan ɗawainiyar wurin dole ya dubi tarihi da halaye na famar wurin, kuma ya sa ayyuka daban daban ɗin nan a wuraren da suka dace da su, bai kamata ba ya yi aiki bisa umurni yadda ya zo masa daga ƙungiyar da ke bisansa ba tare da nasa shiri ba, har ya ƙago "manyan ayyuka" da yawa ya sukukunta kome. Haka kuma ƙungiyar da ke bisa bai kamata ta ba da ayyuka da yawa a lokaci ɗaya ba

ga ƙungiyoyin da ke ƙarƙashinta ba tare da nuna irin muhimmancinsu da gaggawar yinsu ba ko kuma ba tare da nuna wane ne muhimmi ba, domin wannan zai rikita hanyoyin da ƙungiyoyin da ke ƙarƙashinta za su ɗauka a ayyukansu, kuma babu wani abu takamaimai da za a samu. Fasaha ɗaya ce ta shugabanci a ga an dubi dukan halin wuri, kuma a yi shiri bisa halayen tarihi da irin halaye da a ke ciki a ko wane wuri, a tsai da shawara sosai kan muhimmin abu cikin aiki da irin shirin aiki na ko wane lokaci, kuma a tsaya a yi aiki da shawarar domin dole a sami tabbatacciyar aƙiba.

"Wasu Maganganu game da Dabarun Shugabanci" (1 ga Yuni, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Hedkwatar jiha ko ƙaramar hedkwatar jiha ta Kwamitin Tsakiya na Jam'iyya dole ta rika fahimtar ci gaban aiki kullum, ta yi musayar fasaha ta gyara kuskure, bai kamata

ba ta ɗakata sai bayan watanni, ko rabin shekara ko shekara sukutum kafin a yi taron dudduba ayyukan da aka yi domin bincike da gyara kuskure gaba ɗaya. Jira na kai ga babbar ɓarna, amma gyara kuskure lokacin da ya auku yana rage ɓarna.

"Kan Tsarin Manufar Siyasa game da Masana'antu da Ciniki" (27 ga Fabrairu, 1948), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Kada ka jira sai matsaloli sun jibgu kuma sun rikitu kafin ka tasam ma warware su. Dole shugabanni su shiga gaban harka, ƙar su tsaya a baya.

Gabatarwa ga "Aikin Kwangila a Lokacin Noma" (1955).

Abar da mu ke bukata ita ce sha'awa amma da kwantacciyar zuciya, da kuma himma wajen aiki amma a shirye.

"Matsalolin Sihirin Shiri a Yakin Tawayen Sin" (Disamba 1936), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

23. BINCIKE DA NAZARI

Duk wadanda ke cikin aikin gaske dole su binciki halayen kungiyoyin da ke kasa. Irin wannan bincike wajibi ne musamman ga irin wadanda su ke da sanin-ka kawai amma ba su san ainihin halaye ba, im ba haka ba, ba za su iya hada sanin-ka da aiki ba. Ko da ya ke maganata cewa, "Babu bincike, babu hujjar magana", an ba'anta ta cewa wai "gurguwar fasaha ce " ("narrow empiricism"), har ila yau dai ban tuba da yin wannan magana ba, maimakon tuba ni har yanzu na nace cewa im babu bincike ba ya yi-wuwa a sami hujjar magana. Da akwai mutane da yawa wadanda "da saukarsu daga sirdi" sai su shiga hayaniya, su fid da ko wane ra'ayi, su kushe wannan, su la'anci wan-

can, amma a hakika, goma daga cikin goma na irinsu za su fadi ne. Domin irin wadannan ra'ayoyi ko kushe-kushen da ba a dora su bisa bincike sosai ba, ba kome ba ne sai shirmen jahilci. Sau bila'adadi Jam'iyyarmu ta sha wahala a hannayen irin wadannan "jakadun sarauta". Kuma irin wadannan "jakadun sarauta" suna kutsawa nan da can, ana ganinsu ko ina. Gaskiyar Stalin da ya ce, "sanin-ka zai zama maras manufa im ba a hada shi da aikin tawaye ba". Kuma yana da gaskiya da ya jaddada cewa "aiki na aukawa cikin duhu im ba a haskaka hanyarsa da sanin-ka na tawaye ba". Babu wanda za a lankaya masa suna mai "gurguwar fasaha" sai "gogan aiki" wanda ya fada cikin duhu, ya zama maras gobe, kuma ba shi da la'akari.

"Gabatarwa da Karin Bayani ga *Yin Bincike a Kauyuka*" (Maris da Afril 1941), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Uku.

Daukar irin wannan hali shi ne neman gaskiya daga lazumin abuba. "Lazumin abuba" su ne hakikanan abuban da ke da akwai, "gaskiya" kuma ana nufin dangantakarsu ta ciki, watau dokokin da ke mallakarsu, kuma "nema" ana nufin nazari. Dole mu fara daga halayen gaske na ciki da waje na ƙasa, na lardi, na gunduma ko na unguwa, kuma mu samu daga gare su dokokin da suke tare da su tun asali ba na zato ba, watau dole mu gane dangantakar ciki ta abubuwan da ke faruwa a gewaye da mu domin jagorarmu a aiki. Kuma domin mu yi haka, ba za mu dogara bisa zaton zuci ba, ko sha'awar ɗan lokaci, ko kan littattafan wofi, sai dai kan hakikanan abuban da ke da akwai, dole mu tattara abubuwa cikin tsanaki, kuma bisa sanannun ƙa'idodin Marksanci-Leninanci mu tsai da gaskantacciyar shawara daga gare su.

"Kyautata Nazarimmu" (Mayu 1941), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

A yi kamar "mutum na neman kama gwara ido rufe" ko kuma "makaho na neman kama kifi", ba a aiki cikin nitsuwa, a shiga surutun aku, a hakura da ƙaramin sani, irin wannan mummunar haliyar aiki wadda ta saɓa wa tushen ruhun Marksanci-Leninanci sosai, har yanzu da akwai ta tsakanin abokanai da yawa na Jam'iyyarmu. Marks, Engels, Lenin da Stalin sun koya mana cewa wajibi ne a nazarci halaye cikin nitsuwa kuma a fara daga hakikanan abubuwan da ke kewaye da mu ba daga bukatun tunanin zuci ba, amma abokanammu da yawa kai tsaye suke gocewa wannan gaskiya.

"Kyautata Nazarimmu" (Mayu 1941), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ba za ka iya warware wata matsala ba ko? To, zauna ka bincika halullukan da matsalar ke ciki yanzu da kuma tarihinta! Bayan ka bincike matsalar sosai, za ka san

yadda za ka warware ta. Ba a yanke magana kafin bincike, sai bayan bincike. Sai sauna kawai ke buga hankalinsa shi daya, ko tare da 'yam mutane, domin "samo hanyar warware matsala" ko "samo dabara" ba tare da yin wani bincike ba. Ya kamata a karfafa cewa haka ba zai kai ga samun hanyar warware matsala ko dabara mai kyau ba.

"A Ki Bautawa Littafi" (Mayu 1930).

Bincike za a kwatanta shi da watanni masu tsawo na ciki, kuma warware wata matsala a kwatanta shi da ranar haifuwa. A bincike wata matsala, kamar warware ta ne.

"A Ki Bautawa Littafi" (Mayu 1930).

Ya kamata a yi amfani da sanin-ka da dabaru na Marksanci-Leninanci wajen bincike da kuma nazari sosai cikin tsari na

hakikanan abubuwan da ke kewaye da mu. Ba za a yi aiki bisa sha'awa kurum ba, sai dai kamar yadda Stalin ya ce, a hada himmar tawaye da ainihin halin aikatawa.

"Kyautata Nazarimmu" (Mayu 1941), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Hanya daya kawai ta sanin halaye ita ce ta yin binciken zaman al'umma, watau a bincike halayen ko wane aji na zaman al'umma cikin gaskiya sosai. Ga wadanda ke ba da umurnin aiki, hanya mafi tushe ta sanin halaye ita ce ba da karfi kan wasu birane da kauyuka bisa shiri, kuma a yi amfani da tushen ra'ayi na Marksanci, watau hanyar karkasa aji, kuma a yi 'yam bincike-bincike sosai.

"Gabatarwa da Karin Bayani ga *Yin Bincike a Kauyuka*" (Maris da Afril 1941), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Taron neman gaskiya ba zai zama babba ba, mutane uku, biyar, bakwai ko takwas dai sun isa. Ya kamata a ba da lokaci sosai kuma a shirya yadda za a yi bincike, bayan haka, dole ko wane mutum shi da kansa ya yi tambayoyi, ya yi rubutu, kuma ya yi shawara da mahalartan taron. Sabili da haka, mutum ba zai iya yin bincike ba ko kuma ya iya yinsa sosai ba, in dai ba tare da cikakkiyar anniya da kuma himmar sa idanu ga jama'a da kishin sani ba, kuma ba tare da cire rawanin girman kai, a nuna shirin zama almajiri ba.

"Gabatarwa da Karin Bayani ga *Yin Bincike a Kauyuka*" (Maris da Afril 1941), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Gaskiyar rarraba sojoji na daga shawarwari sosai na kwamanda, shawarwarinsa sosai na daga abubuwan da ya gani sosai, abubuwan da ya gani sosai na daga irin leke sosai da ya wajaba da kuma tunani

bisa tsari kan irin abubuwan gaskiya da aka samu daga leken da aka yi. Ya yi amfani da dukan hanyoyin leke masu yiwuwa da suka wajaba, ya yi tunani bisa sanarwar da ya samu ta hanyar leke game da halin da makiyi ke ciki, ya bar totuwa ya rike kwaya, watau ya cire karya ya dauki gaskiya, ya fara daga daya zuwa ga daya, kuma daga waje zuwa ciki, daga nan ya dubi halayen wurinsa, ya yi nazarin dukan gefe biyu ya san dangantakarsu, daga nan ya zartad da ra'ayinsa ya sa niyya ya yi shirinsa. Wannan ita ce cikakkiyar hanyar sanin halin wuri da mashirin sihirin yaki zai bi kafin ya yi shirin sihirin yaki, ko shiri na babba ko karamin fada.

"Matsalolin Sihirin Shiri a Yakin Tawayen Sin" (Disamba 1936), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

24. DAIDAITA TUNANIN KUSKURE

Ko mun sami manyan nasarori sosai a aikimmu, babu wata hujjar da za ta sa mu martabad da kai. Kamilanci na taimaka wa mutum wajen ci gaba, amma alfahari mai da mutum baya ya ke. Ya kamata mu sa wannan gaskiya kullum a kwakwalwarmu.

> "Jawabin Bude Taro na Takwas na Wakilan Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (15 ga Satumba, 1956).

Da nasara, mai yiwuwa ne wadansu halaye su bullo a Jam'iyya, watau alfahari, son nuna kai kamar jarumi, ragwanci, kin ne-

man ci gaba, son dadi da kin ci gaba da zaman wuya. Da nasara, jama'a za su gode mana kuma tajirai za su fito su yi mana fadanci. Tabbataccen abu ne makiyi ba zai iya cimmu da makami ba. Amma fadancin tajirai na iya cin masu gurguwar niyya da ke cikin jerimmu. Mai yiwuwa ne cewa akwai wasu 'yan Kwaminis wadanda makiya ba su taba cinsu da makami ba, kuma sun cancanci a kira su jarumai domin bajintarsu a gaban makiyan nan, amma wadanda ba za su iya tsaya wa harsashi lullube da zuma ba, za a ci su da harsashi lullube da zuma. Dole mu kiyaye haka.

> "Rahoto ga Cikakken Zama na Biyu na Taro na Bakwai na Kwamitin Tsakiya na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (5 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Mai yiwuwa ne abubuwa da yawa su zamana kaya, su zamana kayan jidali, idan

mun like musu a makance kuma ba tare da lamiri ba. Ga wadansu misalai. Bayan kun yi kuskure, kila kuna jin ta ko wane hali zai zama muku kaya a ka, sai ku karaya. Idan ba ku shuka wani kuskure ba, mai yiwuwa ne ku ji cewa ku ba ku ßata har ya sa ku fariya. Rashin nasara cikin aiki na iya kawo bakin ciki da sarewa, kan kuwa nasara na iya kawo fariya da fadin rai. Mai yiwuwa ne aboki mai gajeren tarihi a fama ya guje wa daukar dawainiyar aiki a kan wannan, amma tsoho na iya tsaye wa ra'ayinsa domin dogon tarihin famarsa. Da ma'aikata da manoma masu alfahari da asalin ajinsu na iya raina 'yan ilmi, su 'yan ilmi kuwa sabili da wani dan guntun saninsu na iya raina ma'aikata da manoma. Duk wata gwanintar sana'a na iya zama jari mai sa fadin rai da raina wasu. Har ma shekaru na iya zama abin alfahari. Samari na iya raina tsofaffi sabo da basira da iyawarsu, su tsofaffi kuma domin suna cike da fasaha na iya raina samari.

Duk irin wadannan abubuwa na iya zama jidali ko kaya, idan babu lamirin kushewa.

"Kan Nazari da Halin Da Ake ciki Yanzu" (12 ga Afril, 1944), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Wadansu abokanai da ke aiki a rundunar soja sun zama masu fadin rai, suna rashin adalci ga sojoji, ga jama'a, ga gwamnati, ga Jam'iyya. Ba su zargin kansu sai abokanan da ke aiki cikin jama'a, ba su ganin aibinsu sai nasararsu. Ba su da jimirin sauraren kushewa sai kawai kaunar yabo suke. ... dole rundunar soja ta tashi tsaye sosai ta yaki wannan laifi.

"Ku Shirya Kanku!" (29 ga Nuwamba, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Aiki mai wuya kamar kaya ne a gabammu, da ke son mu dauke shi. Wadansu kayayyaki ba nauyi, wadansu ko akwai. Wasu

mutane sun fi son maras nauyi da mai nauyi, su zaɓi maras nauyi, su tura wa wasu mai nauyi. Wannan ba hali ne mai kyau ba. Waɗansu abokanai kuwa su kan nuna hali daban, suna bar wa wasu daɗi da sauki, su su ɗau nauyi. Su ne farkon fuskantar wahaloli, kuma su ne a baya wajen jin daɗi. Abokanan kirki ke nan. Ya kamata mu dukammu mu yi koyi da halinsu na kwaminisanci.

"Kan Shawarwarin Chungking" (17 ga Oktoba, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Da akwai mutane ba kaɗan ba waɗanda ba su da hankali cikin ayyukansu, sun fi son sauki, suna gudun wuya, kullum suna ɗora kayayyaki masu nauyi bisa waɗansu, su kuma suna zaɓam ma kansu marasa nauyi. Game da ko mene ne kansu suke fara tunawa kafin waɗansu. Idan kuma sun yi wani abu kaɗan, sai su kumbura da alfahari, su shiga yabon kai domin tsoron

kada a ce waɗansu ba su sani ba. Ba su damu da abokanai ko da jama'a ba, kullum suna sanyi-sanyi da mutane, ba ruwansu da kowa, ba su tausayi. A gaskiya dai irin waɗannan mutane ba 'yan Kwaminis ba ne, ko kuma a ƙalla dai ba za a kira su 'yan Kwaminis na kirki ba.

"Tunawa Da Norman Bethune" (21 ga Disamba, 1939), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Waɗanda ke nuna irin halin "'yanci" kullum ba su rabuwa da ra'ayin "ni ne na farko", galibi dai su kan yi kuskure wajen ɗaukar al'amarin dangantaka tsakanin mutum da Jam'iyya. Ko da ya ke a baka su ma su kan ba Jam'iyya girma, amma ta aikatawa su kan sa kansu a matsayi na farko kuma Jam'iyya na biyu. Mene ne waɗannan mutane ke biɗa? Suna biɗar martaba, matsayi, suna son ta da kai. Lokacin da suka ɗauki ɗawainiyar wani sashen aiki, sai su shiga biɗar "'yanci". Da wannan

nufi, suna jawo wadansu a jiki, su gefantad da wadansu, su shiga amfani da fahari da fadanci da lallashi cikin abokanai, suna kawo munanan halaye na jam'iyoyin siyasar tajirai cikin Jam'iyyar Kwaminis. Rashin gaskiyarsu ke sa su shan wahala. A ganina, ya kamata mu yi aiki cikin gaskiya. Domin im babu halin gaskiya, ko kusa ba abin da za mu iya aikatawa a duniyan nan.

"Gyara Haliyar Aiki ta Jam'iyya" (1 ga Fabrairu, 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Dole ne duk dan Kwaminis ya fahimci wannan gaskiya cewa wajibi ne a sa bukatar wani ɓari bayan ta sukutum. Idan wata shawara ta dace da halin ɓari, amma ba da sukutum din hali ba, ya kamata ɓarin ya ba sukutum din hanya. A akasin haka, idan wata shawara ba ta dace da halin ɓarin ba amma ta dace da halin sukutum din, a nan ma ya kamata ɓarin ya ba sukutum din han-

ya. Wannan shi ne abin da a ke nufi da kula da sukutum din hali.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Son bidi'a. A Jar Rundunar Soja da akwai mutane ba kadan ba wadanda son kansu ya kan bayyanu ta son bidi'a. Kullum fata suke sojojinsu su shiga kosassun birane. Suna son zuwa can ba don aiki ba sai domin jin dadin kansu kawai. Abin da ba su so sam shi ne su yi aiki a Jajayen jihohi inda sharudan rayuwa ke da wuya.

"Kan Daidaita Ra'ayin Kuskure a cikin Jam'iyya" (Disamba 1929), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Ya kamata mu yaki hali na "mu-kula-da-sashemmu-kawai" (departmentalism)

wanda ke sa mutum kula da abin moriyar sashensa kawai, ban da na sauran sassa. Duk wanda ba ruwansa ga wahalolin wadansu, yana kin tura ma'aikatan sashensa ga wasu sassa da ke bukata, ko ya aika musu da marasa karfi, watau "yana ganin gonar makwabci kamar kwararon ruwansa", kuma ba ya dan kula da sauran sassa, wurare ko jama'a — irin wannan mutum dan "mu-kula-da-sashemmu-kawai" ne, wanda ya bad da halin kwaminisanci duka-duka. Rashin tunanin abin sukutum din da kin kula da sauran sassa, wurare ko jama'a, su ne halaye na 'yam "mu-kula-da-sashemmu-kawai". Ya kamata a kara tarbiyyar mutanen nan domin su fahimci cewa "mu-kula-da-sashemmu-kawai" hali ne na rukunanci wanda idan am bar shi ya ci gaba zai zama hatsari.

"Gyara Haliyar Aiki ta Jam'iyya" (1 ga Fabrairu, 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Libaralisanci na bayyana kansa a hanyoyi dabam daban.

A bar abubuwa su wuce hakanan domin son lafiya da abokantaka, alhali kuwa mutum ya yi kuskure a fili, kuma a ki muhawara bisa ka'ida domin mutumin wani tsohon idon sani ne, ko mutumin gari, ko abokin makaranta, ko aminin sosai, ko masoyi, ko tsohon abokin aiki, ko wani na karkashin mutum a da. Ko kuma a taɓo maganar sama-sama maimakon neman tahakikin yadda za a daidaita ta, domin son zaman lumana da kowa. Karshen abin shi ne da kungiya da mutum duka sai a lahanta su. Wannan shi ne hali na farko mai bayyana libaralisanci.

A ɓoye sai a shiga sukar banza da wofi maimakon a kokarta kawo shawara a gaban kungiya. A gaban jama'a a yi shiru, amma in am ba da baya, sai ka ji ana ta tsegumi. Ko kuma ba a cewa kome a gun taro, amma in an tashi sai ka ga ana ta tsegumi. Ba a nuna kula ko kadan da ka'idodin rayuwar

tarayya sai yin abin da aka ga dama. Wannan shi ne hali na biyu.

A bar abubuwa su wuce idan ba su shafi mutum shi kansa ba, a yi magana kaɗan alhali kuwa an sani lalle da akwai abin da ya ɓace, a kasance ana da wayo sosai, a iya wasan ɓuya domin kawai a kauce wa laifi. Wannan shi ne hali na uku.

Ba a bin umurni, ra'ayin kai ne a ke ɗorawa bisan kome. Sai amfani a ke nema daga ƙungiya, amma ba a son ladabinta. Wannan shi ne hali na huɗu.

A shiga suka, neman faɗa, nuna ƙin jini ko kuma neman ramako maimakon shiga cikin muhawara da fama bisa ra'ayin kuskure domin haɗin kai ko ci gaba ko samun a yi aiki sosai. Wannan shi ne hali na biyar.

Ba a ƙaryata ra'ayoyin da ba daidai ba in an ji su, har ma a kan bar maganganun 'yan ƙin tawaye su wuce ba a shaidawa, maimakon haka, sai a ɗauke su hankali

a kwance kamar ba abin da ya faru. Wannan shi ne hali na shida.

Mutum na tare da jama'a, amma ba ya yin furofaganda da himmanta su, ba ya yin zantuttuka ko yin bincike ko kuma yin tambayoyi a cikin jama'a, maimakon haka ya yi ba ruwansa kuma ya ƙi kula da wahalolin jama'a, ya manta cewa shi ɗan Kwaminis ne, ya shiga yi kamar wani mutum hakanan kawai ba ɗan Kwaminis ba ne. Wannan shi ne hali na bakwai.

Ana ganin wani da laifin cutar bukatun jama'a amma ba a gwada ɓacin rai, ba a tsawata masa, ba a hana shi, ba a nuna masa dalilai sai kawai a bar shi yana aikatawa. Wannan shi ne hali na takwas.

Ba a aiki cikin nitsuwa, babu wani shiri ko hanyar da za a bi a aiki, haka ɗai kawai ana yi babu wata himma, kamar ɗai a ce, "Muddin mutum ɗan Buddha ne, sai ya yi ta ci gaba da buga ƙararrawa". Wannan shi ne hali na tara.

Zato a ke an amfani tawayen turu sai a shiga homa kamar tsohon hannu. Ba a iya gawurtattun ayyuka amma ana raina kananan ayyuka, ba a sa hankali cikin aiki kuma ana sa kasala ga nazari. Wannan shi ne hali na goma.

An san an shuka laifi, amma ba a son gyararsa, mutum yana nuna wa kansa halin shagwaɓa. Wannan shi ne hali na goma sha daya.

"Kin Libaralisanci" (7 ga Satumba, 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Libaralisanci abu ne mai lahani ainun a cikin kungiyar tarayyar tawaye. Tsatsa ce wadda ke raunana hadin kai, tana sassauta zumunta, tana kawo kyuya da kitiko. Tana hana jerin tawaye yin shiri mai kwari da biyayyar gaske, tana hana tafiyar da manufar siyasa sosai kuma tana ɓare kungiyoyin Jam'iyyar daga jama'ar da Jam'iyyar ke ja

wa ragama. Wannan mummunan hali ne ainun.

"Kin Libaralisanci" (7 ga Satumba, 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Mutanen da ke da ra'ayin libaralisanci na duban ka'idodin Marksanci kamar darikar mafarki (abstract dogma). Sun yarda da Marksanci, amma ba a shirye su ke wajen aikata shi ko kuwa su aikata shi gaba daya ba, ba a shirye su ke su bar libaralisancinsu su dau Marksanci ba. Su wadannan mutane suna da Marksanci nasu, haka kuma suna da libaralisanci nasu, watau suna maganar Marksanci, amma libaralisanci su ke aikatawa. Su kan yi amfani da Marksanci ga wasu, amma ga kansu sai libaralisanci su ke aikatawa. Sun tanada dukan kaya iri biyu, ko wane na da nasa aikin. Wan-

nan shi ne yadda hankulan wadansu irin mutane ke aiki.

"Kin Libaralisanci" (7 ga Satumba, 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Hukumar kasar jama'a ke tsaron jama'a. Sai kawai lokacin da jama'a ke da irin wannan hukuma, za ta iya amfani da hanyoyin dimakuradiyya wajen yin tarbiyyar kanta da sauya kanta a duk kasar tare da halartar kowa da kowa, ta kakkabe tasirin azzaluman gida da na waje (har yanzu dai tasirin na da babban karfi kuma zai jima, ba za a iya rusa shi nan da nan ba), ta yi banza da munanan tsabi'o'i da ra'ayoyin da aka samu daga tsohon zaman al'umma, kada ta yarda azzalumai su ja ta zuwa hanyarsu ta kuskure, kuma ta yi ta ci gaba ta doshi zaman gurguzu da zaman kwaminisanci.

"Kan Mulkin Shibtar Dimakuradiyyar Jama'a" (30 ga Yuni, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ba abin wuya ba ne ga mutum ya yi kyakkyawan abu kadan, abu mai wuya shi ne a duk wanyewar rayuwar mutum a duniya ya yi ta kyawawan abubuwa ba tare da yin wani abu maras kyau ba, ya rika aiki a kai a kai sabo da bukatun dimbin jama'a da samari da tawaye, kuma ya shiga mawuyaciyar fama ta shekaru gommai kamar dai bajintakar da zai nuna a yini guda. Wannan shi ne abu mafi wuya sosai a abubuwa duka!

"Sakon Gaisuwa don Cikon Shekaru 60 da Haihuwar Aboki Wu Yu-chang" (15 ga Janairu, 1940).

25. HADIN KAI

Gama kan ƙasarmu, hadin kan jama'armu da hadin kan duk kabilun ƙasarmu, su ne abin jingina mai digi ga tabbatacciyar nasarar sha'animmu.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Sai ta hadin kan Jam'iyyar Kwaminis kawai ne za a iya tabbatad da hadin kan duk aji da na al'umma baki daya, kuma sai ta hadin kan duk aji da na al'umma baki daya ne za a iya cim makiya, a cika aikin tawayen al'umma da na dimakuradiyya.

"Mu Yi Fama domin Jawo Miliyoyin Jama'a Su Shiga Hadadden Goshin Famar Al'umma na Kiyewa Japan" (7 ga Mayu, 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Za mu hallara duk ƙarfin Jam'iyyarmu sosai bisa ƙa'idodin shirin ƙungiya da biyayya na dimakuradiyya-tattarawa. Za mu hada kai da ko wane aboki, muddin dai ya yi biyayya ga tsari, ka'idodi da zartattun shawarwari na Jam'iyya.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Wannan hanyar dimakuradiyya ta daidaita sabani tsakanin jama'a, a 1942 muka saukaka ta cikin wani kamanni haka (formula), "hadin kai——kushewa——hadin kai". A filla-filla dai ana nufin a fara da burin neman hadin kai kuma a daidaita sabani ta hanyar kushewa ko fama, kana a kai ga sabon hadin kai bisa sabon digi. Bisa fasahar da muka samu, wannan gaskantacciyar hanya ce wajen daidaita sabani tsakanin jama'a.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a"(27 ga Fabrairu, 1957).

Wannan rundunar soja ta samu kyakkyawan hadin kai a cikinta da ita. A cikin rundunar da akwai hadin kai tsakanin hafsoshi da kananan sojoji, tsakanin na gaba da mabi masa, da kuma tsakanin aikin soja, aikin siyasa da aikin bautawa soja. Kuma a waje da akwai hadin kai tsakanin rundunar soja da jama'a, tsakanin rundunar soja da hukumomi da kuma tsakanin rundunar sojammu da rundunar sojan da ke aminci da mu. Duk abin da zai lahanta wannan hadin kai, dole a soke shi.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

26. BIYAYYA

A cikin Jama'a, dimakuradiyya tana dangantaka da tattarawa, haka zalika 'yanci da biyayya. Su kishiyoyi biyu ne da ke cikin sukutum din abu, da sabani tsakaninsu kuma da hadin kai tsakaninsu, bai kamata ta fanni daya mu karfafa daya kawai mu musanta dayan ba. A cikin jama'a, ba ya yiwuwa ba tare da 'yanci ba, haka kuma ba ya yiwuwa ba tare da biyayya ba. Ba ya yiwuwa ba tare da dimakuradiyya ba, haka kuma ba ya yiwuwa ba tare da tattarawa ba. Wannan haduwa ta dimakuradiyya da tattarawa, ta 'yanci da biyayya ita ce tsarimmu na dimakuradiyya-tattarawa. A karkashin irin wannan tsari, jama'a suna cim moriyar fadaddun dimakuradiyya da

'yanci, kuma a lokacin nan ya kamata jama'a ta tsaya cikin haddin biyayyar gurguzu.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Ya kamata a sake jaddada biyayyar Jam'iyya watau: (1) mutum ya yi biyayya ga kungiyarsa, (2) tsirarrun mutane su yi biyayya ga yawancin mutane, (3) kananan kungiyoyi su yi biyayya ga manyan kungiyoyi, (4) Jam'iyya gaba daya ta yi biyayya ga Kwamitin Tsakiya. Duk wanda ke taka wannan dokar biyayya, yana lahanta hadin kan Jam'iyya ke nan.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Daya daga cikin ka'idodin biyayya na Jam'iyya ita ce tsirarrun mutane su yi biyayya ga yawanci. Idan an ki yarda da ra'ayin tsirarrun mutane, dole ne su goyi

bayan shawarwarin da yawancin mutane suka zartas. Idan dai ya zama dole, ana iya sake gabatar da matsalar a taro mai zuwa, amma ban da wannan, ko ta yaya ba a yarje a yi wani abu wanda ya lahanta shawarwarin da aka zartas.

"Kan Daidaita Ra'ayin Kuskure a cikin Jam'iyya" (Disamba 1929), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Manyan Dokoki Uku na Biyayya su ne:

(1) Ku bi umurnai a dukan ayyukanku.

(2) Kada ku dauki allura daya ko silin zare daga jama'a.

(3) Ku kai wa mahukunta duk abin da kuka samu daga wajen yaki.

Ga Ka'idodi Guda Takwas na Lura:

(1) Ku yi magana cikin ladabi.

(2) Duk abin da kuka saya ku biya daidai kudinsa.

(3) Ku mai da duk abin da kuka ara.

(4) Ku biya duk abin da kuka bata.

(5) Kada ku bugi ko ku zagi mutane.

(6) Kada ku yi wa amfanin gonakai ßarna.

(7) Kada ku sakarce wa mata.

(8) Kada ku wulakanta 'yam fursunan yaƙi.

> "Umurnin Da Babbar Hedkwatar Rundunar Sunce Jama'ar Sin Ta Yi game da Sake Gabatar da Manyan Dokoki Uku na Biyayya da Ka'idodi Guda Takwas na Lura" (10 ga Oktoba, 1947), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Ya kamata su (hafsoshi duka da ƙananan sojoji na rundunarmu) ƙarfafa halin biyayya, su tsaya ga gudanad da umurnai, su tafiyar da tsarin manufar siyasa, su àikata Manyan Dokoki Uku na Biyayya da Ka'idodi Guda Takwas na Lura, su tabbata haɗin ƙai tsakanin runduna da jama'a, haɗin kai tsakanin runduna da hukuma, haɗin kai tsakanin hafsoshi da ƙananan sojoji da haɗin kan duk rundunar, ba a yarda da wani abu wanda zai lahanta biyayya.

> "Sanarwar Rundunar Sunce Jama'ar Sin" (Oktoba 1947), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

27. KUSHE DA KUSHEWA KAI

Jam'iyyar Kwaminis ba ta tsoron kushe, domin mu 'yan Marksanci ne, gaskiya na tare da mu, galibin jama'a — ma'aikata da manoma na tare da mu.

> "Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

'Yan materiyalisanci na gaske ba su tsoron kome, muna fata dai dukan abokanan famarmu za su yi ƙarfin halin ɗaukar dukan ɗawainiyoyinsu, su haye dukan wahaloli, kar su ji tsoron ko ßacin rana, ko ba'a, kuma kar su ji tsoron a kushe mana mu 'yan Kwaminis kuma a ba mu shawara.

"Wanda ba ya jin tsoron sara da takobi na iya ture sarki daga sirdi", wannan jan hali ne wanda ya kamata mu nuna wajen famarmu don gina gurguzu da kwaminisanci.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

Muna da makamin Marksanci-Leninanci na kushe da na kushewa kai. Muna iya tsame kammu daga halaye marasa kyau, mu rike masu kyau.

"Rahoto ga Cikakken Zama na Biyu na Taro na Bakwai na Kwamitin Tsakiya na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (5 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Kushewa kai ko rashin yinsa cikin gaskiya, wannan ma wani babban zane ne mai bambanta Jam'iyyarmu da sauran jam'iyoyin siyasa. Kamar yadda muka taba cewa,

ya kamata mu share dakimmu a kai a kai, idan ba haka ba kura za ta taru, ya kamata mu wanke ido kullum, idan ba haka ba fuskarmu za ta yi dauda. Haka ma tunanin abokanammu da aikin Jam'iyyarmu su ma suna iya daukar kura, sabo da haka suna bukatar shara da wanki. Karin maganar nan "Ruwa mai gudu ba ya doyi, kuma almananin kofa ba ya rubewa" na nufin motsi ko da yaushe na hana 'yan kananan halitta da sauran kwari yin barna. A gare mu, mu rika binciken aikimmu, kuma cikin binciken nan muna yada halin dimakuradiyyar aiki, kada mu ji tsoron kushe da kushewa kai, mu yi amfani da karin maganganun nan na Sinnawa masu amfani ainun kamar su "Ka fadi duk abin da ka sani, kada ka boye kome", "Mai magana ba shi da laifi, ya kamata masaurari ya mai da maganganun kamar gargadi", kuma "Idan kana da kuskure ka gyara, idan ba ka da shi, to, ka kiyaye yinsa" — wannan hanya ce daya tilo mai amfani wajen hana dukan

irin kurar siyasa da 'yan kananan halittar siyasa su yi wa hankulan abokanammu da jikin Jam'iyyarmu ßarna.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Kiyayya da fama tsakanin ra'ayoyi daban su kan faru a cikin Jam'iyyz, wannan ita ce inuwa, cikin Jam'iyya, mai nuna saßani tsakanin ajujuwa da saßani tsakanin sabo da tsoho a zaman al'umma. Idan cikin Jam'iyya babu saßani da famar tunani ta daidaita saßani, to, sai Jam'iyya ta wargaje.

"Kan Saßani" (Agusta 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

A himmance mu ke tsaye ga famar tunani domin makami ne mai tabbatad da hadin kai a cikin Jam'iyya da rukunan tawaye don amfani ga famarmu. Ya kamata ko wane dan Kwaminis da dan tawaye ya dau wannan makami a hannu.

Amma libaralisanci shi yana kin famar tunani kuma ya tsaya wa jituwa ba tare da wata ka'ida ba, daga nan ya kawo lalacewar hali kuma ya kawo susucewar siyasa ga wasu kungiyoyi da wasu mutane a cikin Jam'iyya da rukunan tawaye.

"Kin Libaralisanci" (7 ga Satumba, 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

A cikin famarmu ta kin tunanin zuci, rukunanci da tsohuwar hanyar Jam'iyya ta kwaikwayon rubutu (stereotyped Party writing), ya kamata mu lura da ka'idodi biyu, ta farko "samun darasi daga kuskuren da ya shige domin gudun maimaita shi", ta biyu kuma "a warkar da cuta domin tsirad da maras lafiya". Dole a tone duk kuskuren da aka shuka a da ba tare da jin kunyar mutum ba, ya kamata a yi bincike da kushewa abu maras kyau na da ta hanyar kimiyya, domin gobe a fi mai da hankali ga aiki kuma a yi shi da kyau. Wannan

ita ce ma'anar "samun darasi daga kuskuren da ya shige domin gudun maimaita shi". Amma burimmu na tone laifuffuka a fili da kushewa aibi, kamar yadda likita ke warkar da maras lafiya, shi ne kawai don ceton rai amma ba don kashe shi ba. Mai cutar tsiro a ciki na tsira, idan likita ya cire masa tsiron. Duk wanda ya yi laifi, in dai bai ɓoye cutarsa ba domin tsoron warkarwa, ko bai nace da yin kuskure har ya wuce gaban warkarwa ba, idan dai da gaske ya nuna son magani da son gyara, za mu yi maraba da shi kuma mu warkar da shi domin ya zama aboki na kirki. Har abada ba za mu iya nasara a aikimmu ba, idan wani abu ya kwashe mu mun yi hanzarin la'antarsa. Wajen warkar da cutar tunani da ta siyasa, dole a kiyaye halin ketare, amma dole ne a ɗauki halin "a warkar da cuta domin tsirar da maras lafiya", wannan hanya ita ce kawai ta gaskiya kuma mai amfani.

"Gyara Haliyar Aiki ta Jam'iyya" (1 ga Fabrairu, 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Game da maganar kushewa cikin Jam'iyya, wani abu da ya kamata a jaddada shi ne waɗansu abokanai a cikin kushewarsu ba su sa hankali ga muhimman abubuwa sai kawai ga ƙananan abubuwa. Ba su fahimci cewa muhimmancin aikin kushewa shi ne a fidda kuskuren siyasa da na shirin ƙungiya a fili ba. Game da aibin wani mutum shi kansa, in dai bai shafi kuskuren siyasa da na shirin ƙungiya ba, bai kamata ba a yi suka fiye da kima domin gudun kada abokanai su rasa abin da za su yi. Kuma idan irin wannan kushewa ta yi yawa, da akwai babban haɗari cewa cikin Jam'iyya sai kan ƙananan aibobi ne kawai za a fi mai da hankali, kuma sai abokanai su zama matsorata masu hankali fiye da kima, har su manta ayyukan siyasa na Jam'iyya.

"Kan Daidaita Ra'ayin Kuskure a cikin Jam'iyya" (Disamba 1929), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Wajen kushewa cikin Jam'iyya, ya kamata a kiyaye tunanin zuci da ha'inci da kushewar banza da wofi, ya kamata a yi maganganu bisa gaskiya kuma a fi ba da karfi kan fannin siyasa wajen kushewa.

"Kan Daidaita Ra'ayin Kuskure a cikin Jam'iyya" (Disamba 1929), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Kushewa cikin Jam'iyya, makami ne mai karfafa kungiyar Jam'iyya da kuma inganta karfin fadanta. Amma a cikin kungiyar Jam'iyya ta Jar Runduna, wani gami ma kushewa ba a wannan hali ta ke kullum ba, ta kan zama suka tsakanin mutum da mutum. Ta haka ba kawai lahantar mutum a ke ba har da kungiyar Jam'iyya. Wannan bayyanar son kai ce ta ajin kananan tajirai. Hanyar gyara wannan ita ce a taimaki 'yan Jam'iyya su gane cewa burin kushewa shi ne a inganta karfin famar Jam'iyya domin samun nasara a famar aji, kuma

bai kamata a yi amfani da kushewa kamar hanyar suka tsakanin mutum da mutum ba.

"Kan Daidaita Ra'ayin Kuskure a cikin Jam'iyya" (Disamba 1929), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Idan muna da aibobi, ba mu tsoron a nuna mana kuma a kushe mana, domin jama'a mu ke bautawa. Ko wane ne yana iya nuna mana aibobimmu. Idan dai abin da ya ce daidai ne, sai mu gyara. Idan shawarar da ya gabatar ta amfana wa jama'a ce, sai mu yi aiki da ita.

"Bautawa Jama'a" (8 ga Satumba, 1944), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Mu, 'yan Kwaminis Sinnawa wadanda ke fara kome bisa manyan bukatun dimbin jama'ar Sin, muna cike da imani cewa sha'animmu mai adalci ne sosai, ba mu shakkar sadakar da kome namu, kuma a shirye mu ke a ko wane lokaci wajen ba da rayukammu domin

sha'animmu, ashe da akwai wani tunani, ra'ayi, ko shawara ko kuma wata dabara wadanda ba su dace da bukatun jama'a ba, da ba za mu iya rabuwa da su ba? Ashe za mu iya yarda da wata kurar siyasa da 'yan kananan halittar siyasa su zo su kazanta mana tsabtataccivar fuskarmu ko su yi wa jikimmu mai lafiya barna? Dimbin jarumai na tawayemmu sun sadakad da rayukansu domin abin moriyar jama'a, kuma mu masu rai zukatammu na cike da bakin ciki lokacin da mu ke tunaninsu. Ashe da akwai wani abin moriyar kai da ba za mu iya sadakarwa ba, ko da akwai wani laifi wanda ba za mu iya wurgarwa ba?

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ko ta wane hali bai kamata ba mu yi girman kai sabo da ko wace nasara. Ya kamata mu ci karfin girman kai, mu kushe wa aibimmu kullum kamar dai yadda mu

ke wanke fuska ko share daben daki ko wace rana domin fidda kura da tsare tsabta.

"Ku Shirya Kanku!" (29 ga Nuwamba, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Game da kushewa ya kamata a yi ta cikin lokaci. Kar a fada cikin halin kushewa bayan wakanar abu.

"Kan Al'amarin Gama Gwiwa wajen Noma" (31 ga Yuli, 1955).

Kuskure da wahaloli sun koyar da mu, kuma sun sa mun kara zama wayayyu kuma mun kara kyautata aikimmu. Da wuyar kaucewa kuskure ga ko wace jam'iyyar siyasa da ko wane mutum, amma ya kamata mu rika yin kalilan. Idan an shuka kuskure, fata mu ke a gyara, gyara shi da wuri-wuri kuma sosai, zai fi kyau.

"Kan Mulkin Shibtar Dimakuradiyyar Jama'a" (30 ga Yuni, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

28. 'YAN KWAMINIS

Ya kamata duk dan Kwaminis ya zama mafadin gaskiya, maras ha'inci kuma mai himma, ya dubi bukatun tawaye fiye da ransa kuma ya jingina bukatunsa ga bukatun tawaye. Ya kamata ko yaushe kuma ko ina ya tsaya ga gaskantattun ka'idodi, ya sa famar da ba fashi kan duk ra'ayi da aikatawa na kuskure, domin karfafa rayuwar tarayya ta Jam'iyya da karfafa zumunci tsakanin Jam'iyya da jama'a. Ya kara kula da Jam'iyya da jama'a fiye da mutum daya, kuma ya rika kula da saura fiye da shi kansa. Ta haka ne kawai zai cancanci sunan dan Kwaminis.

"Kin Libaralisanci" (7 ga Satumba, 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ya kamata a fahimtad da ko wane aboki cewa duk maganganu da duk ayyuka na dan Kwaminis, muhimmiyar shaidarsu ta farko ita ce ko sun dace da manyan bukatun jama'a mafiya yawa kuma sun sami goyon bayansu.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

A ko da yaushe kuma a ko ina, bai kamata ba dan Kwaminis ya sa bukatun kansa gaba da kome, sai dai ya mai da su a karkashin bukatun kasa da na jama'a. Sabo da haka, son kai da yin kasala a aiki, cin hanci da lalacewa, neman tada kai da sauransu, abubuwa ne na banzatarwa kwarai da gaske, kan kuwa rashin son kai da aiki da kwazo, bautawa aikin jama'a da zuciya daya, yin aiki mai wuya cikin tsanaki, abubuwa ne da za a girmama su.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Dole dan Kwaminis kullum ya shirya ya tsaya ma gaskiya, domin kuwa ko wace gaskiya tana dacewa da bukatun jama'a. Dole dan Kwaminis kullum ya shirya ya gyara laifuffukansa, domin duk laifuffuka ba su dacewa da bukatun jama'a.

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Dole dan Kwaminis ya yi wa kansa tambaya game da ko wane abu da ya gani, dole ya yi amfani da fwafwalwarsa ya yi tunani cikin nitsuwa, ya ga ko ya dace da hakika ko yana da dalilan gaske. Ko ta wane hali, bai kamata ba ya bi shi a makance har ya ba da farfi ga halin bauta.

"Gyara Haliyar Aiki ta Jam'iyya" (1 ga Fabrairu, 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ya kamata a himmantad da ko wane aboki wajen kula da bukatun sukutum din kome. Ko wane dan Jam'iyya, ko wane sashen aiki, ko wace magana da ko wane aiki, dole ne masominsu ya zama bukatun duk Jam'iyya. Ko da sunan wasa ba a yarda a karya wannan fa'ida ba.

"Gyara Haliyar Aiki ta Jam'iyya" (1 ga Fabrairu, 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ya kamata 'yan Kwaminis su zama abin koyi wajen aikatawa cikin gaskiya da kuma hangen nesa. Domin sai ta hanyar aikatawa cikin gaskiya ne kawai za su iya cika dawainiyar da aka dokace su, kuma sai hangen nesa ne kawai zai hana su βatar kai a tafiyarsu ta yin gaba.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yafin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ya kamata 'yan Kwaminis su zama mafiya hangen nesa, mafiya sadakarwa, mafiya tsayewa da kuma mafiya iya gane matsala ba tare da ra'ayin zato ba, ya kamata su dogara ga yawancin jama'a kuma su sami goyon bayansu.

> "Ayyukan Jam'iyyar Kwaminis ta Sin a Lokacin Yakin Kare Harin Japan" (3 ga Mayu, 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

'Yan Kwaminis ya kamata su ba da misali wajen nazari. Ko wace rana ya kamata su zamana malaman jama'a haka kuma almajiransu.

> "Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

A cikin harkar jama'a, ya kamata dan Kwaminis ya zamana aminin jama'a amma

ba babba a bisansu ba, ya zama malami mai matukar kokarin koyarwa amma ba dan siyasa mai nuna halin hakimci ba.

> "Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Bai kamata ba har abada 'yan Kwaminis su ware kansu daga yawancin jama'a kuma su kyale matsalarsu, su shugabanci rukunan 'yan tsirarru masu ci gaba kawai su yi hanzarin ci gaba su kadai. Dole su kula da kafa zumunta sosai tsakanin masu ci gaba da sauran dimbin jama'a. Wannan shi ne abin da a ke nufi da kula da yawanci.

> "Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Mu 'yan Kwaminis kamar iri ɗaya ke, jama'a kuwa kamar gandu. Duk inda muka

je, tilas mu cudu da jama'ar wurin, mu kafu kamar saiwa kuma mu tofu tsakaninsu.

"Kan Shawarwarin Chungking" (17 ga Oktoba, 1945), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Game da kome, ya kamata mu 'yan Kwaminis mu iya cuduwa da jama'a. Idan 'yan Jam'iyyarmu a duk rayuwarsu, a kulle su ke cikin dakunansu, ba su taba fita su fuskanci duniya, su shiga hadari ba, me za su tsinana wa jama'ar Sin? A'a, ko kusa, ba mu bukatar irin wadannan mutane su zama 'yan Jam'iyyarmu. Ya kamata mu 'yan Kwaminis mu fuskanci duniya kuma mu shiga hadari, watau babbar duniya da babban hadari na famar jama'a.

"Ku Shirya Kanku!" (29 ga Nuwamba, 1943), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Aikin maduganci na 'yan Kwaminis da misalin da su ke bayarwa na da kasaitac-

cen muhimmanci. 'Yan Kwaminis ya kamata su ba da misali a Rundunar Hanya ta Takwas da Sabuwar Runduna ta Hudu wajen jarumtakarsu a fada, idad da umurni, yin biyayya, gudanad da aikin siyasa da kara karfafa hadin kan ciki da zumunta.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ko kusa bai kamata ba dan Kwaminis ya tsaya ga ra'ayin kansa, ya yi kanekane da kome, ya zaci cewa kome ya yi mai kyau ne, amma duk abin da saura suka yi ba kyau. Ko kusa bai kamata ba ya rufe kansa a karamin daki, ko ya nuna bunkasa ko kuma ya nuna shi yallabai ne.

"Jawabi a Taron Majalisar Wakilan Jihar Iyaka ta Shensi-Kansu-Ningsia" (21 ga Nuwamba, 1941), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Dole ne 'yan Kwaminis su natsu ga sauraren ra'ayin waɗanda ba 'yan Jam'iyya ne ba kuma su ba su damar magana. Idan abin da suka faɗa daidai ne, ya kamata mu marabci abin kuma mu koyi halaye masu kyau daga gare su. Idan abin da suka faɗa ba daidai ba ne, ya kamata mu bari su ƙarasa abin da suke nufi, sa'idin nan mu yi hakurin yi musu bayani.

"Jawabi a Taron Majalisar Wakilan Jihar Iyaka ta Shensi-Kansu-Ningsia" (21 ga Nuwamba, 1941), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Matsayin 'yan Kwaminis ga waɗanda suka yi laifi cikin aiki shi ne ya kamata su yi amfani da hanyar shawo kai don su taimaka musu gyarawa kuma su sake farawa, kuma bai kamata su gefantad da su ba sai dai in sun gagara horo.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yaƙin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka.* Littafi na Biyu.

Bai kamata ba 'yan Kwaminis su ƙaskanta ko su raina mutane waɗanda ke baya amma ya kamata su yi abuta da su, su haɗu da su, su shawo kansu kuma su himmanta su wajen ci gaba.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yaƙin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

29. MA'AIKATAN HUKUMA

Domin tabbata cewa da Jam'iyyarmu da ƙasarmu ba za su sake launinsu ba, ba kawai ya kamata a ce muna da gaskantattun hanya da manufar siyasa ba amma ma ya kamata mu yi tarbiyya kuma mu shirya miliyoyi ɗin magadan sha'anin tawayen talakawa.

A ƙarshe, maganar horon magadan sha'anin tawayen talakawa ita ce maganar ko da akwai ko babu mutanen da za su ci gaba da sha'aɲin tawayen Marksanci-Leninanci wanda 'yan tawayen talakawa na zuriyar da suka fara, magana ce ko shugabancin Jam'iyyarmu da na ƙasarmu zai ci gaba a hannun 'yan tawayen talakawa, magana ce ko zuriyarmu za ta ci gaba da tafiya bisa gaskantacciyar hanyar da Marksanci-Leninanci ya tsara, watau magana ce ko ma iya nasara wajen kiyaye aukuwar munafuntar Marksanci-Leninanci irin na Khrushchov a Sin. A takaice dai, magana ce mafi muhimmanci wadda ta shafi rai ko mutuwa ga Jam'iyyarmu da ƙasarmu. Magana ce mafi muhimmanci ga sha'anin tawayen talakawa na shekaru ɗari, dubu, ko dubu goma. Bisa sauyin da ya faru a ƙasar Tarayyar Soviet, annabawan daulantaka suna sa kwaɗayin "juyi a ruwan sanyi" a zuriya ta uku ko ta huɗu ta Jam'iyyar Sin. Dole ne mu wargazad da wannan annabcin daulantaka sosai. Duk ƙungiyoyi ko ina, daga mataki na sama har zuwa na ƙasa, dole ne mu rika sa hankali ga tarbiyya da shirya magadan sha'anin tawaye.

Ina sharuɗan da suka dace wajen zama cancantattun magadan sha'anin tawayen talakawa?

Dole su zama 'yan Marksanci-Leninanci na kirki ba munafukai kamar Khrushchov ba masu lullubi da Marksanci-Leninanci.

Dole su zama 'yan tawayen turu masu bauta wa ɗimbin yawancin mutanen Sin da na duniya da zuciya ɗaya, amma ba su yi kamar Khrushchov ba mai bauta wa moriyar 'yan rukunan tajirai masu gata a cikin ƙasarsa, haka zalika da moriyar daulantaka da ta azzalumai na waje.

Dole su zama gwanayen 'yan siyasar talakawa masu iya haɗa kai da ɗimbin yawancin mutane kuma su yi aiki tare da su. Ba kawai sai da masu ra'ayi ɗaya da su za su haɗa kai ba, amma su iya haɗuwa da waɗanda ra'ayinsu ya sha bamban da nasu har ma da waɗanda suka ƙi su a da kuma an riga an shaida kuskurensu a aikatawarsu. Amma fa ya kamata su mai da hankali musamman ga masu kwaɗayin muƙami da masu yin maƙarƙashiya kamar su Khrushchov kuma su hana waɗannan munafukai kame ragamar shugabancin Jam'iyya da ta ƙasa a ko wane mataki.

Dole su zama abin koyi wajen aikata shirin dimaƙuraɗiyya-tattarawa na Jam'iyya,

dole su naƙalci hanyar shugabanci wadda ta dogara bisa ƙa'idar "a fito daga jama'a kuma a koma ga jama'a" kuma su raya halin aiki na dimaƙuraɗiyya wanda zai iya sa su saurarar ra'ayin jama'a. Bai kamata ba su yi kamar Khrushchov, su lalata dimaƙuraɗiyya-tattarawa ta Jam'iyya, su yi mulkin Fir'auna, su far wa abokanai ba zato ba tsammani ko su nuna rashin adalci kuma su yi aiki kamar Fir'auna.

Dole su zama kamilai kuma masu hankali, su kiyayi nuna kai da kaudi, su zamana suna da halin kushewa kai kuma su yi ƙarfin halin gyara aibobi da kuskure a cikin aikinsu. Bai kamata ko ta wace hanya su ɓoye kuskurensu ba, su ba kansu yabo su tura wa wasu laifuffuka kamar Khrushchov.

A gudanarwar famar jama'a ne magadan sha'anin tawayen talakawa ke ɓullowa, a tsakiyar guguwar tawayen turu ne su ke rayuwa su ke nuna. Ya kamata a jarraba kuma a gane ma'aikatan hukuma, a zaɓi

kuma a hori magada a cikin gudanarwar doguwar famar jama'a.

> Daga "Kan Kwaminisancin Karya na Khrushchov da Darasunan Tarihi Da Ya Ba Duniya" (14 ga Yuli, 1964).

Ya kamata kungiyoyin Jam'iyyarmu su yadu a duk kasar, kuma cikin niyya mu hori ma'aikatan hukuma dubu-dubbai da dararrukan shugabanni mafiya kirki na jama'a. Ya kamata su zamana ma'aikatan hukuma da shugabanni wadanda suka yi zurfi a Marksanci-Leninanci, su zamana masu tsinkaya a fannin siyasa, su gwanance a aiki, su zamana masu halin sadakarwa, su iya daidaita al'amura su da kansu, su tsaye sosai ga ko wace wahala, kuma su zamana masu bauta wa al'umma, ajinsu da Jam'iyya da zuciya daya cikin gaskiya. Tare da dogara kan wadannan ma'aikatan hukuma da shugabanni ne Jam'iyya za ta tabbata

zumunta tsakaninta da mambobinta da jama'a, kuma tare da dogara ga tsayayyen shugabancin da wadannan mutane ke yi wa jama'a ne, Jam'iyya za ta iya cika burinta na nakasa makiya. Ya kamata wadannan ma'aikatan hukuma da shugabanni su bar son kai, jaruntakar mutum daya, son ta da kai, ragwanci, saiɓi da kuma rukunanci na girman kai, ya kamata su zamana jarumai marasa son kai na al'umma da na aji. Wadannan su ne halaye da hanyar aikin da suka kamaci mambobin Jam'iyya da ma'aikatanta da shugabanninta.

> "Mu Yi Fama domin Jawo Miliyoyin Jama'a Su Shiga Hadadden Goshin Famar Al'umma na Kiyewa Japan" (7 ga Mayu, 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Idan an tsai da hanyar siyasa, sai ma'aikatan hukuma su zama masu linzamin abu.

Sabo da haka, ɗawainiyar faɗammu ce mu hori ɗimbin ma'aikatan hukuma sababbi bisa shiri.

> "Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yaƙin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ka'idar da ya kamata Jam'iyyar Kwaminis ta aikata wajen manufar siyasa game da ma'aikatan hukumarta ita ce ko wani ma'aikacin hukuma a tsaye shi ke wajen tafiyar da hanyar Jam'iyya, yana bin biyayyar Jam'iyya, yana cuɗanya da jama'a sosai, yana iya aiki da kansa, yana sha'awar aiki da kuzari kuma maras son kai ne. Wannan shi ne abin da a ke nufi da "naɗa mutane bisa kirkinsu" ke nan.

> "Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yaƙin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Dole a tsaya ga tsari na ma'aikatan hukuma su halarci aikin ƙarfin tarayya na kawo albarka. Ma'aikatan Jam'iyyarmu da na ƙasarmu, ma'aikata ne kamar kowa, ba alloli ne masu zama kan bayan jama'a ba. Ta halartar aikin ƙarfin tarayya na kawo albarka ne, ma'aikatan hukuma ke ɗiƙe zumunci mai faɗi na kullum da sosai da jama'a talakawa. Wannan babbar dabara ce mai muhimmin digi ga tsarin gurguzu, tana taimakon a haye ra'ayin nuna hakimci kuma a hana munafuntar Marksanci-Leninanci da dogamatisanci.

> Daga "Kan Kwaminisancin Karya na Khrushchov da Darasunan Tarihi Da Ya Ba Duniya" (14 ga Yuli, 1964).

Ya kamata mu san yadda za mu gane ma'aikatan hukuma. Bai kamata ba mu ƙayyadi ganewarmu ga gajeren lokaci ko ga wani abu da ya faru a rayuwar wani ma'aikacin hukuma, amma ya kamata mu dubi

dukan rayuwarsa da dukan aikinsa. Wannan ita ce muhimmiyar dabarar gane ma'aikatan hukuma.

> "Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ya kamata mu san yadda za mu yi amfani da ma'aikatan hukuma sosai. A karshe dai, shugabanni suna da muhimman hakki biyu, watau su ba da dabara kuma su yi amfani da ma'aikatan hukuma sosai. Irin wadannan abubuwa kamar yin shiri, daukar shawara, ba da umurni da yin gargadi suna cikin inuwar "a ba da dabara". Domin yin aiki da dukan dabarun, ya kamata mu hada kai da ma'aikatan hukuma kuma mu ba su himmar yin aiki, wannan na cikin inuwar "a yi amfani da ma'aikatan hukuma sosai".

> "Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Dole ne mu san yadda za mu tattali ma'aikatan hukuma sosai. Hanyoyin tattali su ne, na farko, a yi musu ja gaba. Watau a bar su su yi aiki cikin walawa domin su samu bajinta su dauki nauyi, kuma a yi musu gargadi cikin lokaci sosai domin a karkashin shugabancin hanyar siyasar Jam'iyya, su iya nuna basirarsu ta kagowa. Na biyu, a ta da matsayinsu. Watau a koyad da su ta hanyar ba su zarafin nazari domin su ta da matsayin sanin-ka da kuma iyawar aikinsu. Na uku, a duba aikinsu, a taimake su tattara fasaharsu, su rika ci gaba da nasarorinsu da gyara kuskurensu. A ba da aiki ba tare da dudduba yadda a ke yinsa ba kuma a kasa kula sai lokacin da aka yi babban kuskure, wannan ba hanya ce ta tattalin ma'aikatan hukuma ba. Na hudu, galibi dai, ya kamata a yi amfani da hanyar shawo kai ga ma'aikatan hukuma wadanda suka yi kuskure, kuma a taimake su gyara kuskurensu. Sai dai ga wadanda suka yi babban kuskure kuma suka

ki jin gargadi za a yi amfani da hanyar fama. A nan hakuri wajibi ne. Ba daidai ba ne a zargi mutane "'yan zarafintaka" a sama-sama ko a fara "yin fama" ta kinsu a sama-sama. Na biyar, a taimake su haye wahalolinsu. Lokacin da ma'aikatan hukuma su ke cikin wahaloli sabo da rashin lafiya, ko rashin isassun hanyoyin rayuwa, ko wahalolin iyali da sauransu, dole mu yi iyakacin kokari mu ba su taimako. Wannan shi ne yadda a ke kula da ma'aikatan hukuma.

> "Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Biyu.

Sai dai ta shiga famar jama'a amma ba ta wariya daga gare ta ba ne, rukunin shugabanci mai hada kai da cuduwa sosai da jama'a ke kafuwa da hankali-hankali. Galibi dai cikin gudanarwar wata babbar fama, bai kamata ba kuma ba ya yiwuwa a kasa

yin sauyi cikin mutanen rukunin shugabanci ko a farkon fama ko a tsakiya ko a karshenta. Mutane masu himma wadanda suka bullo a lokacin da a ke fama dole ne a rika ciyar da su gaba su kama gurbin wadancan mambobin rukunin shugabanci na da wadanda suka nuna kasawa bayan an kwatanta su ko wadanda suka lalace.

> "Wasu Maganganu game da Dabarun Shugabanci" (1 ga Yuni, 1943), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Uku.

Idan Jam'iyyarmu ba ta da dimbin sababbin ma'aikatan hukuma da ke aiki cikin hada kai da gama gwiwa da tsofaffin ma'aikatan hukuma, sha'animmu zai kafe. Don haka duk tsofaffin ma'aikatan hukuma ya kamata su yi maraba da sababbi da hannu biyu-biyu kuma su nuna musu cikakkiyar kula. Gaskiya dai, sababbin ma'aikatan hukuma suna da aibobinsu. Ba su dade a tawaye ba, sun rasa fasaha, wasu kuma

lalle ne suna tare da bulbuɗin mummunan tunanin tsohon zama, watau ringin tunanin nuna son kai na 'yan ƙananan tajirai. Amma aibobin nan abubuwa ne waɗanda za a iya kau da su a kwana a tashi cikin tarbiyya da rayuwa a tawaye. Kyakkyawan hali na sababbin ma'aikatan hukuma, kamar yadda Stalin ya faɗa, shi ne suna iya gane sababbin abubuwa da sauri don haka suna da babbar sha'awa da himma watau irin waɗannan halaye ne wasu tsofaffin ma'aikatan hukuma suka rasa. Ma'aikatan hukuma sababbi da tsofaffi, ya kamata su girmama juna, su yi koyi da juna kuma su haye aibobinsu ta hanyar koyon kyawawan halayen juna domin su haɗa kai a cikin sha'anin tarayya kuma su kiyaye kansu daga nufin rukunanci.

"Gyara Haliyar Aiki ta Jam'iyya" (1 ga Fabrairu, 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ya kamata mu kula da ma'aikatan Jam'iyya har da ma'aikatan hukuma waɗanda ba 'yan Jam'iyya ba ne. Akwai ingantattun mutane da yawa a waje da Jam'iyya waɗanda bai kamata mu ƙyale su ba. Hakki ne ga ko wane ɗan Kwaminis ya rabu da halin kaɗaici da fariya, kuma ya iya aiki da ma'aikatan hukuma waɗanda ba 'yan Jam'iyya ba ne, ya taimake su cikin gaskiya, ya nuna musu kyakkyawan hali na abuta kuma ya ta da himmarsu cikin babban sha'anin kare harin Japan da gina ƙasa.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yaƙin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

30. SAMARI

Duniya taku ce kuma tamu ce, amma a hakika taku ce. Ku samari kuna cike da himma da bajintaka, kuna cikin ƙuruciya kamar rana a ƙarfe takwas ko tara na safe. Ana sa ido a kanku.

.....

Duniya taku ce. Goben Sin na hannunku.

> Ganawa Da Dalibai Sinnawa da 'yan Kos a Mosko (17 ga Nuwamba, 1957).

Ya kamata a fahimtad da duk samari cewa har yanzu ƙasarmu na cikin talauci ƙwarai kuma ba abu ne mai yiwuwa a ce za a iya sauya wannan hali sosai cikin ɗan

gajeren lokaci ba, sai kawai tare da haɗin kai da ƙoƙarin duk samari da jama'a ne waɗanda su ke aiki da hannuwansu, za.a iya mai da Sin ta zama ƙasa mai arziki kuma mai ƙarfi a cikin 'yan shekaru gommai. Kafuwar tsarin gurguzu ta bude mana hanyar zuwa ga cika burin zaman gobe, amma mai da wannan buri cikin hakika na bukatar aiki mai wuya.

> "Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Domin rashin fasahar siyasa da ta halin zaman al'umma, samari da yawa ba su iya bambanta tsohuwar Sin da sabuwar. Suna jin wuyar fahimtar maɗaciyar fama sosai wadda jama'armu suka yi kafin su suntad da kansu daga danniyar daulantaka da azzaluman Kuomintang, ko su fahimci irin dogon lokaci na mawuyacin aikin da ake bukata kafin a kafa kyakkyawan halin zaman gurguzu. Sabo da haka, ya kamata

a rika yin rayayyar tarbiyyar siyasa ta gaske cikin jama'a, kuma a rika gaya musu gaskiya game da wahalolin da ke ɓullowa, kuma a yi shawara tare da su a kan yadda za a haye wahalolin.

"Game da Hanyar Daidaita Saɓani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Samari su ne rundunar karfi mafi kwazo, mafi kuzari cikin halin zamammu. Su ne mafiya ɗoki wajen nazari kuma su ne mafiya karancin ra'ayin gargajiya, musamman ma a zamanin gurguzu. Muna dai fata duk kungiyoyin Jam'iyya a ko wane wuri tare da Kungiyar Samari za su nitsu wajen binciken yadda za a ta da karfin samarimmu musamman. Bai kamata ba kungiyoyin Jam'iyya su ɗauke su kamar sauran mutane kuma su yi banza da musamman halayensu. Amma ya kamata samari su yi koyi daga wajen tsofaffi da dattawa, kuma

su yi matukar kokari su shiga wadansu aikace-aikace masu amfani tare da yardarsu.

Gabatarwa ga "Rundunar Samari Barade ta Kungiyar Hadin Kan Manoma Mai Lamba 9 a Garin Hsinping na Gundumar Chungshan" (1955).

Ta yaya za a iya sanin ko wani saurayi ɗan tawaye ne ko ba ɗan tawaye ne ba? Yaya za a bambanta? Shaida daya tak, watau shi saurayin ko yana son cuɗuwa da ɗimbin jama'a ma'aikata da manoma kuma yana aikatawa. Idan yana so kuma haka ya ke aikatawa, shi ɗan tawaye ne, amma im ba haka ba, shi ba ɗan tawaye ne ba, ko ɗan kin tawaye ne. Idan a yau ya cuɗu da jama'a ma'aikata da manoma, to, shi ɗan tawaye ne a yau, amma in gobe ya daina yin haka ko ya juya ya danne jama'a, sai ya zama ba ɗan tawaye ba ko kuma ma ki tawaye ne.

"Hanyar Da Za A Sa Harkar Samari Bi" (4 ga Mayu, 1939), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Galibi dai 'yan ilmi kafin su sa kansu kai da kafa cikin famar tawayen jama'a kuma su kudura niyya ga bauta wa bukatun jama'a ko su cudu da su, su kan nuna tunanin zuci da son kai, ra'ayinsu ya kan zama maras auki kuma su kan yi shakka wajen aikatawa. Sabo da haka, dimbin 'yan ilmi 'yan tawaye Sinnawa ko da ya ke suna aikin maduganci ko suna aiki kamar kadarkon hada mutane, amma ba duka ne za su iya aikin tawaye har karshe ba. A lokacin matsatsi na tawaye, wadansu a cikinsu su kan fita daga sahun tawaye, su zama masu saiɓi, har ma 'yan kadan su kan zama makiyan tawaye. Sai ta cikin doguwar famar da jama'a ke yi ne 'yan ilmi za su iya haye wadannan laifuffuka.

"Tawayen Sin da Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (Disamba 1939), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Ban da ci gaba da ba da taimako ga muhimmiyar dawainiyar da Jam'iyya ke yi, Kungiyar Samari kuma ya kamata ta yi wasu ayyuka cikin 'yanci da suka dace da halayen samari. Ya kamata Sabuwar Sin ta yi tattalin samarinta, ta rika kula da tashin zuriyar gobe. Ya kamata samari su yi nazari, su yi aiki, amma suna cikin lokacin girma ne. Sabo da haka, ya kamata a ba da cikakkiyar kula ga aikinsu da nazarinsu har ma ga wasanninsu, guje-gujensu na motsa jiki da shakatawarsu.

Gargadi a Wata Saduwa da Rukunin Shugabancin Taron Wakilan Kasa na Biyu na Kungiyar Samari (30 ga Yuni, 1953).

31. MATA

A Sin namiji galibi yana shan daular tsarin hukuma iri uku (hukumar siyasa, hukumar kabila da hukumar addini, watau bayani na mai shirya littafin ne). ... Game da mata kuwa, ban da tsarin hukuman nan iri uku, kuma suna hannun maza (watau hukumar miji). Wadannan hukumomi guda hudu watau ta siyasa, ta kabila, ta addini da ta miji, suna wakiltar sukutum din tsari da tunani na mulkin maigida na gargajiya (feudal-patriarchal), su ne manyan igiyoyi hudu da su ke tanke jama'ar Sin musamman manoma. Yadda manoma suka hamburad da hukumar siyasa ta ma'abutan kasa a kauye an riga an siffanta shi tun farko. Hukumar siyasa ta ma'abutan kasa ita ce

jigo na dukan sauran tsari na hukuma. Bayan an hamburad da hukumar siyasar ma'abutan kasa sai hukumar kabila, ta addini da ta miji gaba daya suka fara kaduwa. ... Game da hukumar miji, tun farko wannan raunanannne ne a cikin matalautan manoma sabo da, bisa rashin arziki, matan matalautan manoma dole ne su yi aikin karfi fiye da matan wadatattun azuzuwa, don haka sun fi samun hujjar magana da ta tsai da magana a al'amarin iyali. Domin ci gaba da rushewar tsimin kauye a 'yan shekarun nan, digin ikon maza kan mata an riga an lalata shi. Tare da bullowar harkar manoma a kwanakin nan, mata a wurare da dama sun fara kafa kungiyoyin hadin kan mata a kauye. Lokaci ya zo musu don su ta da kai, kuma hukumar miji na kara girgizuwa ko wace rana. A takaice dai, dukan tunani da tsari na mulkin

maigida na gargajiya na girgizuwa tare da karuwar ikon karfin manoma.

"Rahoto kan Binciken Harkar Manoma a Lardin Hunan" (Maris 1927), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Ku hada kanku, ku halarci aikin kawo amfani da sha'anin siyasa domin ku kyautata matsayin tsimi da siyasa na mata.

Rubutun Wasu Maganganu don Mujalla Mai Suna *Matan Sabuwar Sin*, An Buga a cikin Fitowar Farko ta Mujallar, 20 ga Yuli, 1949.

A tsare moriyar samari, mata da yara, a yi wa dalibai 'yan gudun hijira gudummawa, a taimaki samari da mata su shirya kansu domin su halarci cikin matsayi daya duk ayyuka masu amfani wajen Yakin Kare Harin Japan da ci gaban zaman al'umma, a tabbatar da 'yancin aure da daraja guda

tsakanin maza da mata, kuma a yi wa samari da yara horo mai amfani. . . .

"Kan Gwamnatin Gama Gwiwa" (24 ga Afril, 1945), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Uku.

Dawainiyarmu mafi muhimmanci game da aikin kawo albarkar noma ita ce mu shirya karfin kawo albarka a cikin tsari, kuma mu himmanta mata su halarci aikin kawo amfani.

"Tsarin Manufar Siyasarmu wajen Tsimi da Tanadi" (23 ga Janairu, 1934), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Domin gina kasaitaccen zaman gurguzu, ta da dimbin mata su shiga aikin kawo albarka na da babbar ma'ana. A cikin aikin kawo albarka dole samun maza da mata ya zama daya muddin dai suna aiki iri daya. Sai ta gudanarwar sauyin gurguzu na dukan halin zama, za a samu daidaicin gaske tsakanin maza da mata.

Gabatarwa ga "Mata Sun Tafi Fagen Aiki" (1955).

Bayan an kare gama gwiwar manoma, kungiyoyin gama gwiwa da yawa sun gane suna cikin rashin isasshen karfin aiki, sabo da haka ya zama wajibi a ta da dimbin mata wadanda a da ba su aikin gona su shiga fagen aiki. ... Matan Sin kamar babban rumbun karfin aiki su ke. Dole ne a fidda abin cikin rumbun nan wajen famar gina babbar kasar gurguzu.

Gabatarwa ga "An Warware Matsalar Karancin Leburori ta Hanyar Tada Mata Tsaye Su Shiga Aikin Kawo Albarka" (1955).

Ya kamata ko wace mace wadda ke iya aiki a ba ta damar shiga fagen aiki bisa ka'idar nan ta irin aikinka irin samunka. Kuma abu ne wanda ya kamata a tabbatad da shi cikin dan gajeren lokaci.

Gabatarwa ga "Shirin Kungiyar Tarayyar Dimakuradiyya ta Mata ta Gundumar Hsingtai domin Karfafa Aikin Mata a cikin Harkar Gama Gwiwar Manoma" (1955).

32. AL'ADA DA FASAHA

A duniyar yau, duk wata al'ada da duk wata wallafa da fasaha na wani kudurarren aji ne kuma dukansu na wata kudurarriyar hanyar siyasa ne. A cikin gaskiya dai, ba wata fasaha domin fasaha kawai, ko wata fasaha wadda ta fi karfin aji, ko fasahar da ke kunnen doki da siyasa ko wata fasaha da ba ta jingina ga siyasa ba. Da wallafa da fasaha na talakawa suna sashi daya daga sha'anin sukutum din tawayen talakawa, kamar yadda Lenin ya fada, su ne "hakora da kusoshi" na sukutum din na'urar tawaye.

"Jawabi a Taron Yenan kan Wallafa da Fasaha" (Mayu 1942), *Zababbun Ayyuka*, Littafi na Uku.

Al'ada ta tawaye makami ne mai karfi na tawaye ga dimbin jama'a. Kafin a yi tawaye, ta kan shirya jama'a ta fannin tunani, kuma a yayin tawaye, ta kan zama muhimmin fage wanda shi ke wajibi ne ga dukan fagen tawaye.

"Kan Sabuwar Dimakuradiyya" (Janairu 1940), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Wallafarmu da fasaharmu gaba daya bauta wa dimbin jama'a su ke, da farko dai domin ma'aikata, manoma da sojoji ne. Sabo da ma'aikata, manoma da sojoji ne aka kago su, kuma su ne su ke amfani da su.

"Jawabi a Taron Yenan kan Wallafa da Fasaha" (Mayu 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Dole marubutammu da 'yan fasaharmu su cika dawainiyar nan, dole su sake matsayinsu, dole kuma da kadan-kadan su koma

ta wajen ma'aikata, manoma da sojoji, su koma ma talakawa, ta hanyar shiga cikinsu da kuma shiga cikin tsakiyar famar aikatawa tare da nazarin Marksanci da halin zaman al'umma. Ta haka ne kawai, za mu iya samun wallafa da fasaha masu bauta wa jama'a ma'aikata, manoma da sojoji da gaske, watau wallafa da fasaha na talakawan gaske.

"Jawabi a Taron Yenan kan Wallafa da Fasaha" (Mayu 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ya kamata a sa wallafa da fasaha su zama gaba sosai ta sukutum din na'urar tawayen turu, su zama kakkarfan makami wajen hada kan jama'a da tarbiyyarsu da kuma wajen dukan makiya da halakad da su, kuma su taimaki jama'a wajen fama da makiya da zuciya guda da niyya guda.

"Jawabi a Taron Yenan kan Wallafa da Fasaha" (Mayu 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Kushewa ta wallafa da fasaha na da shaidu biyu, ɗaya ta siyasa, ɗaya kuma ta fasaha. ...

Ga shaida ta siyasa ga kuma ta fasaha, ina dangantaka tsakanin waɗannan shaidu biyu? Siyasa ba daidai ta ke da fasaha ba, haka kuma ra'ayi game da duniya da dabarun ƙagowa da kushewa na fasaha ba za a ba su daraja ɗaya ba. Ba kawai muna musanta cewa da akwai shaidar iska ta siyasa maras sauyawa sam ba (abstract, absolutely unchangeable political criterion), amma har ma muna musanta cewa da akwai shaidar iska ta fasaha maras sauyawa sam (abstract, absolutely unchangeable artistic criterion). Ko wane aji a cikin ko wane halin zama na aji yana da nasa shaidu na siyasa da fasaha. Amma fa ko wane aji a cikin ko wane halin zama na aji, kullum yana sa shaidarsa ta siyasa a matsayi na farko, ta fasaha kuwa a na biyu. ... Mu kuwa, abin da mu ke so shi ne haɗin kan siyasa da fasaha, haɗin kan ma'ana da siffa da kuma haɗin kan ma'anar

siyasar tawaye da siffar fasaha mafi kyau. Ayyukan fasaha waɗanda darajar fasaha ta yi musu gaira, kome ci gabansu a fannin siyasa, ba su da ƙarfi. Sabo da haka muna ƙin ayyukan fasaha masu gabatad da ra'ayin kuskure na siyasa, kuma muna ƙin nufi ga "halin hauragiya da sanarwa" (slogans) wanda ra'ayin siyasa daidai ne amma wajen fasaha ba shi da ƙarfi. Game da wallafa da fasaha, ya kamata mu sanya fama a fannoni biyu.

"Jawabi a Taron Yenan kan Wallafa da Fasaha" (Mayu 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

A bar "furanni ɗari su tohu kuma makarantun tunani ɗari su shiga takara", manufar siyasa ce mai ingiza yalwatar fasaha da ci gaban kimiyya da kuma mai ingiza tohuwar al'adun gurguzu a ƙasarmu. A fannin fasaha kamannu dabam daban da halaye iri iri suna iya yalwata cikin 'yanci, a fannin kimiyya makarantun tunani dabam daban

na iya muhawara cikin 'yanci. A ganimmu zai kawo ßarna ga yalwatar fasaha da kimiyya idan an yi amfani da ƙarfin hukuma wajen tilasta wata haliyar fasaha ko wata makarantar tunani ko kuma hana wata haliyar fasaha ko wata makarantar tunani. Maganar gaskiya da ƙarya a fasaha da kimiyya, ya kamata a daidaita ta ta hanyar taune-taune cikin 'yanci a da'irorin fasaha da kimiyya da kuma ta aikatawa a waɗannan fannoni. Amma bai kamata a daidaita ta sauwaƙaƙkiyar hanya ba.

"Game da Hanyar Daidaita Saßani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Rundunar soja maras al'ada, jahilar runduna ce, kuma nasara kan maƙiya ba ta samuwa ga jahilar runduna.

"Haɗaɗɗen Goshin Fama a cikin Aikin Al'adu" (30 ga Oktoba, 1944), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

33. NAZARI

Muna fuskantar aiki mai ɗaci wajen sauya ƙasar Sin wadda ta ke baya kuma ta noma ce ta zama ƙasa mai masana'antu kuma mai ci gaba, kuma fasaharmu ba ta isa ba ko kusa. Don haka dole ne mu gwanance a koyo.

"Jawabin Buɗe Taro na Takwas na Wakilan Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (15 ga Satumba, 1956).

Kullum halaye cikin sakewa su ke, kuma domin ra'ayimmu ya dace da sababbin halaye, tilas ne mu yi koyo. Ko ga waɗanda suka fi nakaltar Marksanci kuma a kwatance tsayayyu ne a matsayinsu na talakawa, dole

ne su ci gaba da koyo, su yarda da sabon abu kuma su yi nazarin sababbin al'amura.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

Za mu iya koyon duk abin da ba mu sani ba a da. Ba kawai mun gwanance ba wajen rugurguza tsohuwar duniya har ma mun gwanance wajen gina sabuwa.

"Rahoto ga Cikakken Zama na Biyu na Taro na Bakwai na Kwamitin Tsakiya na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin" (5 ga Maris, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Akwai halaye biyu na koyo. Daya shi ne halin dogamatisanci na shigo da kome ko ya dace ko bai dace da halin kasarmu ba. Wannan ba halin kirki ne ba. Dayan kuma shi ne mu yi aiki da kwakwalwarmu, kuma mu koyi abubuwan da suka dace da halin matsalar kasarmu, watau mu yarda da ko

wace fasahar da za ta iya amfanarmu. Wannan shi ne halin da ya kamata mu zaba.

"Game da Hanyar Daidaita Sabani Sosai tsakanin Jama'a" (27 ga Fabrairu, 1957).

Tsarin sanin-ka na Marks, Engels, Lenin da Stalin abu ne wanda ake iya aiki da shi a ko ina a duniya. Bai kamata ba a dauke shi kamar tsafaffen abu (dogma) sai dai kamar ja gora wajen aikatawa. Bai kamata a koyi kalmomi da ayoyin Marksanci-Leninanci kawai ba sai dai a yi nazarin Marksanci-Leninanci kamar kimiyyar tawaye. Bai kamata kawai a fahimci galiban ka'idodin da Marks, Engels, Lenin da Stalin suka samu ba daga zurfin nazarinsu na zaman gaske da fasahar tawaye, amma har ma ya kamata a nazarci matsayi da dabarar da suka dauka wajen bincika da daidaita al'amura.

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Idan muna da tsarin sanin-ka na gaske amma sai surutu kawai mu ke game da shi, mu ajiye shi ba tare da aikata shi ba, to, wannan tsarin sanin-ka kome kyaunsa ba shi da ma'ana.

"Kan Aikatawa" (Yuli 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Ya kamata a nakalci tsarin sanin-ka na Marksanci sosai kuma a aikata shi, a nakalce shi domin aikata shi kawai. Idan ka iya yin amfani da ra'ayin Marksanci-Leninanci wajen bayyana al'amuran gaske daya ko biyu, za ka cancanci yabo kuma a iya cewa ka sami 'yar nasara. Muddin kana kara bayyana al'amura, muddin bayaninka na kara fadi da zurfi, haka nasarorinka za su kara yawa.

"Gyara Haliyar Aiki ta Jam'iyya" (1 ga Fabrairu, 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Ta yaya za a cuda tsarin sanin-ka na Marksanci-Leninanci da aikin tawayen kasar Sin? A yi amfani da wata magana ta kullum, watau "harba kibiyarka kan bara". Yadda kibiya ta ke ga bara, haka Marksanci-Leninanci ya ke ga tawayen Sin. Amma wadansu abokanammu na "harba kibiyarsu ba ga bara ba", harbi su ke a iska kawai, kuma irin wadannan mutane ba wuya su jawo wa tawaye asara.

"Gyara Haliyar Aiki ta Jam'iyya" (1 ga Fabrairu, 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Masu fasaha a aiki, ya kamata su mai da hankali wajen nazarin tsarin sanin-ka kuma su yi karatu cikin tsanaki, daga nan ne kawai za su iya tsara fasaharsu, su takaita fasaharsu kuma su tayar da ita zuwa ga matsayin tsarin sanin-ka, daga nan ne kawai za su iya kiyaye daukar guntuwar fasaharsu

kamar gaskiya ce ta ko ina, kuma su guji yin kuskuren fasahantaka.

"Gyara Haliyar Aiki ta Jam'iyya" (1 ga Fabrairu, 1942), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Uku.

Karatu shi ne koyo, amma aikata abin da aka koya koyo ne shi ma kuma koyo ne mafi muhimmanci. Babbar dabararmu ita ce mu koyi yaki cikin yaki. Mutum wanda ba shi da damar shiga makaranta shi ma ya iya koyon yaki watau ya iya koyo daga yaki. Yakin tawaye sha'ani ne na jama'a, galibi dai ba magana ce ta fara koyo kana a yi ba, amma magana ce ta fara yi kana a koya, domin yi shi kansa koyo ne.

"Matsalolin Sihirin Shiri a Yakin Tawayen Sin" (Disamba 1936), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Da akwai rata tsakanin farar hula da soja, amma ba Babbar Ganuwa ce tsakaninsu ba, kuma ita wannan rata ana iya cim mata

da sauri. Hanyar cim mata ita ce a shiga tawaye da yaki. Lokacin da muka ce ba abu mai sauki ba ne a koya kuma a aikata, abin da mu ke nufi a nan shi ne, ba abu mai sauki ba ne a koya sosai kuma a aikata tare da gwaninta. Lokacin da muka ce farar hula nan da nan na iya zama soja, nufi mu ke cewa ba shi da wuya a shige dokin kofa. Im mun hada maganganun nan biyu ma iya siffanta su da karin maganar Sinnawa, "Ba wani abu mai wuya a duniya ga mai son mai da hankalinsa ga abin." Shige kofa ba ya da wuya kuma inganta kai shi ma mai yiwuwa ne idan dai za a mai da hankali kuma za a gwanance wajen koyo.

"Matsalolin Sihirin Shiri a Yakin Tawayen Sin" (Disamba 1936), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Ya kamata mu koyi yadda za mu yi aikin tsimi daga duk wadanda su ke da sanin (ko wadanne ne su). Ya kamata mu mai da

su malamammu, mu yi koyi daga gare su cikin girmamawa da gaskiya. Kada mu nuna mun sani alhali kuwa ba mu sani ba.

"Kan Mulkin Shibtar Dimakuradiyyar Jama'a" (30 ga Yuni, 1949), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Hudu.

Sani magana ce ta kimiyya, kuma ba ta yarda da rashin gaskiya ko girman kai ko kadan. Tabbat abin da ta ke so shi ne akasin haka watau gaskiya da kamilanci.

"Kan Aikatawa" (Yuli 1937), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Farko.

Girman kai shi ne makiyin nazari. Ba za mu iya koyon kome da gaske ba sai dai mun raba kammu da girman kai. Gare mu halin da ya kamata mu dauka shi ne "ba a nuna koshi wajen koyo", kuma ga wasu "kada a gaji wajen koyarwa".

"Aikin Jam'iyyar Kwaminis ta Sin cikin Yakin Al'umma" (Oktoba 1938), *Zababbun Ayyuka,* Littafi na Biyu.

Wadansu mutane sun karanta wadansu littattafan Marksanci, kuma suna daukar kansu masana, amma abin da suka karanta bai shige su ba, saiwa ba ta kafu a kwakwalwarsu ba, don haka ba su san yadda za su yi amfani da shi ba kuma tunaninsu game da aji ya zaune bai sake ba har yanzu . Wadansu ma suna girman kai kwarai kuma bayan da suka koyi 'yan ayoyi na littattafai, sai suka shiga bunkasa da faharin gaske. Amma da hadari ya taso sai suka dauki matsayin da ya bambanta kwarai da na ma'aikata da galibin manoma. Suna tangadi alhali kuwa ma'aikata da galibin manoma suna tsaye sosai, suna shakka alhali kuwa ma'aikata da galibin manoma sun fito fili.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

Wajen nakaltar Marksanci ba kawai ya kamata a koye shi daga littattafai ba, amma musamman ma ta famar aji, aikatawa da

cuɗanya da jama'a ma'aikata da manoma ne za a iya koyonsa sosai. Idan, bayan karanta littattafan Marksanci, 'yan ilmimmu sun fahimci waɗansu abubuwa ta cuɗanya da jama'a ma'aikata da manoma kuma ta aikatawarsu, to, mu duk bakimmu zai zama ɗaya, ba kawai baki ɗaya kan kishin ƙasa da tsarin gurguzu ba, amma har ma mai yiwuwa ne bakimmu zai zama ɗaya kan ra'ayin kwaminisanci game da duniya. In dai haka ya faru, ba shakka dukammu za mu yi aiki mafi kyau.

"Jawabi a Taron Kasa na Jam'iyyar Kwaminis ta Sin kan Aikin Furofaganda" (12 ga Maris, 1957).

毛 主 席 语 录

*

外文出版社出版（北京）

1972年出版

编号：（豪）1050—626

00077

1-Ha-734Pc